(¯`*•.¸,¤°´✿.｡.:*ℙℝ𝕆𝔽𝕀ℂ𝕀𝔼ℕ𝕋 𝕎ℝ𝕀𝕋𝔼ℝ𝕊*.:｡.✿`°¤,¸.•*´¯)

ᴛʜᴇ ᴀʙɪʟɪᴛʏ ᴛᴏ ɢᴜɪᴅᴇ ɪs ᴛʜᴇ ᴍᴏsᴛ ɪᴍᴘᴏʀᴛᴀɴᴛ ǫᴜᴀʟɪᴛʏ ᴀ ᴡʀɪᴛᴇʀ ᴄᴀɴ ʜᴀᴠᴇ, ᴡᴇ *_ᴘʀᴏғɪᴄɪᴇɴᴛ ᴡʀɪᴛᴇʀ's ᴀssᴏᴄɪᴀᴛɪᴏɴ_* ᴡɪʟʟ sʜᴀʀᴇ ᴛʜᴇsᴇ ǫᴜᴀʟɪᴛɪᴇs.

INSTAGRAM: https://www.instagram.com/proficient_writers/

FACEBOOK: https://mobile.facebook.com/groups/2455147078097572/

TWITTER: https://twitter.com/pro__writers?s=09

🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
_*BARIKI*_
👨‍✈️ _Auren soja_👨‍✈️
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

_written by fenerh_
Maman Ammar

*Dedicated to*
Fiddousi mainasara

*Allahamdulilahi Ala kulli halem ina godiya ga Allah mai kowa mai komai da ya bani ikon dawowa a cikin sabon labari na wato BARIKI Auren soja duk kan yabo da godiya su tabbata ga Allah madaukakin sarki wanda ya bani ikon rubuta wannan labari Alkhairin dake cikin shi Allah yasa Alumma su Amfana dashi kuskuren dake ciki Allah ka gafarta min Ameen*

*KADUNA*

N.D.A BARRACK convoy ne na sojoji a Jere na hilux sai wata jeep katuwa guda daya a tsakiyar su,

Katon gate d'in suka shiga na w'anda gaba daya sojojin dake wurin suka kame Alamar girmama wa ga wanda ke cikin jeep din mai ruwan kalar sojoji,

Jiniya kawai ke tashi Alamar koma waye a ciki babba ne  a Aikin,  jerin  manyan gidajen suka nufa w'anda daga gani na manyan sojoji ne dake cikin barikin wanda sune farkon shigowa,

Gidan da yafi kowanne girma suka tsayar da motocin, kuratan sojojin suka fito dauke da bindigogin su tareda kamewa domin jiran Fitowar ogan nasu,

Gaban motar aka bude gefen mai zaman banza wani soja ya fito rike da brief case da kuma manyan wayoyi  har ma da jakar laptop duka a hannun shi,

Shi ya bude kofar bayan tare da sarawa da hannun shi daya Alamar girma mawa, w'anda ni a zatona  shine ogan saidai ganin wanda yasako  kafar shi a waje ai tuni na yi saurin boyewa bayan manyan itacen fulawoyin dake harabar gidan,

Wani kyakkyawa kuma kakkarfan matashi ne  fari tas dashi ya fito daga bayan motar sanye cikin kakin green na soja,

Wanda da Alama da wuya ya kai shekara Arba'in a duniya,  ga kakin ya mugun  fitoda kwarjinin shi har ma da kara bayyanar da kyanshi a zahiri,

Cikin takun shi mai cike da  kasaita da kuzari irin nasu na sojoji jarumai, ya fara takawa domin shiga cikin gidan nashi,

Nayi matukar jin mamakin ganin wannan karamin matashin ana bashi girma duk inda ya wuce,

General Muhammad Abdullah kenan  G.O.C I DIV Nigerian Army Kaduna

Mutum mai matukar kwarjini da cikar haiba kana ganin shi kasan yana gina jikin shi ta hanyar training da kuma Abinci mai lafiya,

Yakai namiji ta ko ina domin samun kyakkyawan namiji sosai wanda ko wacce mace zataso ta mallaki irin shi,

Kofar gidan nashi ma sojoji ne masu tsaron lafiyar shi, ciki suka shiga shida PA dinshi wanda daga gani Akwai y'ar da mai karfi a tsakanin su da kuma Aminci,

Juyowa yayi cike da bada umarni ya kalle shi "Ahmed take care of them am going to take a bath and rest u can go to your house and rest too,

" tank you sir ya fada tareda mikamai kayan shi ya juya domin isa nashi gidan,

Motar ogan nasu ya bude ya  Ciro bandir din kudi ya mika wa sojojin da suka rako ogan,

Sunyi matukar farin ciki shiyasa suke matukar kaunar megidan nasu domin Akwai kyauta kusan kullum sai ya basu kudi su raba,

Kafin su wuce,
Shima PA din da aka kira da Ahmed ya wuce gidan shi wanda yake gaba kadan da gidan ogan nashi wanda kana gani kasan boys quarters ne duk da suma ba laifi sun tsaru Amma ba kamar gidajen manyan ba,

Wata kyakkyawar  mace ce ta fito da gudu tareda dan karamin yaronta ta tareshi  da murna fal fuskar ta,

Da sauri ya riketa da hannu daya shima fuskar shi cike da fara a dajin dad'in ganin farin ciki a fuskar Matar tashi,

"Madam dina ya Akayi kike irin wannan gudu haka kin manta da Ajiya ta ne kikeso kimun Asara?

Kankame shi tayi gam tareda fara hawaye w'anda kana gani kasan na farin ciki ne. Da kuma jin dadi,

Dagowa tayi tareda Jan hannun shi suka shiga cikin falon su tana cewa " Dadyn Auwal ka tayani murna yau munyi waya da baba harda Mama yau da kanshi zai kawomin Yasmin Ahmed baba ya daina fushi dani,

Ta karasa tana fashe wa da kuka, kan kujerun dake falon ya jata tareda rungume su gam ita da yaron shi yana mai lallashin ta daga gani kasan Akwai wata akasa da har yakesa shi jin tausayin Matar tashi,

"Am sory Maryam nasan nine sanadin komai Amma ki daina damun kanki bazan taba juya miki bayaba kuma gashi kinga su baba sun hakura har zai kawo mana uwar rigima da kanshi,

To kija mata kunne karta zo tana leka min gidan oga don nasan tasa mai ido, ya furta cike da dariya domin kawar mata da damuwar ta,

Dariya tasa itama tareda goge fuskar ta " ai Yasmin Akwai tsiwa ita wai y'anda mata ke shiga da fitane yasa ta tsane shi kuma ko ganin shi bata taba yiba Amma ta mugun sashi gaba da Zagi,

"Hmm pray for him ni kaina ina son oga yayi Aure ko zai rage kwaso mata gidan shi, duk da nasan wasu suke kawo Kansu Amma inaso Allah ya bashi ikon daina wa,

Ameen tace tareda zamewa ta fara kwance mai boot din kafar shi ya rungume yaron shi dakyau a kirjin shi,

" mama tace kar inyaye Auwal inbari har inhaihu tunda bai kaiba, "haka nafada miki tun farko ai kika kiji yanzu tunda mama ta fada zakiji ai,

Dariya tayi tareda mikewa rikeda takalmin domin fita dasu susha iska, bin bayan ta yayi da kallo yana maijin son Matar tashi har cikin b'argon shi,

Muhammad na shiga falon shi yaci karo da takalmin mace, ya kwalawa kukun shi kira tareda ajiye kayan dake hannun shi akan kujerar dake lafiyayyan falon nashi da ya mugun kaya tuwa da kayan Alatu,

Da gudu ya fito yana " yes sir "Emanuel who came? " oga na da madam way day give me money come,

Wani irin mugun kallo ya watsa mai tareda cewa "you are very stupid didn't I warn you ?

" sory sir ya fada yana kamewa kafin yace wani Abu  yaji tace "hy M.A  ta fada cikeda yanga da kara'i raya  gaba daya surar jikinta a bayyane yake don kusan rabin kirjinta da sukayi ruku'u a bayyane suke,

Matsowa tayi tareda rungume shitsam wanda yayi sanadiyyar watsawa Emanuel mugun kallon da ya kwasa a guje yayi kitchen din gidan,

Saurin janyeta  yayi tareda daure fuskar shida Sam dama ba Alamar fara'a atare da ita,

" why the you come? Marai raicewa tayi tareda cewa "come on baby I miss you so much that's is why I came,

Kafin ya bude baki yayi magana wata budurwa  ta fito daga cikin dakin baccin shi sanye da T-shirt dinshi na Como flag  rigar ko cinyar ta bata rufe ba domin idan tayi  kyakkyawan motsi za a iya ganin pant dinta,

Wani irin kallo ya bita dashi tareda kwalawa Emanuel kira cike da bakin ciki,

Da gudu ya fito rike da cooking spoon yana sarawa " yes sir, wani irin disgusting look yake aika mai kafin ya ce,

"Are you stupid,? " no sir Am sory "na she tell me say..... " come on keep quite, ya fada yana mai ture su duka cike da fada "now All of you out of my house, you All no my rules no one comes to my house without my permission,

" and you I will del with you letter, ya nuna Emanuel da  hannu kafin ya wuce ciki, binshi sukayi da kallo  domin sun saba da halin shi na wulakanci  don haka kowacce ta kama gabanta kafin ya jona su da  mugayen kuratan yaran shi,

Wanka yayi kawai ya haye gado domin ya sauke farali a office kuma bayajin yunwa he just need to rest before going out,

---

A zaune suke a barandar kofar apartment dinsu suna shan iska shida iyalin shi  kana ganin y'anda yake tarai rayar ta kasan Akwai soyayya mai karfi a tare dasu,

Gefe daya d'an karamin yaron sune ke wasa akan d'an keken shi na yara,
Kara shigewa tayi jikin shi tsam,

"Ya Akayi ne farin cikin Ahmed? Murmushi tayi tareda fara yimai shagwaba,

" wallahi na matsu  Yasmin batazo ba inaso  inga babana Baban Auwal,  "k'arki damu maman Auwal dina komai yazo karshe insha Allah,

Tsayuwar mashin din da ya dakko ta yasa tayi saurin mikewa tareda rugawa da gudu ta rungume ta,

Itama cike da zumudi ko akwatin ta bata d'auka ba ta rugo suka rungume juna cike da so irin na yan uwan da suka mugun shakuwa da kuma son junan su,

Daka gansu kaga jini daya saidai Yasmin tafi Maryam kyau nesa ba kusa ba duk da ita din kyakkyawa  ce sosai Amma Yasmin tafita don ita farinta  har wani daukar ido yakeyi,

Yarinyar kamar Aljana ga jikinta dai dai da ita,  saida suka gama murnar su sannan ta kalle ta " ina babana?

"Wallahi baba ya tafi zaria Anki rashi wurin aiki shiyasa nazo ni kadai Amma yace shi zaizo daukata,

Wani iri tayi domin taso ganin mahaifin nata sosai tasa rai,  tsaye yayi tareda nan nade hannu yana zabga murmushi domin ganin Abinda sukeyi,

Shi ya matso tareda Sallamar mai mashin din ya kallesu to mushiga  daga ciki idan kun gama murnar ni ko gani na kanwata batayiba wannan karon nayi fushi,

" Iah yayana wallahi tsabar murnar ganin rabin jiki ko boy dina Bangani ba sai yanzu ta ruga tareda rungume shi tsab "I miss you my boy,

Ta fada with so much excitement  yayi dariya shima yaron kamar ya ganeta

A kan kujerun da suka tashi ra zauna tareda zubawa kofar katon gate din ido,

" Aunty ina bunsurun can gidan? Saurin rufe mata baki tayi "kiyi shiru kar Baban Auwal ya jiki wallahi kina zagar mai oga,

" ai Aunty ban taba ganin namiji mai d'an banzan son mata ba irin shi  wallahi ana fadan  sojoji na kwashe kwashe nashi karshe ne,

Shiyasa bana ko kaunar ganin shi A Rayuwata I hate him to the extend,

"Ikon Allah wai maikarfi  na bara ina ruwanki da bawan Allah da baruwan  shi da harkar mutane kuma bai ko San Allah ya tsiroki ba Amma kinsa mai ido,

" ai Bazai ma San daniba  har abada d'an iskan mtsww ta mike tareda nufar cikin gidan domin maganar shi kawai tasa ranta ya baci,

Dariya kawai Maryam tayi domin tasan halin y'ar kanwar tata, ta shiga ciki itama,

Tare sukaci Abinci suna hira atsaka nin su kafin ta fito mata da tsarabar da takawo ma yaron ta na kayan wasa da kuma kayan sawa masu kyau,

Sai su kubewa da Daddawa da sauran kayan gargajiya irin na bahaushe daga mama domin tasan basa samu a bariki,

Saida tayi wanka ta  shirya cikin kana nan kaya San nan ta dora after dress akai domin tana son tafita tasha iska  a wajen gidan dama ta saba duk tazo nan ne wurin zaman ta tana karewa bariki kallo,

Yaron ta ta d'auka ta fito tana tafiya a hankali kamar bataso hannun ta rike da wayar ta hot 8 ta zauna tana karewa gidajen kallo kafin ta sauke akan katon cikin su wato na oga kwata kwata,

Emanuel ne ya fito daga gate din hangota da yayi yasa ya zo da  sauri bakin shi har kunne,

"My friend don come, ya fada with so much excitement da jin dad'in ganin ta domin sun saba sosai kuma shine ummul khaba isin  da yasa ta kara tsanar M.A domin shike bata labarin komai,

Washe mai fararen hakoran ta tayi cike da jin dadi tace " yes woo friend how are you?

"Fine mam hope you are not going back and leav me here again? " yeah I will but I will spend

one month  here with my friend, ta fada tana dariya,

Da yake ba wani kan gado gareshi ba ya ce "come escort me na oga send me' itama kan narawa tace ok  Am coming

Ciki ta koma tareda janyo hijabi ta dora akan kayan jikinta ta saba yaron ta akafada tace Aunty zamuje yawo da EMA,

Kallon ta tayi kafin tace " keda EMA ko sai gyaran  Allah kun hadu kun dace wallahi,

"He is very funny and friendly wallahi inajin dad'in hira dashi Akwai shafta " kodai gulma ? Keda yayanki ba ruwana

Fita tayi tana dariya  sunyi tafiya mai nisa yana gabza mata labari da kuma Abinda ya faru dazu shida ogan shi yaja ya tsaya tareda dora hannu aka,

"Ewo I don die I forget wetin oga tell me wo ' come mo we go back and ask him, kallon shi takeyi cike da mamakin wautar  shi ko waye ya dauke shi a aiki oho,

Da sauri sauri suka juyo domin yasan yayi laifi karya kara wani,

Shikuwa  M.A da ya dauki lokaci yana jiran Emanuel ya kawomai sako yaji shiru kuma yanaso ya fita dole ya fito ya tsaya sanye cikin tree quarter da t-shirt na  Como flag  yayi masifar yin kyau  ga wani Annuri da haske dake bayyane a fuskar shi,

Isowar Ahmed wurin shi yasa ya fara mai magana cike da takaici, " you have to find better cook for me I don't like this guy at All can you imaging him letting Kate and that stupid girl chioma in my house?

Dariya Ahmed yayi kafin yace "oga sun cika naci ne wallahi bebs din nan naga ka gama yayin

su Amma sunki hakura,

" ni bansan me yasa duk Yarinyar da na sake mata fuska sau daya ba sai ta nace min, "farin jini ne oga, Ahmed ya fada cikin dariya,

" kodai rashin class I hate that kind of girls, "am idan mun fito  daga gidan Hajiya zamu biya unguwar shanu inason inyi renewing wasu'

Yafada tareda yin wani tsadadden murmushin shi mai kyau, dariya Ahmed yayi " oga Karfa mu samo wasu karfen kafar kuma  kuma kasan zuby ta kusa zuwa karka hada rigima,

Dariya yayi sosai tunawa da zubyn tashi da yayi  domin tsohuwar budurwar shice kuma itace y'ar gidan ministern kudi Yarinyar naji da kyau da gata sun dade tare da juna suna Kwasar muguwar soyayya atsaka nin su,

Bata kaunar ganin shi da ko wacce mace duk da itama tana nata Rung's din a kasar wajen da take karatu,

Karaso wa sukayi itada Emanuel suna Kwasar dariya, tunda suka matso yake kallon ta yana mamakin wace mahaukaciyar  ce take hira haka da Emanuel gata daga gani kamar tanada hankali,

Tana hango mijin yayar tata da wani a wurin tayi saurin tsayawa daga nesa domin tasan da shine ogan nasu da ake fada kuma wannan ne karon farko da ta fara ganin shi fuska da fuska,

"Amma anyi kyan dan maciji ta furta a hankali tareda zabga mai harara da kuma tsaki, w'anda ya ganta sarai domin kallon ta yakeyi sosai batareda ya cire idon shi akan taba,

" she is very beautiful  but psycho daga gani kyan ne kawai Amma  batada  hankali,

"Oga I forget wetin  you sen......" You are mada Emanuel give me my money ' ya furta cike da jin haushi ya fada motar shi tareda kallon Ahmed "let go before I do something bad here,

Fadawa motar yayi tareda tayarwa  domin shine zaija  motar ogan na gefen shi yana matsa waya,

" wai me ka aikeshi  ne ? "Forget that mad man, saida ya matso kusa da Yasmin ya d'an tsaya tareda sauke glass kadan,

Kanwata zan shiga gari me kike so?
Kawar da kanta tayi domin batason kallon fuskar wannan gayen ko kadan mai kama da Aljani,

" bakomai yaya na sai kadawo' "yau baza Asha ice cream din ba da two one two bread ? Dariya kawai tayi har hakoran ta suka bayyana  tace bye tareda nufar gidan na y'ar uwar ta,

Domin Sam bata son ko minti daya tayi da wannan mutumin, saida sukayi nisa yace " kanwar kace wannan? "Eh sistan maman  Auwal ce,

" Amma dai kamar itama kalar Emanuel din ce ko ? Dariya yayi tareda cewa "kawai tana son mutane ne kuma sun dade da sabawa dashi tun farkon zuwanta,

" Hmm kawai yace tareda ci gaba da d'anna wayar shi har suka isa lafiyayyar unguwar ta malali dake cikin garin na Kaduna

Bakin wani tafkeken gate ya yi horn mai gadi ya wangale mishi ya kutsa hancin katuwar jeep din, tasowa sojojin sukayi tareda Sara mai domin har mai gadin gidan soja ne,

Da kanshi ya bude motar ya fito tareda nufar cikin gidan da tundaga bakin kofa yake jiyo hayaniya,  yana bude falon gaba daya suka koma wacce ta natsu kamar ruwa ya cinyesu,

Y'an  matane  guda uku a cikin falon sau wata dattijuwa bai cikar haiba da kamala faratas da ita tana Jan carbi sanye take da less lafiyayye dinkin buba,

Sallamar shi yasa  Matar ta dago kanta domin ita Sam hankalin ta baya kan yaran zuciyar ta tay nisa sosai,

Washe bakin ta tayi wanda ya bayyanar da hakorin makkan dake gaban hakoranta guda biyu na gold suna sheki,

Saida ya zauna kusa da ita akasa kafin yace "ina wuni momy na? " lafiya lau  yanzu nake son insa Fatima ta kiramin kai a waya danaji  shiru,

"Gani nazo momy kema kinsan dole inzo inganki kullum sai dai idan da Akwai matsala ko aiki ya rikeni kuma ai Zanfada miki,

" ina wuni ya Muhammad, yan matan suka hada baki wurin fada ya waiga tareda zabga musu harara "dama zaman da kukeyi kenan saboda kusa jinin uwata ya hau sai haushi kukeyi kamar karnuka a cikin gida kowacce fuska kamar tayi dambe da toka  kun tasa min ita a gaba kuna ta iface iface,

." banson dibar Albarka Muhammadu kai Bakayi Aure naga Matar ka ba  bare insa ran jikoki ya'yan ka ba kila sai na mutu sannan yaran dake debe min kewa ka sasu agaba da kyara,

Dukan su wani irin bakin cikine ya rufesu wai duk kwalliyar da suka caba shine zai ce kamar sunyi danbe da toka lallai wannan gayen zasuga Matar Auren shi,

Tashi sukayi sum sum suka shige kafin ya kara labto musu wata bakar maganar,  Shigowar Ahmed ne yasa momy tasaki fara'a "Amadu dama tare kuke?

" eh mama  ina wuni? "Lafiya lau d'an Albarka ya iyali, ? Ina labarin y'ar Albarka Yasmin? " ai momy dazu kuwa tazo bariki tazo mana hutu,

"Ai yar nan nada hankali sai daya kawai da kukazo tayi mugun shiga zuciya ta, kallon Momyn nashi yayi kafin ya kalli Ahmed yace " who is Yasmin?

"Oga that my sister, tabe baki yayi   kafin yace yaushe kukazo nan har momy ta ganta? Last time datazo  ka aikoni lokacin zata tafi muka biyo nan kafin in sauke ta gida,

Shiru kawai yayi domin yasan halin Momyn shi idan taso mutum, " Muhammadu yaushe zanga Auren ka ? Idan Bakada zabine  ni inmaka zabi kuma nasan zakayi farin ciki,

.

"Momy Muyi magana mai ma ana don Allah Mubar wannan, " oh wannan batada ma'sna kenan ? "Muhammadu idan lafiya ce Bakada ka fada min anemi  magani shekarar ka talatin da bakwai yanzu kakusa  arbain kullum ba wai yarinta kake karawa ba shekarun ka natafiya ne fa, Amadu ka fadawa Abokin ka ko mai gidanka zance ne oho domin nasan baida wani Abokin da zai iya fadawa matsalar shi sama dakai,

"In Akwai  matsala kufada min, ta fada cike da damuwa aranta, saurin riko hannun ta yayi tareda rage murya a hankali,

" momy na kiyimin hakuri zanyi kok'arin yin hakan idan na shirya banason inyi Auren da zan shiga damuwa insa Kaina a matsala momy kitayani Addu'a kawai,

Tashi yayi tareda kallon Ahmed da idanun shi da sukayi ja saboda tausayin mahaifiyar  tashi "muje ko dafatan bakwa bukatar komai?

Ya tanbaye ta Amma ido kawai ta zuba mai domin babbar bukatar ta itace Auren tilon d'an nata

ta kuma ga jinin shi a duniya,

Yana fadawa motar ya jefar da wayar shi ya dafe goshin shi da yafara Sara mai Ahmed ya tayar da ita sai da suka tsaya bakin unguwar shanu  sannan yace " oga Gasu nan fa sai ka zaba,

Daga jajayen idanun shi yayi ya zuba wurin matan dake Jere akan titi da shiga kamar Tsirara

Fita Ahmed yayi saida yayi ma wata magana tareda Ciro bandir din kudi ya bata ya dawo cikin motar "oga na yi making Arrangement din,

" ok muje mess ", ya fada kai tsaye suka wuce batareda  sun tafi da ita ba,

Karfe kusan tara nadare suka dawo, kasan cewar lokacin zafine kusan mafi. Yawancin mutane kan fito waje domin shan iska  duk da kuwa Akwai wutar lantarki ta ko ina ga A.c

Amma sanin kowane iskar ubangiji tafi kowace iskar bature ni ima tareda Amfani a jikin dan Adam,

Hirar su sukeyi irin ta y'an Uwa gefe data bowl ne dauke da chips Yasmin ta Ajiye agefen ta wandone ajikinta dogo mai fadi sosai da wata tea shirt mai guntun hannu ta kamata tsam kanta sanye da hular net  kafar ta kuwa silipas ne sabo tayi matukar yin kyau sosai duk da bawai kwalliya tayi ba,

Amma she look very Adorable  kamar ka sace ta ka gudu Babyn ta hadu sosai kamar y'ar Aljana ga kirjin nan cike tab da dukiyar Fulani daga kasa kuwa zakasan Allah yayi halitta a wurin nan mai daukar hankali,

Maryam ta kalle ta " Yasmin kije ki saka hijabi kinga yadda mijin maman Amla ya kasa shiga cikin gida tun dazu saboda ganin ki a nan kuma ga shigar dake jikin ki,

"Kyale tsinan ne Matar shi naciki tana jiran shi Amma ya tsaya kallo na Ayya kuwa sai na haukata shi,

" nidai ki rufamin Asiri kina ganin Matar nida ita saidai gaisuwa daga nesa saboda tsabar kishi tun zuwan ki na farko tazo nan tayi min magana "wai me yasa mukeson kawo kannin mu mata bariki neman maza?

" Kwal uba kika ce mata mene? "Hakuri na bata nace nidai ba neman miji kika zoyi ba zumunci ya kawoki tayi hakuri,

" ai wallahi sai nayi maganin ta Allah ya kai mu gobe bari ma kigani tun yanzu in dana tarko,

Mikewa tayi cikin salon daukar hankali har tana girgiza kirjin ta wanda suka yi d'an rawa kadan da saida numfashin shi yayi skipped sannan ta duk'a ta dauki bowl din chips din da takeci,

Ta kalli y'ar uwar ta "muje ciki Aunty ai munsha iska sosai ga boy na yayi bacci, baza mai duwai wukan ta tayi da gangan saida ta saka kafar ta cikin falon ta juyo tareda jefa mai blow kiss har da kashe mai ido daya cike da salon daukar magana

Ta fada cikin falon, kusan sumewa yayi a tsaye yakai hannun shi saitin wandon shi ya dafe saida ya dauki lokaci kafin ya daure fuska tamau ya shige cikin gidan nashi shima dauke da kudurin samun wannan Aljanar Yarinyar daga gani yar hannu ce,

Ita kuwa tana shiga ta kyal kyale da dariyar mugunta " ai zaki ga BARIKI maman Amla,

"Dariyar me kikeyi Yasmin? Ina fatan ba wani mugun Abin zaki kulla ba domin nasan halinki sarai dariyar ki ba Alkhairi bace,

" kai Aunty na ba komai kawai inajin nishad'i  ne' "Hmmm Allah yasa, ta wuce masaukin ta wato dakin y'ar uwarta domin bin lafiyar gado saidai kwanciyar ta keda wuya ba Abinda ya fado mata sai fuskar wannan gayen,

" me yasa kake neman mata? Shine kawai ta samu bakin ta da furtawa tarasa dalilin da yasa taji kawai tsanar shi ta ragu a cikin ranta tunda ta ga fuskar shi a karon farko,

Kirar jikin shi domin ta hango irin muscles din da ya Ajiye na karfi w'anda tasan ba shakka idan ya riki namiji zai ji jiki bare mace,

His face look innocent he look pure but why is he like that? Saurin runtse idanun ta tayi tareda yin Addu'a har barawon ya dauke ta,

*"farkon farawa kenan my fans ina fatan wannan labari nawa da na faro ya baku ni shadin  da kuke bukatar samu ya kuma ilmantar daku ya fadakar*

*"ku ci gaba da biyoni nidin ce dai "UMMU AMMAR Aunty Fener ku kuma Matar soja*
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
_*BARIKI*_
_Auren soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

_written by fenerh_
Maman Ammar

*Dedicated to*
Fiddousi mainasara

3&4

Kasan cewar ta saba tashi da wuri, yasa ko a gidan y'ar uwar tata ta tashi tun karfe shida tafara gyara musu gidan,

Ita ta shirya breakfast na gargajiya koko da kosai   domin basa rabo da ni kak'ken wake a firij domin k'arin safe,

Saida ta kammala da wannan ta kwashi kayan su ta fita domin d'aurayewa, tana fitowa taci karo da maman Amla na tsaye tana kallon gidan nasu,

Daga murya tayi tareda cewa "ina kwana maman Amla  mun sameku  lafiya? Wata irin muguwar harara ta zabga mata tareda maka mata mugun tsaki ta shige tareda cewa " karuwan banza masu kwace mazan  mutane kawai,

Dariya Yasmin tayi ta girgiza kai "zakiga karuwa ganin idon ki karamar y'ar bariki sai na koya miki darasi,

Tafada can kasan zuciyar ta domin batason tayi wata hayaniya da Matar Aure Ace tayi rashin kunya Amma sai ta gasa ta a ruwan sanyi zata koya mata hankali,

Wankin ta tayi ta shanya kasan cewar ba yawa ta koma ciki lokacin har Ahmed ya shirya cikin kakin shi ya fito fes Maryam na rike da hannun shi tana cewa,

....yanzu dear Bazaka sha ko tea ba? " Nop  nayi latti kuma kinga mun makara yau, Shigowar ta yasa suka kalleta ganin ta rike da bocket "Yasmin har kintashi?

" ina kwanan ku ta fada tareda kallon mijin yayar ta "ni ai tun karfe shida Natashi da yake ku yan

gayu ne kalli karfe takwas fa yanzu,

" eh bakyason matata ta huta ne ? "Inaso y'ar uwata ta huta don haka nayi mata Aikin komai har breakfast nayi muku yau,

" wow kanwata godiya nake bari ingani yafada yana matsawa wurin d'an karamin table dinsu ya bude flask yaga koko da kosai,

"Gaskiya kin burgeni kanwata a zuba min idan naje office zansha Acan nayi latti oga na jira na yanzu,.

Juyawa kawai tayi ta nemi flask me kyau ta zuba mai koko da kosan yayar ta karba ta rakashi har waje kafin ta dawo cikin gidan,

Kukan yaron Yane yasa ta nufi cikin dakin ta dakko shi dakan ta tayi mai wanka ta shirya shi kafin yasha nonon shi,

Shirya wa tayi cikin kwalliyar ta mai matukar kyau da daukar hankalin duk wani namiji, riga da wandone tasaka sunfito da surar ta mai kyau duk da rigar takai har guiwar ta,

Ta yafa d'an karamin mayafi ta fito tana zuba kamshi da kuma kyalli,
Taku take kamar wata Sarauniyar kyau tsabar jin kanta datakeyi,

Y'ar uwar ta ma saida tace " yayi Autar Mama wannan irin kyau haka saikace suruki na zai zo?
Murmushi tayi kafin tace "kin manta kinada suruki a kusa Baban Amla,

" aa Yasmin kirufa min Asiri k'arki tafi kibarni da rigimar Matar nan don y'ar bala'i ce ta karshe wallahi, "takai karshen ta kuwa Aunty watch and see,

...nidai aa ki fita hanyar ta kawai, " hmm kawai tace tayi waje' "ina zakije? " shan iska zanfita "ki rufa min Asiri ki sanya hijabi Yasmin kinsan halin sojoji kuwa?

" wanda duk ya sa rai yasha wuya domin gani nan bari nan wallahi bani ba soja, shiru kawai tayi ta bita da kallo har ta fice,

Tana fitowa Emanuel na fitowa daga cikin gidan ya washe baki tareda nufota jikin shi na rawa"my friend '

"Yes wo good morning EMA, ya zauna gab da ita tareda zuba mata idanu domin tayi mugun yimai kyau, " chiii friend this kind fine no be small ting wo if my oga saw you Ahh,,,

Ya fada yana cizon yatsa basar da shirmen shi tayi tareda kawo wata hirar "why are you not going to office? " na because I dey cook for oga so I no dey go office,

"Friend oga bring one Celine Dione yerstaday no shape no boobs noting I don no wetin he go enjoy there wo?

Wani irin kallo ta watsa mai domin ya fara bata haushi da mu gayen hirar shin nan da baya gajiya kowa ya tanbaye shi oho?

Ta manta ita ke tanbayar shi a da can saboda gulma, kuma ita yau bata bukata impact zaman jiran Baban Amla takeyi Alakar sa idon can ta juya bata ta oga MA yanzu,

Ganin taki bashi fuska ya canja magana " I beg friend help me na oga say ma I cook kuka soup for him before he come back,

Kallon shi kawai tayi domin ya ishe ta da magana gashi da mugun nacin tsiya bata taba dana sanin sake mai fuska ba irin yau,

Cewa tayi ya tafi kawai zatazo ta nuna mai da fatan ogan shi Bazai dawo ya sameta ba yayi saurin girgiza kai "no oga no go comeback now till one O'Clock,

Saida ta fadawa Aunty Maryam ta fito suka wuce tare yana ta faman zabga mata magana,

Tundaga harabar gidan ta fara baza idanu fulawoyin da aka zagaye gidan sunyi matukar burgeta bata taba sanin haka wurin yakeba  don bata taba matsawa ko jikin gate din dake zagaye da Bob ware ba ginin na tsakiyar shi,

Wani irin ni ima ke kadawa da ita ga kamshin furanni kala kala ga kayan mar mari zagaye da gidan irin su lemo gwanda mangwaro ayba har ma dasu gwaba,

Tsarin wurin ya matukar burgeta " hmm gidan mutum daya d'an iska yafi kuma kowa tsula iskan ci ogan y'an iska, ta fada aranta,

Falon gidan kuwa ai sai shuru kawai domin tsarin gidan gaba daya kamar Akwai mace saboda kyale kyale ga shi kalar komai favourite dinta purple and white,

Daga gefen kitchen din step da zai kaika upstairs din ne she wish zata iya hawa saman shima

taga tsiyar dake ciki,

Maganar EMA ta dawo da ita ta bishi cikin kitchen din da ta kira Aljanar mace domin tana mugun son ganin kitchen a tsare ga wannan ya tsaru kamar a turai komai na bukatar macen data San kan kitchen Akwai a ciki,

Ajiyar zuciya ta sauke tareda ku durin idan zatayi Aure haka zata tsara nata insha Allah,

Da taimakon EMA ta hada komai ta shirya musu lafiyayyar miyar kuka da taji namomi zuku zuku aciki sai kamshin garlic da citta ke tashi  domin sunada komai na Amfanin gargajiya da Alama ogan nason harkar gargajiya,

Shi kuwa EMA baki har kunne sai zuba yake mata kamar kanya har ta matsu tabar gidan tana kammalawa tace zata wuce ya rakota sai godiya yakeyi kamar ya ari baki,

"Tank you friend you save me today from my oga  suna bude kofar shigowa wata sisi ta shigo kyakkyawa ce ba laifi ga wanka iya wanka domin less din jikin ta kadai zai nuna ma kudi sun koka  Anan,

Komai na jikin ta kudi ne har Bangle's da jakar hanun ta Abin kallo ne sai walwali take tana zabga kamshi,

Wani irin kallo suke watsawa juna domin kowa na hango kyan kowa ita Yasmin Yarinyar burgeta tayi domin tana son mace mai daukar wanka kuma wannan tayi ba karya,

Ita kuwa zuby wani irin hade fuska tayi tana mata wani irin kallon ke wacece kafin ta bude baki cikin masifa tace,

" Emanuel who the hell is this? Tuni jikin shi ya fara rawa "sory madam na my friend I call her ne to help.......

" quiet ke kuma kiji nan nan gidan mijin da zan Aura ne ban y'arda ko wacce mace ta shigomin cikin shiba ni na tsara gidana kuma  banason mace na rabar shi

Kinzo da kazaman kafar ki har cikin gidana to kar in kuma ganin ki daga yau stay away from my husband house,

Me neman kuka ai jikin Yasmin har rawa yakeyi ta gyara tsayuwar ta dakyau harda jijiga jikin da saida zuby tayi Addu'ar Allah yasa Muhammad bai taba ganin wannan Yarinyar ba,

"Ke wacece da zaki zo har cikin falo na kina min ihun wai gidan mijin ki  lallai karuwan cin ki ya girma

" kin shigo min gidan Aure har kinada gut da zakice wai gidan mijin ki to ni Matar shi ce sai ki jira ya Auro ki kafin Kizo kiyimin gadara kuma yanzu kibar min gida kafin inhada ki da kuratan sojojin dake wajen gate din nan,

Wani irin tsuma jikin zuby ya farayi tuni hawaye suka wanke mata fuska wani irin kishi ne ya tokare mata kirji,

Kafin ta iya bude baki tayi magana kawai Yasmin ta turata waje ta datse kofar har tana huci kamar da gaske gidan tane,

EMA suman tsaye yayi ya dora hannu akai ya zama kamar statue duk da ba hausa yakeji ba yasan what ever Yasmin is saying is not right at All

"Chineke me friend na oga love wo na him girl friend she come from abroad  you don kill me......

Tuni yafara paret tsaki ta yi tareda bude kofar ta leka taga ta tafi ta fito tayi wucewar ta gidan y'ar uwar ta ko ajikin ta,

A zaune yake a cikin office dinshi sanye da kakin shi yayi wani irin kyau a ciki gefen shi pistol ce da kuma system din shi har ma dasu tabs din shi akan table din  ya dora kafafun shi dake sanye da boot dinshi masu sheki akai,

Kanshi a sama yana tunanin maganar  shi da Momyn shi jiya, ta shigo cikin office din kamar yaki ta buga kofar jikin ta na rawa,

Har saida yayi saurin mikewa cikin hanzari ya janyo pistol dake gefen shi, ganin fuskar ta yasa yaji ranshi ya mugun baci,

.
Komawa yayi ya zauna kawai batareda yace mata ci kanki ba ta fara magana, " ka kyauta Muhammad na kiraka yakai sau uku jiya kaki daga min waya,

Bayan na fada maka zan dawo a jiya baka damu ba sannan d'an wulakanci na iso ko ka neme ni......any way nagano  matsalar wato Aure kayi Muhammad bayan tafiya ta bayan kayi min

Alkawarin Aure yanzu duk halaccin da nayi ma irin sakayyar da zaka biyani da ita kenan?

"All......." Quite don't you there couse me ke kika Ajiye ni ? Auren ki nayi ni nace ki jirani ? Na fada miki sai ke zan Aura ? How thare you banged into my office like this?

"Duk Rung's din da kikeyi a can na sani kar ki rena min hankali kuma Aure da kike magana.... Shiru yayi tareda kare matse fuska " eh nayi Aure kiyi Abinda zakiyi kuma yanzu kifitar min a office kafin inyi loosing control inci ubanki a nan '

Wani irin kuka ta fashe dashi kamar zata hadiye zuciya ta juya zata fita tana rufe baki yace "wait, tsaya wa tayi cak domin tayi tunanin hakuri zai bata,

" stay away from my wife and my house, da gudu tafice bako waiwaye duk inda ta wuce yaran shi kallon ta sukeyi domin kowa ya Santa dashi kuma sun San irin y'anda oga,ke mugun ji da ita to yau me ya faru,

Tana ficewa ya zauna kan kujera yana fitar da huci kamar kumurcin maciji yana tunani ko wace shegiya ce ta shigo mai gida har zuby ta ganta,?

Zaici uban Emanuel yau sai ya kulle shi don uban shi, baiso ya ma zuby haka ba Amma ai tasan bayason mace tayi mai gadara da rashin da'a shi yasa ya mata haka amma zai lallashe ta letter,

Intercoms ya danna Ahmed ya shigo saramai yayi ya koma gefe yana jiran umarni "ka hada

min connection din TV inason inga wace ce a gidana?

" ok sir domin Akwai connection da yake ganin komai dake faruwa a gidan nashi Abinka da zamani,

Janyo tan din dake gaban shi yayi danna kawai yafara viewing Abinda ya faru na yau Ahmed zare idanu yayi waje lokacin da video ya fara aiki,

Goshin shi ya dafe cike da kaduwa "wannan Yarinyar zata kashe ni waya aiketa gidan oga,?

MA kuwa tagumi yayi yana karewa karfin halin ta kallo mamakin ta ya mugun cika shi,

" og a....... Ahmed ya fada bakin shi na rawa zai bashi hakuri yayi saurin daga mai hannu tareda da nuna mai kofa yace ya fita kawai,

Jikin shi yayi sanyi ya fita shi kuwa ya kalli video din yakai sau uku yana repeat din shi dressing dinta yake karewa kallo har zuwa y'anda ta baje mai cikin kitchen ta hada mai miya a natse cikin kwarewa da kuma tsantsar tsabta,

Stop yasa dai dai lokacin da ta jijiga jikinta a gaban zuby zata zabga masifa d'an karamin bakinta ya tsurawa ido har zuwa lips din masu sheki da kuma idanun ta masu kama da fish lashes dinta sunyi zaro zaro ga gefen fuskar ta suma akwance tana sheki da Alamar taji gyara,

Samun kanshi yayi da jin nishadi karfe sha biyu ya bar office yace su tafi gida shima bai San dalilin shi na son komawar ba kasan cewar shi mutum mai son Aikin shi baya son wasa ko

kadan,

Gefen mutane biyu kuwa sai zullumi sukeyi domin basu San me ogan nasu zaiyi ba yau wato EMA da Ahmed,

Motar su na tsaya wa sojojin shi suka bude mai motar ya fito kawai ya samu kanshi da wai gawa kofar gidan Ahmed din bakowa a wurin,

Saida gaban Ahmed ya fadi domin yasan wa yake kallo Yarinyar nan tajamun gidan ya shiga EMA tuni ya tsure tun jin jiniyar motar ta ogan don yasan lokacin dawowar shi baiyi ba

Tundaga kofar falon ya cire rigar saman ta kaki ya rataya a wani abin rataya kaya ya zauna a kan kujera tareda dora kafa daya kan daya yana girgiza wa,

Ahmed na shigomai da kayan shi ya nufi hanyar fita tsayar dashi yayi tareda bashi umarnin yayi serving dinshi Abinci,

Kallon shi yayi domin baiyi tunanin zaici Abincin da yana gani Yasmin ta hada shi ba, da sauri ya nufi kitchen ya samu EMA na sintiri hannu saman kai ya daka mai tsawa,

Ya natsu tareda bashi umarnin aje ya shirya table din oga, sanin halin EMA yanzu zai kuma tafka wani shirmen yasa ya hada mai komai da kanshi ya zuba ya jera a kan table din dake gefen shi ya zuba mai komai tareda dakko mai ruwa mai sanyi har da coke ya Ajiye a gefe sannan ya fita domin zuwa jawa uwar rigima kunne,

Tashi yayi ya zubawa plate din miyar idanu tayi gwanin sha'awa miyar batayi mugun yauki ba yasa mu kanshi da daukar spoon ya deba yakai bakin shi saida ya rintse idanun shi tsabar dad'in da ya ratsa shi,

Bai San lokacin da ya shanye miyar tas ba batareda ya ko kalli tuwon semon  da EMA ya tuka mai ba ya dauki ruwa ya kora yaji ya koshi tab kamar yaci wani Abu,

Gaskiya girki hannu ne sirri ne kuma ga duk macen da tasan me takeyi ko ruwa ta dafa na tea zakaji shi daban

Ko takan EMA bai biba ya haye sama ya fada wanka EMA na ganin ya tashi ya fito ya tattara kayan yayi kitchen da gudu tareda Addu'ar kar ya shiga hannun oga,

*UMMU AMMAR*
[8/30, 2:56 PM] Feenerh Wrtr: 🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
        _*BARIKI*_
_Auren soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

_written by fenerh_
Maman Ammar

*Dedicated to*
Fiddousi mainasara

5&6

......Ahmed na shiga gidan nashi ya sameta a baje ita da yaron ta  a falon sai cin Abin cinta

takeyi hankali kwance shi kuma ta jefa shi a zullumi,

Gaishe shi tayi ya zauna a kusa da ita tareda daukar yaron shi "ina Maryam take? " Aunty na hutawa bacci takeyi bari in kawo ma Abinci,

Ta fada tana shirin mikewa yace "no zo Muyi magana Yasmin, yakira sunan ta tasan kwanan zancen don haka ko a jikin ta ta koma ta zauna tareda zabga mai na mujiya,

Dariya ya yi ganin reaction dinta, " Yasmin haka kikeyi a school? "Kallon Bangane ba tayi mai, " eh naga kinada mugun karfin hali ne wanda ba haka Maryam take ba ita matata batason fitina bata son matsala Amma ke naga idan ma matsalar batazo ba da kanki kike tara kai ki kirata tazo,

"Yaya Ahmed Nafasan me kake son fada' ta fada tana turo baki " hhhh yayi dariya kafin ya cigaba,
"Nasan kinsan me kikayi ai, " Amma so kike a kulle ni ne kinsan laifin zai iya komawa Kaina?

"Oga nane kuma Yarinyar da kika yima wulakanci bakisan tsakanin su ba " oga Muhammad na matukar jida ita tanada muhim manci a rayuwar shi ita kadai ce macen da ya dade da ita kuma nake sa ran zai iya Auren ta duk da bansan zuciyar shi ba amma kowa yasan kusan cin su,

"To ni ya Ahmed ina ruwa na dasu ? " me kikaje yi gidan oga dazu? "Nifa taimako nayi Emanuel ne.... Ta yi mai bayanin y'anda sukayi dashi yayi shiru,

" amma Yasmin duk barikin nan kirasa wanda zakiyi mutumci dashi sai EMA?    "Kaji yaya to sai inki mai sona? " aa ban fada ba nidai a kiyaye kar ajamin matsala da aiki na,

Tashi tayi kawai tare da duba sakon da yashigo wayar ta , wani murmushin mugun ta tayi kafin ta yi tsaki "zanci ubanki maman Amla sai nasa jinin ki ya hau,

Dama bayan Fitowar ta daga gidan MA tayi karo da Baban Amla sukayi musayar number  yace zai kirata suyi hira da dare

Ganin sakon da ya turo mata yanzu yasa ta kara d'ana tarko,

_zan kiraki Anjima Muyi hira face to face domin kin tafi da zuciya ta har ma da murad'i na_

Reply ta tura mai

_saika zo ina nan ina jiran ka I love you_

Ta tura tana tun tsura dariya,  ai kuwa jiki na rawa ya kirata kai tsaye a lokacin yana zaune da Matar shi ya mike ya fito don kawai yaji muryar ta,

Ba bata lokaci ta d'auka tare da karya murya " Aslm Alkm "Wslm gimbiya kin rikita ni gaba daya na matsu ban ganki ba pls ki leko ko sau daya inyi tozali da kyakkyawar fuskar ki ko zanji dad'i,

Wata irin dariya tayi mai tafiya da ruhi  tace " Karka damu zaka ganni sai ma ka gaji da gani na' "Allah kar ya nufe ni da gajiya da ganin ki gimbiya,

" sai Anjima yanzu ina busy ne' "ok bye gimbiya ta, ta katse wayar tareda tunawa da bakar fuskar shi tace " god forbid bad thing,

Karfe takwas na daren ranar yasha wanka tareda nufo kofar gidan nasu ya kirata a waya,
Tana zaune suna hira da Aunty Maryam ta ce "ina zuwa Aunty nayi bako,

" zaro ido tayi waje "yaushe kika fara kula samari Yasmin? " kaji Aunty ban isa bane? "Am nineteen fa going to twenty,

Naji kije kidawo kifada min waye? " ok ta fada saida ta koma ciki ta kara gyara fuskar ta tareda fesa turare mai laushin kamshi sannan ta yafo gyale akan  doguwar rigar jikin ta,

Tayi matukar yin kyau kamar ka sace ta ka gudu ta fito cikin taku dai dai, yana hango Fitowar ta ya kashe ta da ido  kamar ya hadiye ta yakeji Babyn ta mugun tafiya da tunanin ruhin shi,

"Barka da fitowa gimbiyar Umar, murmushi tayi itama tareda cewa barka da dare'

Namiji muna fuki  saida ya kalli kofar gidan shi sannan ya ce mu dan matsa can nan haske yayi yawa banason sa ido, batareda ta damu ba suka matsa d'an gaba kadan wanda tana hango harabar gidan na Oga kwata kwata kuma idan ba karya idanun ta ke mata ba tana hango mutum ta saman benen  ta waje wurin da Akayi domin shan iska kuma idan mutum na wurin yana iya hango duk Abubuwan dake faruwa akusa ,

Sharewa tayi kawai suka fara zuba hira kasan cewar ta mai son zance tuni ta saki jiki da shi har tana dariya, hasken wayar shi ya haska fuskar ta,

" gimbiya ina fatan  ba w'anda ya riga ni ko? "Aa ni banida saurayi banda lokacin kowa, ta fada " kai Amma ni mai sa'a ne Ashe,

Gyara tsayuwar shi yayi tareda d'an riko gefen gyalen ta "baby kin fa hadu sosai Allah yayi miki kira mai kyau komai yaji,

Shiyasa gaba daya kika tafi da ima nina, " Anzo wajen ta fada tareda kok'arin janye gyalen ta Amma da yake d'an duniya ne  tuni ya rike hannun ta tamau,

Wani irin laushi yaji a hannun kamar na jariri  ya lumshe idanu "wow gimbiya hannun ki keda wannan laushin lnaga.......

Fisge hannun ta tayi cikin fushi tareda matsawa kadan " bana son irin haka fa shiyasa naki kula samarin yanzun nan kai ma zamu bata idan ka kuma irin haka,

"Oh gimbiya sai kace rainon kyauye? Keda nake ganin ki a waye "ba irin wannan waye war nayi ba don haka saida safe,

Ta juya cike da takaicin rike mata hannu da yayi d'an iska gobe zan cika aiki na in watsar da kai shege,

Kiran ta yake tayi amma ko juyowa batayi ba tayi shigewar ta gida,

Muhammad kuwa tun lokacin da ya haska fuskar ta yaga irin dariyar da takeyi yaji zuciyar shi tayi mai baki ya miki tareda dunkule hannun shi kamar zai daki mutum

Ganin ya riko hannun ta ai tuni ya wuce cikin gidan don ji yayi jinin shi na harbawa kamar zai tsiyaye a jinin shi,

Daga karshe wurin motsa jikin shi ya nufa yafara daga wani heavyweight da ko za a hada mu mu goma baza mu iya daga shi ba,

Saida ya hada gumi kamar w'anda ya fito filin daga ya mike tareda daukar ruwa mai sanyi ya sheka wa kanshi,

Towel ya d'auka ya fara tsane jikin shi dake tsiyaya kafin ya wurgar a zafafe ya  jefar ya nufi bathroom ya sakarwa kanshi shower batareda ya cire gajeran wandon  jikin shi ba,

Saida ya dauki lokaci mai tsawo a tsakiyar ruwan kafin ya fito daure da towel ya fada gado, bai taba tsintar zuciyar shi so restless ba irin yau  meke damun shi  ?

Ya rasa me yasa shi jin yanayin da yake ciki kodan sunyi fada ne da zuby? Runtse idon shi yayi gam tareda dunkule Hannayen shi yana maida numfashi mai zafi ji yake kanshi na juya wa,

Jin ankwanta  a bayan shi yasa shi saurin zabura ya juyo domin ganin wace shegiyar  ce ta isa da har ta shigo mai gida batareda ya kirata ba kuma for that matter har bedroom dinshi,

Ganin fuskar zuby yasa ya d'an yi cool dwan ya maida wukar fadan komawa jikin shi tayi tareda sa mai kuka ,

"Me yasa zaka hora ni haka Muhammad ? Kasan ina matukar kaunar ka me yasa zaka yimun haka ? Na tanbayi Ahmed yace mun kanwar shi ce ba Matar ka ba ce Am sorry baby for what I did,

" a jiyar zuciya ya sauke tareda cireta a jikin shi yace "is ok kinsan banason raini ai " riko hanun shi tayi masu burgeta saboda wasu jijiyoyi da suka shata ko ina kana gani kasan na karfi ne tareda motsa jiki,

Kallon shi takeyi wani iri Kamar hoto domin ba haka yake ba ya canja "meke damun ka Muhammad dina? " waya bata baka rai ? Nasan Muhammad din zubaida ba haka yake ba why the sudden change?

"Ni ba wani canji ke ke ganin haka, " ok ya isa ni dai hakuri nazo bayar wa don haka let me take a bath and come you no I really miss you ta fada tana daga gira,

Saurin tsayar da ita yayi "no need ki koma gida bana bukatar komai sai hutu yau please no

aguement,

Sanin hali yasa taja ta tsaya tareda zuba mai ido kafin ta dauki key din motar ta ta fita kawai kafin ya kuma hawa,

Runtse idanun shi yayi gam yarasa meke damun shi ji yake kamar ya mike ya dawo da zuby amma ina yasan zataso ya taba ta shi kuma yagaji da wahalar da jikin shi batareda ya samu Abin da yakeso ba,

" wai haka ne matan suke? To meye zaisa yayi Aure tunda shidai  har yau baiji wani Abin da zaisa yace zaiyi Aure ba, sex food what ?

Shidai yasan ko mace goma yakeso a rana zai samu but meye dadi a cikin su duk Abin daya ne shi har yau bai samu ruwan da zai kashe mai kishi ba har yau gobarar cikin shi na ci

Shi mace ma duk wadda ya taba bayajin wani feelings he is just using them to reduced the fluid

__________

Umar ya kirata yafi sau goma taki dagawa Shikuwa a halin yanzu baijin  zai iya hakura da ita har dai da yaji irin taushin dake jikin ta yasha cudanya da mata Amma ita da ban ce shi gaba daya ma ya canja akalar  zuciyar daga samun biyan bukata zuwa mallakar ta gaba daya Auren ta zaiyi kawai,

A ranar Sam Matar shi bata gane mai ba domin ya mugun daure mata fuska karshe ma ko makwanci yaki hada wa da ita,

Falo ya dawo sai faman text yake turawa Yasmin na lallashi Amma ina tama yi nisa ita a bacci tareda ku durin cin uban maman Amla da safe,

Tana tashi da sakon nin shi tayi karo dariyar mugunta tayi mai kafin ta tura mai msg

_Zamu hadu kafin kaje aiki by_

Ta fara taya y'ar uwar ta aiki tana cike da nishadi w'anda saida Maryam tayi magana "Yasmin me ke faruwa? Nifa ban gane miki ba Sam '

" bakomai Aunty na kawai naji dad'in wannan ziyarar da na kawo muku ne jina nake cikin farin ciki tun zuwa na, Hmm kawai Maryam tace kafin tace....

"Allah yasa ba wani Abun kike hadawa ba , Ameen ta Amsa saida suka kammala Aikin gidan ta fada wanka shirya wa tayi cikin wata riga da wandon Pakistan purple wandon fari tayi matukar yin kyau ta gyara gashin ta mai tsawo tareda dunkule shi gyale fari d'an karami ta yafa ta fesa turare ta fito,

Wani sheki takeyi ga kayan sunyi matukar karbar ta rigar ta d'an kamata ta West ga wandon pencil silipas ts sanya masu d'an tudu ta dauki wayar ta ta kirashi,

A lokacin zaune yake Matar shi sai zuba take amma hankalin shi na kan wayar shi duk da yayi late Amma Bazai taba tafiya bai ganta ba,,

Motoci tagani a kofar katon gate din a Jere hilux biyu da kuma wata Benz Army colour a tsakiya sojoji ne a tsaye da bindi gogi kamar zasu ci babu dauke kanta tayi duk da taji tsoro saida ta kusa kofar gidan na Umar ta kirashi " ka fito ina waje,

Wani irib zabura yayi kamar wani maye ya fito batareda yako kalli Matar shi ba jikin shi na rawa , meke damun Baban Amla ne wai ta fada tareda biyo bayan shi,

Lokacin har ya karaso kusa da ita kamar zai rungumo ta "gimbiya kin sani cikin wani hali wallahi na horu da yawa a Gaskiya kin gama tafiya da zuciyar Umar,

Murmushi tayi na mugunta domin hankalin ta na kofar gidan nashi kuma ta hango Matar shi tsaye ta dora hannu akai hawaye na zuba,

Karaso wa tayi kamar guguwa  ta matso " Amma Allah ya isa tsakani na dake wallahi karuwa kawai masu shigowa bariki domin kwace mazan mutane a haka zaku kare tsinan nu,

Wani irin tsawa ya buga mata tareda yi mata tsatstsauran gargadi "hauwa ki wuce kafin yanzu in canja Shawara akan ki wallahi,

Tasan  halin shi dole ta wuce cikin gidan tana kuka kafin ya nad'a mata  na jaki tana wucewa Yasmin ta juya zata tafi domin burin ta ya cika tasan yanzu can ta matse musu ko ya lallashi Matar shi ko yayi biyu babu,

Shan gaban ta yayi jikin shi na rawa " Yasmin please kiyi hakuri zan ja mata kunne k'arki tafi ki barni cikin damuwa,

Tsayawa tayi cikin daure fuska "aini ban ma San kanada Aure ba da ban saurare ka tun farko ba kuma indai wannan ce Matar ka wallahi ban Auren ka don ba tun yau ts saba Zagina ba don haka ka kama kanka dani kafin in hada ka da yaya na,

" what is happening? Taji muryar Ahmed saurin juyawa tayi wurin shi "Yauwa ya Ahmed ka shiga tsakani na da wannan mutumin yasa min ido ka man iyaka  dashi ko dole ne in soshi  tayi shigewar ta cikin gidan batareda ta ko saurari Ahmed din ba,,

Muhammad da ya fito daga gidan shi har ya shiga cikin motar shi yaga duk Abin da ya faru yana hango su daga cikin motar har Fitowar Ahmed da wucewar ta ciki,

This girl is unbelievable meke damun ta ta hada shi da budurwar shi yanzu kuma miji da mata bayan sun gama shan soyayyar su,

Isowar Ahmed cikin motar yasa shi dawowa cikin dogon tunanin da yakeyi gaida shi yayi cikin respect irin nasu na sojoji sannan aka rufe motar suka kama hanya,

Sai bayan sun isa office ya kirashi office, " Ahmed meke faruwa ne dazu I saw everything me ka fadawa Umar? Me yake tsakanin su da sister ka?

"Oga wai yana sonta ne kuma yanzu tace ya fita hanyar ta ni ban gane me ke faruwa ba shima nace ya jirani har mu dawo gida Muyi magana domin nasan halin Yasmin,

" Yasmin"" ya furta sunan can kasan zuciyar shi sunan ta Akwai dad'i sosai,

Ka fada mai karya kuma gangan cin zuwa gidanka tunda tace ya kyale ta ba a so dole don haka warn him before I do something about it

"Ok sir I will do so , ya sallame shi tareda maida bayan shi bayan kujera ya runtse idanun shi yana wani irin murmushi " what a woman Yarinyar nan me take nufi da rayuwar suda ta shigo bariki ?

*I don't no kuci gaba da biyo ni,"*

*UMMU AMMAR*
[8/30, 2:56 PM] Feenerh Wrtr: 🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
_*BARIKI*_
_Auren soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

_written by fenerh_
Maman Ammar

*Dedicated to*
Fiddousi mainasara

(¯`*•.¸,¤°´✿.｡.:*ք̲ʀօʄɨƈɨɛռȶ ɯʀɨȶɛʀֆ*.:｡.✿`°¤,¸.•*´¯)

ᴛʜɛ αвιℓιтү тσ gυι∂ε ιѕ тнε мσѕт ιмρσятαηт qυαℓιтү α ωяιтєя cαη нανε, ωε *_ρяσғιcιεηт ωяιтεя'ѕ αѕѕσcιαтιση_* ωιℓℓ ѕнαяε тнεѕε qυαℓιтιεѕ.

INSTAGRAM: https://www.instagram.com/proficient_writers/

FACEBOOK: https://mobile.facebook.com/groups/2455147078097572/

TWITTER: https://twitter.com/pro__writers?s=09

7&8

Maryam batasan wainar da ake toyawa ba saida Maman Amla ta zo gidan da kanta tana uban kuka,

Har kasa tasa guiwoyin ta tana rokon Maryam don Allah su bar mata mijin ta gaba daya yace idan bai samu Yasmin ba itama zata barmai gida,

Abin ya bama Aunty Maryam mamaki ganin ko a jikin Yasmin yasa tasan Akwai wata akasa tayi saurin kallon y'anda ta juya musu baya,

"Yasmin meke faruwa ? " AUNTY ki tanbaye ta ita data zo miki gida da kuka , kuma tasan banbacin karuwan gida dana bariki yau ba boka ba malam mujiya kwakwal war mijin mace idan tayi wasa kuma wallahi tayi gidan su,

Baki Maryam ta saki kafin ta lallashi Maman Amla ta tafi tareda kwantar mata da hankali bayan ta rakata "ki kyale Yasmin haka take kuma tanada wanda zata Aura d'an uwan mu ne kawai ta daga miki hankali ne,

Wani dadi taji tareda ba wa Aunty Maryam hakuri akan zagin ta datayi " kiyi hakuri Maman Auwal bazan kuma fitina dake ba insha Allahu,

Koda ta shigo gidan kasa ce mata komai tayi saidai idanu kawai don tasan halin y'ar kanwar tata idan ta matsa sai yanzu tace zatayi mata yaji gwara ta bari idan tayi niya zata fada mata da kanta,

*tushen labari*
2years back,

Tafe suke a kan hanyar su ta dawowa daga makaranta sanye suke a cikin fararen kaya da d'an karamin hijabi sai bakin low pass a lamar dai malaman jinya ne su

Kyawa wane su sosai duk da kana ganin su kasan yaya da k'anwa ne Amma Akwai shakuwa mai girma a tsakanin su

Saidai kanwar tafi yayar nesa ba kusa ba kuma kirar jikin su Akwai banbanci domin Maryam nada jiki kadan ita kuma Yasmin jikin ta d'an dai dai ne,

Zasuyi matukar burgeka idan kaga y'anda suke tafiyar su kamar wasu kawaye,
Motace tasha gaban su fara tas kirar Lexus sukayi saurin tsayawa cak,.

Fitowa yayi sanye cikin kakin shi yayi matukar yin kyau kanshi ba hula ya fara basu hakuri,

"Y'an mata Kuyi hakuri na tsayar da ku akan hanya, wani irin mugun kallo Yasmin ta watsa mai " kadai yi niyyar kashe mu Allah ne baiyi ba saboda ka ganka soja to Allah ya fika , ta furta tana mai murguda mai baki,

Saurin riko hannun ta Maryam tayi Alamar ya isa mana,  dariya yayi ya kalli Maryam "kibawa kawar mu ko kanwar muce hakuri naga tanada tsiwa,

Yana tsaye ya jingina da kofa sai kallon ta yakeyi Kamar ya hadiyeta ya Kara so ciki' yakamata kidaina boyemin komai baby kin hana ni kallon ki yanda nakeso me yasa?

"Nidai zantafi kaga kusan sha biyu,  riko ta yayi suka sakko bayan ya saka y'ar Riga, "muje inraka ki kafin indawo inyi wanka,

Karamin gyalenta ta yafa tareda daukar wayarta yana biye da ita Kamar ya riketa a gidan yakeji, har kofar gidan ya rakata tashige cikin sauri ta kulle kofar   sannan ya wuce,  saida ta leka dakin Aunty taga tana baccin ta hankali kwance, sannan ta wuce dakinta saida ta Kara kitmtsa kanta ta cire rigar shi mai she gen kamshin jikinshi Kamar yana wurin  ta sunsuna tareda lumshe ido ta ninke ta Ajiye a kayanta,

Katifa ta haye tareda janyo wayarta ta Dora saman kirjinta ta runtse idanun ta tana tuno Abinda ya faru moment ago  "MA karshen Y'an iska  Wallahi bata taba ganin iskanci irin nashi ba,

Wani irin yamm taji tsigar jikin ta na tashi da ta tuno da yanda yake lasar kirjinta Kamar wata Zuma kai yau ta hadu da namijin Zuma,

Shima MA haka ya kasance bayan yayi wanka ya  Kara dumama Abincin da ta dafamai ya zsuna yaci sosai badon yunwaba saidon hannun da ya girka shi saida ya wanke baki  kafin ya jefa sweet mai tsada da kamshi ya haye gado wayar shi ya janyo ya duba time,

Runtse idanu yayi yanajin Kamar yaje ya dawo da ita   murmushi yake na farinciki da Kuma shauki,  Kasa daurewa yayi ya Kira layinta,

Ba bata lokaci ta daga,  "hmm yace na dogon lokaci ya Kasa cewa komai sai fitar numfashin ta kawai yake saurara,

"Baby am speechless  bansan mezan fada ba,  kingama da zuciya ta kintafi da natsuwa ta I can't sleep  today kitayani hira kozan samu natsuwa,

Narkewa takarayi akan filo tareda kwanciya lub ta rike wayar gam Kamar shine,  "ina ganin komai baby Kamar indawo da hannun ago go baya nakeji,

"Ki soni don Allah  bazan iya hakuri da rashin kiba ke rabin jikina ce ki soni baby please kisoni, ya mai maita yafi cikin kwando,  tayi Ajiyar zuciya  tareda sharce hawaye masu zafi,

"Kadaina maganar so Aure zan..... "Please  kidaina zancen nan karki samun ciwon zuciya yanzu Aure Hmm in my foot Wallahi ba wannan limamin a kaduna da zai daura Aurenki da wani

babu shi,  ko abani ke ko indauke ki muyi rayuwar da kowa bazaiji dadinta ba ke tawa ce koma waye ya cire idon shi akan matata,

"D'an uwana ne yanada ikon Aurar dani ga koma waye bare shi karan kanshi ne zai.... Stop YASMIN  banason ji karkisa inyi Abinda banyi niyya ba,

Saida safe kawai yace tareda katse kiran zuciyar shi na zafi,  Wato YASMIN d'an uwanki kikeso har kike iya fada min Baki damu da halinda zuciya ta ke ciki ba,  ko Y'an biyu ne ku sai ya bar minke baby,  ya furta tareda yin jifa da wayar shi ya dafe kai,

A ranar Kasa bacci yayi har saida Asuba tayi  ya tashi yayi salla kafin yayi wanka yafita wurin da yake motsa jiki,
Ko kiranta baiyiba yau ya shirya motocin shi suka iso ya wuce bakin aiki cike da haiba da kwajini ga kaki na mugun karbar shi dole maza su girgiza idan ya fito

***************
Karfe goma YASMIN ta hada kayan ta domin ismail zai zo ya kaita gida duk ta damu da rashin kiranta da baiyi ba ga shi baxata iya kiranshi ba itama haka har ismail yazo suka wuce, saida suka kai kofar gidan su kafin ya fara yimata magana don yau komai bai ce mata ba tunda suka fito,
"Yasmin Akwai matsala fa,  ta kalle shi " mai  yafaru?  Ki shiga baba na ma na nan yazo,  zakiji koma Meye,

Saidai kisani ina sonki sosai YASMIN,  kanta ya d'aure  haka ta fita jikinta yayi sanyi ta shiga gidan shi ya kwashe mata kayan ta ya shiga dasu,

 Muryar baba Zango  tafara ji yanata ruwan fada domin shi yafi baban su zafi,  "Yaya bai isaba mu zai mayar mutanen banza?

"Mamuda babu ruwanka yarodai ya fadi ra ayinshi don haka dole mubi don iya biyayya yayi mana,
"Yaya Wallahi kai ke biye mai don haka babu ruwana bada miyau naba,

"Dama ai bamusa miyanka ba nidai don kana uban Yasmin ne nafada maka karkaji daga baya,

Gaishe su tayi bayan tayi sallama ta Kuma ji duk sharhin su Amma bata kamo bakin zaren ba, Ta gaida baban Zango yanda suke kiran kanin mahaifin nasu,

"Mama na kin iso? Ya maryamar da yarinyar ta, ? Lfy lau baba yasu innan Zango? Duk suna Lafiya mama na ismail ya shigo baba ya kirashi,

"Kaje ku gama magana a tsakanin ku Gobe insha Allahu zamu kammala komai kaji karka damu,

Dakin ta yasameta har ta cire hijabin jikinta zani ne single da Riga play tayi kyau sosai duk da ba make up tayi matukar haskawa,

Zama yayi tareda zuba mata ido "Fatima ya Kira real sunan ta yau tasan akwai magana, um ta zauna tareda zuba mai idanun ta tana sauraren shi,

"Kiyi hakuri da Abinda zanfada miki, yaja numfashi ya fara magana, " lokacin da narasa maryam mun hadu da wata yarinya a wurin Aikin mu gaskiya bazan boye miki ba naso Zainab sosai kafin mahaifin ta ya yi mata miji ya Auradda ita na dauki dangana a lokacin na Kuma y'arda da kaddara nasan Allah da ya hana ni Auren maryam da Zainab shi zai yaye mun soyayyar su cikin zuciya ta,

Cikin satin da ya wuce kwatsam na samu labarin a she sabodani taki yarda Sam tayi zaman Auren ta har mijin ya sauwake mata, ina wurin aiki ta sameni da kuka sosai akan idan ban Aure ta ba zata kashe kanta,

Maganar gaskiya YASMIN ina son Zainab Kuma nayi mata Alkawarin Aure, ina sonku duka don haka na fadawa baba zan hadaku baki daya ina fatan zaki bani Goyon baya kanwata,?

Tunda yafara maganar ta zuba Mai idanu tareda yimai wani irin mugun kallon Kama raina min wayau,

"Yaya kenan to ni na hakura kaje ka Aureta ba laifi Wallahi na yafe ka tafi kawai, wani irin kallon ta yayi "karkiyi mun haka YASMIN na kwallafa rai akanki don Allah karkisa in zaba tsakanin ku bazan iya barin kowacce ba a cikin ku,

"Wallahi sai ka Barni don bazan y'arda ka hadani da wata ba tun yanzu ni Yasmin kishiya a rana daya ina Wallahi kaje kawai na hakura,

Jiyo maganar su baba ne yasa sukayo waje,   da sauri,  mama ma tafito rike da  ludayi a hannu jin jiniya ta cika ko ina a Unguwar  baba ya sharce gumi ya kalli kanin shi,

Mamuda ina ganin barayin da akace suna Unguwar nan da gaskiya ne watannin baya sojoji Kamar yaki kullum cikin Unguwar nan kaga yau ma sundawo Allah ya jishe mu Alkhairi,.........
🖊️

*ai ina ganin tawagar su maman kids ne sukazo artabu ni nayi nan ba ruwana fan's love you All'*

*Matar soja*
[8/30, 2:56 PM] Feenerh Wrtr: PROFICIENT WRITERS ASSOCIATION

тнɛ αвιℓιтγ тσ gυι∂ɛ ιѕ тнɛ мσѕт ιмρσятαηт qυαℓιтγ  α ωяιтєя cαη нανɛ, ωɛ ρяσғιcιɛηт ωяιтєя's αѕѕσcιαтιση ωιℓℓ ѕнαяɛ тнɛѕɛ qυαℓιтιɛѕ.

INSTAGRAM: https://www.instagram.com/proficient_writers/

FACEBOOK: https://mobile.facebook.com'/groups/2455147078097572/

TWITTER: https://twitter.come m/pro__writers?s=09

🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
*BARIKI*
_Auren Soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

_written by FENERH_
Maman Ammar

*Dedicated to*
Fiddausi mainasara feby

*NA  sadaukar da wannan shafin gareku my people kungiya mai tarin Albarka da dumbin hadin kai proficient writer's ina Alfahari daku Allah yakara hada kanmu Allah  ya baku Ify mutane na Nabeela sarauniya tareda MAMAN Mamy SHALELEN proficient*
*Ammyn khyarat*
*Rukayyat Ikra*
*khadeja Auta*
*baba sadeq*
*nusee y'ar Amana*
*Ummu najma*
*Aisha Alto*
*Tareda kai bawan zage zagi Yusuf Indabo*

*jinjina agareku baki daya Allah  ya kiyaye  ku da ga sharrin mahassada ya Kara muku zakin hannu da kaifin kwakwal wa*

27&28

Wani irin trumbling cikinta yayi saboda tsabar tsorata ta zaro idanun ta waje tareda dafe kirji, "nashiga uku ta fada a fili  duk suka zuba mata ido'

"Meye najin tsoro YASMIN bayan gani anan,  ismail yafada ta zabga mai wani irin kallon bakasan me kakeyi ba ya nufi hanyar waje a rude domin tabbatar wa idanun ta,

Take mata baya su baba sukayi domin suma duk suna son ganin meke faruwa a wajen,  baba da y'ar butar shi ya fita a hannu ta Alwala,

Kusan suman tsaye tayi domin motocine sunkai kusan goma a jere sai katuwar hummer dake tsakiya duk kalar Army sauran duka hilux ne,

Tunfitowar ta ya hangota tareda  yin Ajiyar zuciya yana kare mata kallo tayi mai masifar kyau da shigar native wear din saidai ranshi yabaci data fito ba hijabi ga kirjinta sun kunburo sosai don Abinda yafara kallo kenan Ajikinta,

Kallon irin Yaran da yakwaso yayi yabasu umarnin komawa cikin motocin su don duk sunfito sungama zagaye wurin gaba daya da bindigogi,

Takowa yafarayi cikin takun girma da Kuma haiba lokacinda su baba ke tsaya suna kallon ina wa innan mala I kun duniyar zasuje?  baban Zango kam kanshi kawai ya leko daga waje,

Ta Riga ta gama sumewa da tsoro jin kawai tayi anrungume ta tareda yin Ajiyar zuciya,

Saurin dawowa tayi daga doguwar sumar tsayen da tayi ta yi saurin ja baya tareda sanya kukan rashin mafita musamman data kalli gefen da baba ke tsaye ga butar hannun shi ta fadi duk ta tsiyaye sai ismail da idanun shi suka juya tsabar kishin ganin wani kato rungume da Matar. Da zai Aura,

Kara matsota yayi kamar zai shige jikinta ga wani kallo da yake mata kamar zai lashe ta tsabar so "baby meyasa kika wuce baki fada min ba?

"Nifa da nayi fushine Kuma zuciyata taki y'arda da hakan ina bakin aiki naji bazan iya hakurin rashin kiba dole na koma gida nasamu Wai kinyo nan shiyasa na biyoki, "baby I can't indure nakasa daurewa indai akanki ne zan iya yin komai baby I can do anything bcous of you,

Ai YASMIN tashin hankalinda ta shiga bai misaltuwa yau tashiga uku da baba yau MA ya gama kasheta yau ta gama yawo,

Ai tuni su baba sunkoma cikin gida har ismail  ma sun barsu a wurin Sam tarasa madafa sai kukan da ya Kara kufce mata ta kalleshi hawaye share share ta ce "meyasa baka tunanin Abinda zaije ya dawo meyasa kake Abu ba tunani me yasa baka Abu cikin hankali?

Bata fuska yayi tareda zuba mata ido "oh nine bana tunani?  Naji idan akanki ne banda tunanin komai Kuma zan nuna miki banida tunani yanzu,

Kofar gidan ya nufa kai tsaye ya kutsa kai tareda sallama mama na nan rike da ludayinta tana sonjin labari ko wa ya Kasa cewa komai baba ne ya janyo kujerar roba zai zauna yaji sallama hade da kutso kai  ciki ba wani bata lokaci,  ai duka sun tsorata tuni baba ya mike tareda matsawa jiki na rawa baban Zango ne ya Amsa cikin rawar jiki tareda mika mai kujera,

"Bismillahi d'an nan zauna,
Dukawa yayi har kasa ya gaishe su tareda cire hula cikin bangirma ya fara kwasar gaisuwa mama tuni ta shige ciki
Kanta ya daure sosai yau me suke gani haka. Meye hadin su da wannan murdeden katon?

"Baba kuyi hakuri don Allah na shigo kai tsaye bayan nasan hakan bai dace ba,  Amma idan kunduba ta wani gefen ba wani Abu bane don nine surukin ku,

Baban zango yace "toto Amadu ne?  Baba yace aa bashi bane bari muji dai ko waye shi?
"Alhmdulillah  baba nine keson YASMIN mundade sosai da ita taki bani damar zuwa nan gidan ingabatar da kaina akan cewar kun zabamata miji batason ta bata muku rai taki bani hadin kai Amma Wallahi baba ku yarda dani YASMIN ni take so batason zabin ku kawai biyayya zatayi badon zuciyarta nasoba,

Yasmin data rabe gefe guda tuni ta Kara sautin kukanta  tareda fara magana "baba Wallahi ni sharri zai mun ni banason shi kawai so yake ya hadani daku,

Wani irin d'aci yaji a cikin zuciyar shi yanzu shi YASMIN zatace bataso kai tsaye? Ranshi yakai kololuwar baci ya mike tareda mikawa baba hannu "baba ni zantafi ina bakin aiki ne jiya na shigo kasar zanje tarbar rundunar da na wakilta a jaji,

Duka hannu suka bashi cike da girma mawa don sun san wanna mutum daga gani yataki wata tsiya ko a gidan soja,

Banda ismail da ya hade fuska tareda dauke kai cike da kunar zuciya,  kusa da ita ya matsa tareda yimata kallon zaki biya bashi ya fita ya barta da fargabar Abinda zai biyo baya,

Ba Wanda ya iya cewa komai saida sukaji karar jiniyar tafiyarsu baba ya zauna tareda sharce gumin da ta tsatsafo mai kamar ya shiga gidan brodi,

Baban Zango ma malum malum dinshi ya gyara tareda kallon YASMIN "zo nan mama na,  ya fada cikin natsuwa, jiki na rawa ta matso tareda tsugun nawa tana jiran hukunci,

"Saude' baba ya kirata,  ta fito tareda janyo kujerar mata ta zauna "malam Wai meke faruwa ne naganku kamar gidan mutuwa Nifa bangane ba?

"Toh ai nima saudatu bangane komai ba sai wadda tayi jagorar komai tayi mana bayani' wake nan?  "Yarki mana waye in banda YASMIN,

"Yaya mubi a hankali  muji komai a natse don ni koda yaron nan ke magana bangane komai ba, "toh mamuda idan banbi a hankali ba garaje zanyi?

"Yo ko zafi nayi ina zai kaini kana ganin y'anda ya zagaye mana unguwa kamar masu laifi kaduba ma kota har a katanga suna leko mu irin wannan bala I har ina?

"Mama na Meye wanna  ina kikeso ki jefa mu shikuma wanna don girman Allah ina kika tsinto shi?  Abarikin?  Ku Kuma haka Zaku kare a jajubo mana masifa ita maryam ta makale tace sai soja kema ji me kika kwaso,

"Mamuda daga gani wannan yaron bazaiyi mutunci ba,  don haka ka dauketa kawai ku wuce zango idan andaura Aure Sa dawo da mijinta

'Yaya ai wanna ba shawara mai kyau bace ai ko birnin sin zamuje banjin wannan yaro bazai biyomu ba Kuma ai nida natafi da ita ni kwabata zatayi ruwa,

"Kai samaila dama kanada zainabu sai ka hakura kawai da mama na,  "Aa mamuda banson Abinda kakeyi meyasa kakeson rabashi da y'ar uwar shi?

Tashi kawai baban Zango yayi ya saba malum malum tareda gyara zaman hula" toh nidai nafada muku inkuma dai nine waliyin Yasmin to ban daura mata Aure da kowa sai in wanna sojan yazo yace ya fasa zancen Auren ta don haka ni nayi gida Saude Allah bamu Alkhairi,

Ya wuce kawai batareda karawa waigowa ba, baba zuba mata ido kawai yayi kafin yace "tashi ki wuce ai ke kanki kinzama Abin tsoro Fatima Kuma nasan komai da sanin maryam zamu gauraya da ita,

Ciki ta wuce tarasa me ke mata dad'i tarasa madafa tarasa ina zata tsoma ranta tana hango bacin randa ya tafi dashi ya mugun tsaya mata a rai,

*****************

Bayan ya tashi aiki ya nufi gidan su dama Hajiya tasan da zuwan shi don haka ta shirya mai dish Kala Kala da kanta ta jera mai a dadduma ya iso da tawagar shi kamar gwamna,

Saida ya koshi ya fara bata hakurin rashin zuwan shi da wuri, "aa bakomai nasan aiki ne ya rikeka, riko hannun ta yayi cikin damuwa,

"Akwai magana kenan yau don nasan ka tun kana yaro daka rikeni hakan akwai babbar magana, "eh mama akwai, ina cikin damuwa , narasa mafita bansan yazanyi ba,?

"Tell me what to do kaina ya kulle, "kayimin bayani badai matsalar wurin aiki bace ko? "Akan yarinyar da nakeso ne, ya fara yimata bayanin komai akan YASMIN, Amma banda zancen Auren ta ya boye wannan,

Hamdala tafarayi kafin tace kai nagodewa Allah yau kaine ke zancen Aure? Lallai wannan yarinya ta ciri tuta Ashe soyayya ta da ita akwai Abinda Allah yaboye,

Kai nayi farin ciki sosai baba na Allah yasa rabonka ce, ya Amsa da Amen, yaushe zakuje nema min Auren ta?

"Banson garaje Ai gobe zankira kannin mahaifinka sai muyi magana inyaso sai mu tsara komai,

"Don Allah kar ya wuce jibi zuwan su 'ya ciro ATM ya mika mata gashi asiya komai da ake bukatar kaiwa akwai kudi sosai a ciki zasukai 2milion idan basu isa ba kifadamin inturo muku Wasu,

Sakin baki kawai Hajiya tayi tareda mamakin d'an nata yau ba mafarki takeyi ba kuwa? Muhammad ke son Aure kuma cikin sauri haka? Lallai mahakurci mawadaci

Allah ya ma wannan yarinya Albarka ita kam koda Asiri YASMIN tayima MA tana farin ciki da hakan kuma sai takara mata kudi takaiwa malamin,

Ma kuwa a gidan ya yi wanka ya shirya domin yanada daki na musamman, ya sallami yaranshi kafin ya fito cikin shigar manyan kaya shadda ce fara kar ya murza hula kamar wani sabon Ango ya fito yana zabga kamshi fadin haduwar da yayi bata bakine,

Waya ya dauka yakira tareda bada umarni kai tsaye,
"Mu hadu a Unguwar Dosa da wannan motar harma da kayan cikin duka,

Ya fita Hajiya nakara godewa Allah da Yau take ganin irin wannan farin ciki,

***************
Yasmin dai yau a daki ta wuni bayan tafiyar ismail , ya gama yi mata bori ko kallon shi batayi ba kuma tasan da bai bullo da zancen Auren Zainab ba bazata taba yimai hakan ba,

Yama raina mata hankali Wallahi kuma ta shirya ko baba zai Yanka ta bazata taba y'arda da Auren shi ba,

Baba kuwa yakasa cewa komai ya zubawa sarautar Allah ido yaga ta ina wannan rikici zai

kare?

Karfe takwas na dare YASMIN  ta samu tsalki ta sheko wanka tareda yin Alwala ta shiga dakinta ta shirya kanta tsab cikin wata rigar baccin ta guntuwa dai dai guiwa tareda daura zani ta Dora hijabi tareda tada salla,

Tana sallamewa baba ya kirata falon su ' ta zauna kamar wadda tayiwa sarki karya  gefe guda tareda dukar da kanta,

"Mama na kimun bayani ina sauraren ki " me kikeso ki fadamin?  Kema bazaki Auri d'an uwanki ba kike nufi?  Dake da y'ar uwarki kun gama watsa min tsarina baki daya ko,

"Haba malam yakamata ka barwa Allah  wannan  lamari ita maryam da kake magana Ina zamukai wa innan rabon kana ganin cikin shekara biyu Yara biyu ai sai mu yarda da yin ubangiji,

"Haka ne saudatu yanzu kina so ki fadamin bansan Allah keyin komai ba kome?  "Toto yanzu nasan komai ma da sanin ki sukeyi tunda ba danginki bane shiyasa kike zuge ya'yan ki su ki Auren shi ko?

"Haba malam ya zaka fadi haka bayan kasan irin y'anda na reni ismail da hannu na kamar ni na haifeshi bai dace wannan kalma tafito daga bakinka ba,

Toh kusani keda Yasmin indai nine mahaifin ta to bazata taba Auren wannan yaron mara tarbiya ba,  ya mike fuu ya fita,

YASMIN tashiga tashin hankali najin yau saboda ita iyayen ta na misayar yawu,  abinda bata taba jiba tsawon rayuwar su,
Kuka taji ya kwace mata mama ta kalleta,

"Toh Allah  ya biyaku ya'yan Albarka Wato dai kullum sai kunja mun magana idan zancen Auren ku yataso haka y'ar uwarki tayi kema gashi Abu yazo gab shine kika bullo da naki iya she gen,

"Kuyi kokari Kuyi Auren ku inda kukeso ni kuma sai ku kashe min nawa kunji nagode muku, itama maryam yanzu zankirata inji don nasan da sanin ta komai ya faru,

Kukan tane ya Kara sauti tareda girgiza kai cikin Kuka" mama don Allah kiyi hakuri Wallahi ni ban turoshi ba kuma Aunty batasan komai akai ba,  ni wallahi na yarda da Auren ya'yan karkuyi fada akaina don Allah,

.
"Tashi kije ni nagama magana kuma,  tashi tayi kamar wadda kwai   yafashe mata ta nufi dakinta,

Baba na fita yaci karo da motoci sababbi dal a kofar gidan daya fara sai kuma ja y'ar Kara ma mai shegen kyau kirar Volvo sabuwar fitowa ya tsaya cak tareda makakin ko suwaye a ciki,

Fitowa MA yayi daga cikin farar ga kayan jikin shi farare yayi mugun haduwa ga kwarjini da haiba da ya cika ko Ina,  baba bai gane shiba saida ya matso tareda mika Mai hannu,

"Salamu alaikum baba barka da dare' baba ya Amsa cikeda ganin girman yaron yace wa kake nema yaro?

"YASMIN   nine dazu nazo da safe "toto nagane soja ko?  "Eh baba sunana Muhammad Abdullah,  to Sannu muhammadu bismillah shigo,

Tana kwance ta Dora wayar ta saman kirjinta  tana tunanin rashin kiranta da yayi yau kardai fushi yakeyi da ita?

Kamshin jikinshi tajiyo tun shigowar shi taji domin turaren nada mugun kamshin da da mutum ya doso zakasan mutum na zuwa,

Wani irin faduwa gabanta yayi kardai shine ya dawo?  Tashiga uku,   kuwa MA zai jefa ta a damuwa,

Kiran baba  yasa tayi saurin zabura cikin tsoro batareda ta tsaya daukar hijabi ba ta fito ta gyara sumar ta ta nannade ta sai zanin da ta Dora a kugunta saman rigar baccin ta mai guntun hannu Mai dauke da hoton  frozen a jiki,

Kirjin nan na MA ya fito da kyau  gwanin burgewa  saida tasawo kanta wajen ta ganshi cikinta ya Kara d'urar ruwa,
Idanu ta zuba mishi cikeda tsoro gashi wannan ne karon farko data fara ganin shi cikin shigar manyan kaya yayi mata kyau sosai kamar Ango,

"Kije ki fito mana da kujera kintsaya kina kallon mutum kamar zaki cinyeshi,  saida taji kunya tareda shigewa dakin   mama tafito da kujerun roba guda biyu ta ajiye jikinta narawa  ta koma daki cikin sauri,

Tunda tafito ya zuba mata ido kamar ya cinyeta yakeji  tayi mugun yimai kyau gashi kanta ba dankwali yaga y'anda sirrin sumar ta yafito

Wani iri yakeji kamar ya bita cikin dakin ya turmushe ta yakeji,....... 🖊️

*hmm fan's yau hakuri zakuyi dani wallahi nayi typing ya goge  tas by mistake don haka Kuyi manage gobe zan wanke muku zuciya da yardar Allah*

*Matar soja*
[8/30, 2:56 PM] Feenerh Wrtr: 🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
*BARIKI*

_Auren Soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

_written by FENERH_
Maman Ammar

*Dedicated to*
Fiddausi mainasara feby

*Ina son ku ina kaunar ki kuna faranta min ina matukar jinjina muku Allah yakara dankon zumunci yakaro kauna my real fan's AISHA BABAYO,  HUSSY ALI MAMAN ABDULLAH UMMI ZARIA,  MOMYN KIDS,  MOM HUSNAH,* _WA INDA MA BANKIRA BA ZAKUJINI A NEXT PAGE,   AP NAYI TUYA NA MANCE DA ALBASA AISHA DAHIRU UWAR GAYYA MAJI D'ADIN M. A JINJINAR BANGIRMA UWAR DAKIN YASMIN ALLAH YABAR KAUNA DA AMANA_

29&30

Yaudai taga Rayuwa,  kirjin ta har wani irin tsalle yakeyi kamar zaifito tsabar tsoro "MA zai kasheta kwanan ta bai kare ba,

"Bari inkira mahaifiyar ta ku gaisa,  baba ya fada tareda mikewa ya shiga dakin mama,  wayar shi ya janyo tareda tura mata text  _kifito kefa nazo gani kin wani shige ciki kinbarni da yunwar idanu_

Saurin dubawa tayi tareda cewa "naboni yau,  kasa motsi tayi ta koma lafewa a katifar ya kuma turo mata wani   _wallahi zan shigo ciki kuma sai nayi Abinda nakeso zanfito inbarki da kunya kinsan ni bansan Abinda ya dace ba_

Zabura tayi ta mike cikin sauri ta saka hijabin ta tareda fitowa,  wani irin kallo yake binta dashi

tundaga sama Har kasa ya matse fuska "me kike boyemin?

Marai raice fuska tayi tareda  matsowa kadan" don Allah me kazoyi?  "Bansani ba kicire hijabin sai inbaki Amsa,

"Don Allah muh'd ka rufamin Asiri ka bari inji da tashin hankalin da ka jefani,  "banajinki saikin cire wannan hijab din sai muyi maganar,

Cikin sauri ta koma dakin domin jiyo maganar su baba Zasu fito,  gyara zaman shi yayi da kyau ya zubawa fuskar mama ido cike da farin cikin ganin inda YASMIN din shi ta gado kyau da fari,

Ya zame kasa tareda cire hula cikin bada girma irin na soja "mama barka da dare,  ta Amsa cikin farin ciki da natsuwa bayan ta d'an zauna kan karamar kujera "ya aiki,?  Yace Alhmdulillah, "to Allah ya tsare ku ya kuma kare ku,  Amen Amen nagode mama,

Yaji dadin Addu ar ta har cikin zuciyar shi ga Matar nada kwarjini da kamala ga tsafta don tunda ya shigo gidan karan farko yasan  Matar gidan nada matukar tsafa don sumintin tsakar gidansu tsab Abu zai fadi ka dauka ka jefa a baki,

Saida suka gama gaisawa ta mike tareda cewa" kaga Yasmin din?  "Aa ya fada cikin sauri "mama tagan ni Amma taki fitowa kuma tasan saboda ita nazo,  mama don Allah kiyi mata magana tana wahalar dani bayan itama fa tana sona sosai,

Wata irin kunya ce ta rufe mama naganin y'anda yake mata magana kamar wani Kara min yaro, shikuma harga Allah  jinta yake kamar hajiyar shi,

Ya koma kan kujera ya zauna da kyau tareda dukar da kanshi kadan ya kalli baba yasan baba baya ra ayin shi sarai don yasan yanda Akayi akan Auren maryam don haka yasa shi nuna iko kota karfin mulki sai Anbashi Yasmin sunyi Aure su sami jikokin sunnah ko kuma su tarbi jikokin soyayya,

"Toh Nima bari inshiga ciki sai tafito Kuyi magana,  baba yayi magana,  "eh dama baba inaso

infada maka jibi iyaye na zasuzo nan sukawo kudin gaisuwa,

Tsit baba yayi na d'an lokaci kafin yace "tom muhammadu nidai banine mad'aurin Auren Fatima ba Amma gobe zan Kira kanin nawa infada mai sai kuyi maganar komai a tsakanin ku,

Kara dukowa yayi kadan yayi godiya kafin ya koma mazaunin shi, shigewa sukayi ciki tareda barin shi a wurin bayan baba ya kwala wa Yasmin Kira ' kuryar daki suka shige domin su tattauna magana atsakanin su,

Alokacin ya mike zuruf ya nufi kofar dakin nata cikin hanzari,

Dai dai tana canja kayan jikinta domin rufawa kanta a siri domin tasan bazata iya fita da kayan jikinta batareda hijabi ba kuma a tsakar gidansu,

Riga da sket ne ta fito dashi na material ja domin canjawa, bata taba tunanin MA zai shigo cikin dakin ba shiyasa ta tube daga ita sai pant da bra ta saka sket din ko guiwar ta baikai ba ya shigo,
Da yake tabawa kofar baya yasa yaja ya tokare tareda nannade hannun shi a kirjinshi,

Wani irin trumbling marar shi tayi naganin ta a tsaye sanye da pant da bra farare duk da bata juyoba he can see ha awesome hips dai dai jikinta masu daukar hankali ga bombom dinta wow,

Ai tana zuge sket din ta janyo rigar yayi wuf ya karasa kusa da ita tareda rungume ta ta baya ya Dora hannayen shi akan westdinta tareda sauko da kanshi daidai wuyanta ya Dora mata kiss a wuyan,

Lamarin MA yadai na bata mamaki saidai tsoro don haka koda taji hannun mutum tasan shine, cikin tsoro tayi saurin juyowa bayan ya sauke mata hot kiss a wuya,

Tama manta da ba Riga a jikinta ta zuba Mai ido jikinta NA rawa tareda dafe bakinta da hannu cikin rasa mafita,

"Wai meyasa kakemun hakane?  Don Allah kafita kajirani ina zuwa please  kaje waje karsu mama su fito suganka muh'd ka rufa min Asiri don darajar iyayenka,

Aikin banza domin shi yayi nisa tunda ya Dora idanun shi akan boosty boob dinta ya rikice idanun shi suka juya Kala  yayi wani  irin kalar tausayi tareda kokarin rikota taja baya da sauri tareda kare kirjinta da rigar, cikin tsoron Abinda tasan zai iya yi,

Baya baya yakoma ya fada kan katuwar katifar tata mai cike da kamshin ta mai dadin gaske ya runtse idanun shi tareda kokarin natsa kanshi,

Gaskiya yau yayi namijin kokari DA bai yi striping  dinta a cikin gidansu ba don ta mugun kunnashi sosai   d'auriya iya d'auriya yau yayi,

Ganin y'anda ya runtse idanun shi yasa ta yi saurin saka rigar tareda janyo d'an karamin mayafin ta ta yafa ta matsa kadan kusa dashi' katashi mutafi don Allah  karsu mama sufita inshiga uku,

Bude idanun shi yayi tareda zuba mata su cikeda shaukin zazzafar soyayyar ta "love you baby more and more,  ya fada cikin kwantar da murya kafin yabi dakin nata da kallo,

Bayan katifar sai walldrp mai kofa biyu da mirror dinta dake dauke da turaruka da kayan shafa gefe data akwatunan tane guda shida pink masu kyau domin su ba talakawa bane don duk Wanda keda maganin lalurar yau da gobe ya wuce talaka,  don Albashin baba ya ishesu suji dad'i har ma suyiwa Y'an Uwa Alheri,

Kan bangon dakin ya sauke idanun shi dake dauke da hotunan su Kala Kala ita da maryam tundaga na kuruciya har zuwa yanzu,

Murmushi yayi mai kyau ganin wani hoto nata tana sanye da kayan ta na nurse tayi masifar kyau,  yatashi tsaye tareda kakkafe shaddar shi data fara squzing ya nufi wurin tareda ciro hoton ya rungume yasaka hannu ya ciro wani datake sanye da wata doguwar Riga pink kamar babie kanta da crown daga gani na wani occasion ne,

Kallon shi kawai takeyi,  ga kamshin shi yacika dakin nata tab ya matso gab da ita" tank's for this beautiful pictures muje inbaki tsarabarki tana waje,

Bai jira komai ba ya fita tabi bayanshi cikin sauri domin ganin ko ba Wanda ya fito,  tayi Ajiyar zuciya har suka kai kofar gidan bakowa,

Yana rungume da hotunan kamar kwai saida ya bude gaban motar ya ajiyesu kafin ya dawo wurinta,

Baki Yasmin ta saki wurin kallon motar da tagani y'ar karama tayi mugun yi mata kyau tana sheki duk da dare ne akwai d'an hasken wutar nefa a Unguwar kota ina,

Matsowa yayi tareda sanya hannun shi cikin pocket din Aljihun shi ya d'an rankwafo ta fuskar ta kadan "hope you like it?  Idan kuma batayi ba a canjo miki'

Wani irin kallon shi tayi cikin tsoro,  " me kake nufi?  "Motarki ce akwai tsarabarki ma a ciki ya bude motar tareda bude bayan boot din ya    Wasu irin akwatuna ne guda uku Kala daban daban manya duka girma daya blue red da kuma purple ya fito dasu kamar bakomai a ciki  ya dauki  biyu ya shiga dasu cikin tsakar gidan  kafin yadawo ya dauki dayar ya shiga da ita,

Takasa cewa komai saida ya dawo yace "zomuyi magana kai tsaye ya riko hannun ta suka shiga gaban motar,

Juyowa yayi dakyau ya dafe kumatun shi ya zuba mata ido "baby nasan kinfi karfin wannan y'ar kyautar Amma kiyi hakuri zamuje kasuwa insiya miki komai ya d'anka mata key din motar  a tafin hannun ta,

Gaba daya tarasa nayi ita yanzu ta ina zata fara tasan kotace mai bazata karba ba Aikin banza zatayi don ta lura dashi mutum ne mai ra ayin rikyau idan yayi niyyar Abu ba Wanda ya isa ya hana shi,  don haka kallo kawai take binshi dashi,

Saida ya bata key din ne tayi saurin girgiza kai" aa nidai ka bar ni banason mota ta ina zanshiga da wannan key din incewa su baba me?   Bayan kayan da kashiga dasu nidai don Allah kabari ingama dasu Lafiya,

"Hhhh yayi dariya sannan yace "tom idan bakyaso sai ki yi sadaka nidai nakawo kuma bazan koma dasu ba don kiji,

Matsowa yayi tareda riko hannun ta ya kashe mata ido,  "baby kinfa dauki alhakina yau,  kiri kiri Kinyi min kwalelen Abin kallo na inaji ina ganin su kin hana ni morewa,

"Tun fa shekaran jiya rabon da in rage ruwan Marana kinga yau Kim in wani Abu Inba hakaba yau bazan iya bacci ba,

Kallon nariga nasaba da halinka kawai takemai kafin tayi magana,  "wannan ne soyayyar taka da kake fadar kanamun?

"Sosai baby da banasonki da na danne ki wallahi na rabaki da wannan y'anar dakike yanga da ita tuntuni,  "dama kasaba yiwa yaran mutane '

"Point of correction,  yaran dake ra ayi dai ko yanzu zuby najirana a gidana zanje ta ragemin wannan ruwan dole yau sai sun zuba zan iya bacci ya fada tareda shafo marar shi,

Cikin takaici ta bude motar ta fita,  yana kiranta ta shige abinta Allah yagani tana tareda aiki don KO Auren MA tayi to sai tasamu hawan jini domin shi mutum ne mai yin Abinda yaga dama ba Wanda ya isa ya hanashi,

Fitowa yayi tareda rufe mata motar ya shigo gidan bai koma takanta ba ya ajiye key din akan akwatunan ganin karfe goma harda rabi yasa ya wuce gidan shi,

*********************

Tundosowar shi kofar gate din ya ga motar zuby a wurin ya matse fuska kafin ya shiga cikin gidan,    tundaga falon yaci karo da Emanuel,

Yafara yimai ruwan bala'i akan yadawo zai fara barin mai gida kamar gidan karuwai ko,  ya fara bashi hakuri jiki na rawa "Oga sory sir I no go do one again,  ys fada yana sarawa kamar koda yaushe,

Dakin dake kasan falon ya nufa tareda kullewa gam da key ya fada kan katon gadon ya kife tareda runtse idanun yana tuno Abincin zuciyar shi Yasmin,

Kasa daurewa yayi ya kirata,  lokacin tana kwance cike da kishin Kila yana can wurin karuwan nashi har Wasu hawaye takeyi na bakin ciki taga Kiran shi,

Ba jan Aji ta dauka domin tanason tasan halin da yake ciki,  "babyyyyyy ya furta yana nishi "ad'aura min Aure zuwa jibi kar inkara lalacewa,  I can't sleep Marana babyyy,  ya fada cike da bukatuwa tareda sauke mata huci mai zafi a kunne,

Ajiyar zuciya kawai ta sauke tareda fara magana,  "kana ina ne yanzu?  "Ina gida na a BARIKI, "kaida waye agidan?  "Nida zuby ne tana sama ni kuma ina kasa  nazo nasame ta agidan,

Wani kululu ne ya tokareta yanzu don iskancin MA yake fada mata shida wata ne a gidan? Tsaki taja mai karfi,   ya dago da kanshi daga kwancen "baby ina fatan tsakin ba nawa bane?

Banza tayi mai "Hmm you must pay that,  ya katse Kiran,  minti biyu ya kuma kiranta again "karki kuma yi koda badani kike ba banaso zan shigo gidan da safe injira baban mu da zai mana Aure,

Ajiyar zuciya tayi tareda rike wayar gam a kunne. "No matter how he is she love him to the

extend da bata taba iya fushi dashi  tana jin son MA kamar fitar numfashin ta,

"Baby barci kikeji?  "Aa tace cikin sauri tareda Kara rungume wayar kamar shi  ta rungume "kaifa bacci kakeji?  "Aini idan ina tareda ke banajin bacci baby banki mukai safe ba ahaka,

Tuni ta baje idanun ta  bude ido tarai domin zataso su kwana tana jin shi kar yaje wurin zuby don jitake ina ma tana barikin yau sai takoreta a gidan,  ko yanzu jitake kamar tace ya koreta Amma ita a wa?

Haka suka kusan kwana yana zuba mata sambatu har karfe hudun Asuba kafin ya katse "baby bari inje inyi wanka inyi salla kafin akira asuba  kinsani zubarda ruwa jin numfashin ki kawai "baby kema kinajin me nakeji kema kin yi yo yo?  Kit ta katse Kiran tana dariyar halin muh'd , shidai baruwan shi saidai inbaiyi niyayyar magana ba duk abinda yafito abakin shi sai ya fada,

Saida tayi Alwala tafara nafila tareda yin Adduar neman zabin Alkhairi a rayuwar ta kafin akira salla tayi ta d'an  karanta qur ani kadan tarufe ta haye katifa domin biyan bashi don yau gaskiya saidai mama tayi mata hakuri,  Aikin  gidan nan saita tashi,

Saidai karfe shida baba ya doki kofar ta ta zabura ta mike idanun ta cike da bacci ta fito waje tana hada Han ya,  idanun ta a waje ganin baba ya zubawa akwatuna ido,  mama na gefe rike da carbi,

"Fatima wa innan kayan fa ga mota nagani awaje tun jiya ga kuma makulli a anan?  Bakin ta na rawa tafara in ina" baba shi ya kawo min Wai tsaraba,

"Harda mota?  Inji baba cikin karaji,  Amma y'ar nan me kikeso kimayar dani ne karamin mutum?  Aurenki saura kwana uku ki karbi kayan wani kato haka akeyi me kika bashi zai miki irin wannan kyauta haka harda motar da har in mutu kudin Albashina bazasu taba siyan rabin

taba,

Kuka tafarayi najin maganar baba,  mama tace "malam kabi a hankali idan mamuda yazo sai asan nayi KO ka bashi hakuri kawai yadai na zuwa,

Kallon ta yayi da kyau "lallai Saude to bari mamuda yazo muji shi zaisan nayi tunda shine uban yarinya,  "aa ai kai zakayi wani Abu akai kafin shi yazo saika jamai layi,

"Anki aja layin kifita idona saudatu inkinaso mu shirya kema ai uwarta ce kija mai layin kuma ki binciki y'ar ki  sarai nidai nafada miki kuma itama maryam ina nan yau ina jiranta,

Ya wuce ciki fuuu,  mama ta kalleta "saiki kwashe kayan kishigo dasu ciki ai kin kyauta,   jikinta na rawa ta Sa hannu ta ja daya dakyar take janta ta shiga da ita tana mamakin yanda taga ya dagasu kamar empty Ashe uban nauyi garesu,

 Baccin  da bata koma ba kenan ta fara Aikin gida saida ta shirya break takai dakin tajera a falon su mama tasame su suna dramar da ta kun no gidan yanzu na zancen MA,  baba yasa ta bude akwatunan duka kayane English wears da takalma masu tsada sai zannuwa masu tsada da jakun kuna da sarkoki harda gwal da passion masu aji ga inter wears dai dai size dinta kusan kowane dozen yakai biyar,

Idanun ta awaje lallai MA d'an iskan ciki da waje ne na bugawa a calendar,  baba yakasa magana ya kalleta kwashe kikai dakin ki ai nakine tarkacen,

Haka ta kuma kwashe su baba ya karbi makullin motar yace bari mamuda yazo zanbashi ya mayar mai da ita,  "hmm kawai mama tace,

Karfe goma ismail ya iso da jerin saitin akwatunan shi har saiti biyu na yayi ya shigo dasu tsakar gidan da taimakon Abokin shi suka baje su a wurin kafin ya leka falon mama yace tazo tagani in akwai Abinda baiyi ba ya karo  natane Dana zainab,

Mama kallon kayan kawai tayi tana tunanin gwaramar dazata biyo baya tasa Albarka tareda cewa "Allah dai ya muku zabin Alkhairi ismail in Yasmin rabonka ce Allah yasa ayi damu in kuma ba rabonka bace Allah yabaka dangana,.......... 🖊️

Kujira sabon post zuwa dare mutane na insha Allah,

*lamarin nan yafi karfi na my fan's  kuyi Addu ar sauki don akwai gwarama nake gani gaba akwai kura*

*Matar Soja*
[8/30, 2:56 PM] Feenerh Wrtr: PROFICIENT WRITERS ASSOCIATION

тнɛ αвιℓιту тσ gυι∂ɛ ιs тнɛ мσsт ιмρσятαηт qυαℓιту α ωяιтєя cαη нανɛ, ωɛ ρяσғιcιɛηт ωяιтєя's αssσcιαтιση ωιℓℓ sнαяɛ тнɛsɛ qυαℓιтιɛs.

INSTAGRAM: https://www.instagram.com/proficient_writers/

FACEBOOK: https://mobile.facebook.com'/groups/2455147078097572/

TWITTER: https://twitter.come m/pro__writers?s=09

🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
*BARIKI*
_Auren Soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

_written by FENERH_
Maman Ammar

*Dedicated to*
Fiddausi mainasara feby

31&32

Yasmin na daki tana maida bacci batasan ma me yakeyi ba a tsakar gidan,  karfe sha daya baban zango ya iso Shima,  ya tarar da kayan a nan,

Bayan sun gama gaisawa da mama ya zauna takawo mai Abin kari yanaci yana kallon kayan saida yayi kat ya fara tanbayar yayan shi,

"Saude ina Yaya?  "Malam ya fita yanzu  zai dawo baiyi nisa ba,  "wa innan kayan zainabu ne ko?  "Eh da na Yasmin,  "waya kawosu?  Yafada cike da rainin hankali,  "na ismail ne,  "Wato duk maganar da mukayi dashi baiji ba KO?

"Mahmud Kayi mai Addu ar zabin Allah kawai kubi komai Ahankali,  "to nidai Yaya yakirani akan maganar soja kuma nidai Saude inkinga ba ayiba to bana numfashi,

Ko kuma shi yace bayaso ai ni tunda ismail yakawo maganar Auren Zainabu naji hadin yafita araina  banason Auren shi da mama na nafison tayi Auren hutawa ba gidan kishiya ba,

Dariya mama tayi "Au shiyasa Kuka kasa Aure kaida malam?  "Ai kune Kuka hanamu keda hinde  "aa karkuyi mana sharri baruwan mu mukan,

Rahar su suka taba kafin dawowar baba suka zauna domin neman mafita "ai ni Yaya inada mafita don gobe su liman zasuzo mu Amshi kayan Aure shi yaje can yakai ma zainabu wa innan duk mun yafe,

"Mamuda kana Abu kamar mace wallahi nidai ismail  zanbawa Aure "to mu zuba muga uban ya' Sallamar MA ce ta tsayar dasu ya shigo cikin haiba sanye da kakin nashi green kanshi ba hula yayi matukar fitowa kayan na mugun Amsar shi,

Suka gaisa mama ta kawo wata kujera ya zauna,  baban zango yace "Saude karo mana kosan idan akwai da kokon,  ta ce  to ta shiga kitchen tareda hado wa kan tray cikin jug mai  kyau ta dakko kular kosan hade da cup da kuma  robar sugar ta Ajiye musu tareda komawa daki,

Domin basu  wuri su tattauna,

Baban Zango ya ce "suriki na bismillah ga Abin karya wa ko bazaka iya cin Abincin mu ba,? "Noo baba ai inason gargajiya sosai ya dauki karamin kofi ya tsiyaya kokon tareda Sa sugar kadan domin ciwon shi,

Yasaki jiki dasu sosai yanasha yana zuba musu hira  har baba dake d'ari d'ari yasaki jiki baban zango daman shi akwai son shafta,  saida yaci sosai don kosan Yamai dad'i yayi hamdala daman dokin ganin Yasmin bai Sa ya tsaya karya waba daga office kawai ya gudo,  gashi baiji ko motsinta ba Anya ma tana gidan,?

"Toh muhammadu kake ko?  Inji baban Zango  yace "Alhmdulillah  naji dadin da kakeson jinin mu kuma Kayi mutunci daka zo kai tsaye ka same mu kuma indai nine mad'aurin   Auren mama na to nabaka gobe muna jiran zuwan manya,

Saidai kuma wani hanzari ba gudu ba kasan da zancen Aurenta da Dan uwanta to yanzu dai yasamu wata kaga iyaye mata muke jira yanzu sukai akwati in Allah yakai mu jibi a daura Aure,

Toh yanzu dai naku maganar Auren sai manyanka sunzo sai muga kamar wata nawa zamu sa, yayi saurin kallon baban dake magana

"A gaskiya inaso a daura da namu jibin ni basai kun tsaya wani shi shiri ba tunda dama a shirye kuke da Auren don haka don Allah Karku daga a barshi a hakan,

Baba kallon shi kawai yakeyi y'anda ya ke rokon a daura mai Aure jibi sai kace y'ar tsana ko kuma mara Gata,

Baban zango yace "ka bar magana sai su manyanka sunzo wannan tsakanin mune zamu tsara komai,

Shiru kawai baba yayi yana ganin zamani agabansu yaro yazo yana zaben ranar Auren shi,
MA shiru kawai yayi bai gamsu da wani zancen daga Aure ba, don bazai haifarda da Mai idoba don gaskiya hakurin shi yakai bango,

Kamar a mafarki Yasmin take jiyo maganar shi atsakar gidan tareda kamshin shi mai rikitarwa duk da haryanzu katifar ta na kamshin jikinshi Amma Wanda takeji tasan fresh ne,  ta zabura tareda lekawa ta window shine da gaske tana mam akin y'anda ya zage sai hira sukeyi kamar sundade da sanin juna gashi harda kofin koko a gaban shi lallai MA baida ta I do,

Kamar yasan tana kallon shi yakalli dai dai window  sukayi ido biyu ya kashe mata ido tareda bata wani shegen murmushi,  tayi saurin sakin labulen ta koma tana dafe kirji kawai tagama sallama wa MA,

Wayar shi ya danna  ya tura mata sako _"kifito ko intashi inshigo kinsan zan iya_
Ai ba wasting time ta sako  guntun hijabi akan kayan doguwar rigar dake jikinta kana kallon ta kasan bacci ta tashi,

Tafito kamar mara gaskiya ta gaida su baba batareda ta kalleshi ba  baban Zango yace "Aa mama na dama kina ciki a she?  "Eh baba bacci nakeyi,  "to y'ar Albarka kwashe kayan nan ki shiga dasu mungama,

Tunda ta fito ya zarga mata na mujiya tareda yin Ajiyar zuciya yana jin wani irin nishadi Allah yasa su baba su yarda su mallaka mai wannan halitta ko zai samu natsuwa shidai gaskiya ya mutu kan kaunar Yasmin,

Kasa fitowa tayi daga kitchen din tarasa Abinyi idanun shi sunyi mata kaifi sosai,  jin yana musu sallama yasa tayi Ajiyar zuciya  tareda hamdala,

Saidai yana fita ya dsnna mata Kira ta daga ba bata lokaci  yace "ki fito inganki ina waje,

Zuru tayi Rashin mafita yasa ta fito sum sum ta fice, a jikin motar shi ya dogare tareda zubawa kofar gidan ido,

Tsayawa tayi daga nesa ta kasa cewa komai,  "good morning madam Muhammad Abdullah, murmushi tayi mai kayatar wa kafin ta Gaishe shi yace ki motso ko inzo indauke ki,

Karasowa tayi cikin takunta mai ban sha awa  "wow masha  Allah  yafada yana kallon ta kamar ya rungumota yakeji,

"Baby Hajiya tayi farin ciki sosai da maganar Auren nan Hajiya ta na sonki sosai,  "Nima ina kaunar ta sosai tunfarko ta nuna tana kaunata don haka Nima dole insota,  wani irin dad'i yaji har cikin zuciyar shi yace hmm "Maison Uwa ya so d'an ta,

Kallon shi tayi kafin tace "ai dole ne kodan Alharkar Uwa a so d'an,  zaro ido yayi "yanzu ke bakya sona sai don Albarkar Hajiya?

"Ina sonk... Tayi saurin rufe bakinta ya yi dariya sosai "no need baby nasani kina sona ko baki fada ba and I love you too much baby,

Kisa baki a mana Aure jibi kar in baki ciki a gida don nakusa aika aika Wallahi,   Wai meyasa bakajin kunya ne?

"Wane yarene kunya kuma?  Ya fada tareda rike kuma tunshi tace nidai banajin wannan yaren,

Isowar Aunty maryam tareda mijin ta yasa Yasmin ta shige gida da gudu cike da kunya tabar shi,  Ahmad na fitowa ya Sara ma ogan shi cikin girma mawa,

"Oga a she nan kazo?  "Eh ina nan baby ta hana ni zuwa aiki,   dariya kawai Ahmad yayi domin shikan shi baisan komai ba saida maryam tafada mai jiya,  bayan baba ya kirata ya wanke ta tas,

Gaida maryam yayi cikin bata girma $Sannu Auntyn mu kunya ta rufeta domin tunda take bata taba haduwa da ogan mijin nata face to face ba sai yau,
Lallai dole mata surika rububin shi gashi duk iskancin da suke fada nashi yau yadawo yana son kanwar ta,

Shigewa tayi tabarsu  rike da y'ar ta a hannu da sallama ta shiga cike kuma da farin ciki domin tunda tabar gidan bata kuma zuwa ba saboda baba sai yau da rikicin na Yasmin ya taso,

Dakin maman ta tashiga cikeda farin ciki mama ma tayi murnar ganin ta ta karbi NANA Aisha "mama ina d'an rigimar ki ko baya damun ki?  "Aa ba ruwan shi sunfita da malam yanzu,

Bayan ta natsa sungama d'an zantawa da mama sannan ta mike domin samun Yasmin,
Tana shiga dakin ta ce "toh kingama gudun munafuka?  Wallahi Yasmin kin gama binne ni da raina a ce muna tare dake ki kasa fada min komai kinja baba ya warwareni jiya Banji ba bangani ba?

Dariya kawai tayi tasan ba gaskiya,  zama tayi gefen ta domin jin labari,  "yaushe aka kulla?  Ina BARIKI Bansani ba wai yaushe kukayi wannan sabon Yasmin?

"Gaskiya kin shammace ni ace muna tare ko Alama bangani ba ina tsine mai da kikeyi?
Yaushe kema Yama zuciyar ki Gini? "Kai Aunty wa innan tanbayoyi haka,?

"Dole kice tanbayoyi bayan kin gama min boyo Ashe shiyasa ya so ya kulle min miji lokacin da kuke soyayya da Oga umar Ashe kishine yasa yake ma baban Auwal warning oh kice ba abanza ba umar ya fita hanyar ki Oga na ciki,

"Hmm Yasmin to be sincere nayi farin ciki sosai wallahi ki daina maganar mata mafi yawan maza yanzu suna bin matan waje Wanda ya bayyana nashi ne kawai ake gani,  bare Oga MA kowa yasan mafi yawan su suke kawo kansu,

"Yasmin koda yana bi ke zaki gyara Abinki,  nayi farin ciki A ce kanwata zata Auri Oga MA  da ko wace mace ke burin samu,  naji Wai har zaki fara murza sitiyari,?

Dariya Yasmin tayi kuma sai bataji dadin boyewa y'ar uwarta ta datayi ba tun farko gashi yanzu taji farin ciki.

"Aunty kiyi hakuri Wallahi ni kunya naji bayan na gama zagin shi kuma infito infada miki Wai muna soyayya kuma gaskiya da farko banaso......

Ta bata labarin komai maryam ta rike baki lallai kin ciri tuta saboda ke zai fita layin gauro, saidai Yaya ismail fa ta ake ciki? Nan ma ta mata bayani sun dade suna hira a tsakanin su saida baban Auwal yashigo suka gaisa da mama ya fara sarawa Yasmin cikin tsokana,

"Toh kanwata haka labari ya juya lallai kin zama Babba dole mubiki mu dangwali arziki dariya sukasa gaba daya, maryam ta kawo musu tsarabar dawowar mijinta harda Yasmin bayan ta bata tace "ai ke mezakiyi da kaya masu Arha bayan kina Matar Oga to be,

Sun wuni cikin farin ciki kafin ta tafi ranar Oga MA bai samu kanshi ba har dare sosai kafin ya kirata a waya,

Zuby kuwa iya naci tayi Amma bataga ko keyar shiba koda ta tashi ranar har ya shirya ya fuce bakin Aikin shi, amma tana nan don jaraba,

Washe gari gidan mama ya fara cika da mutane domin bikin ismail da Zainab don baban Zango ya buda mai wuta sosai dole ya hakura da zancen Yasmin badon yasoba,

Kuma a yaune Zasu tarbi bakin MA Wato iyayen shi masu nema mai Aure,
Aunty maryam tazo da wuri suka shirya musu kayan tarba su snack tareda kaji dakwala tarbar girma dai suka shirya,

Karfe goma baki suka iso falon baba aka bude musu ta waje Wanda dama don baki ya tanade shi yau angyare tas yana kamshi,

Mayan mutane ne kana ganin irin motocin da suka shigo Unguwar kasan MA ya gaji Arziki gaba da baya, baban Zango da baba da Abokin mahaifin su limamin Zango dattijon Arziki suka tarbesu cikin girma,

Maryam ta shigo musu da kayan motsa baki  cikin harkar girma kuma sun yaba da inda MA yazo neman Aure,  sungabatar da kayan nema irin su giro sweet katan katan dasu biscuit da dai sauran kaya hade da dubu d'ari na gaisuwar iyaye,

Baba liman yace ina Abin yayi yawa kudin gaisuwa ai ba sadaqi bane,  sukace Sam Abarshi haka bama haka yaron ya so ba kawai sun ragene don Albarkar Aure kawai suke nema ba riya ba,

Baban Zango  yace to Allah yasa Albarka,  suka nemi Alfarmar daurin Aure a gobe inyaso tarewa a jira lokacin da duk suka shirya,

Baba baiso hakan ba Amma baida ta cewa don kanin shi tuni ya Aminci da zancen tareda baba liman suka sa Albarka a nan take suka ajiye dubu d'ari biyar na sadaki,

Suka rabu cikin mutunci tareda farin ciki..... 🖊️

Kyawon Alkawari cikawa shiyasa nayi muku amma da ba haka ba 😟

Kudai biyoni zuwa jibi my fans🏃‍♀️

*Matar soja*
[8/30, 2:56 PM] Feenerh Wrtr: PROFICIENT WRITERS ASSOCIATION

ᴛʜɛ ᴀʙɪʟɪᴛʏ ᴛᴏ ɢᴜɪᴅᴇ ɪs ᴛʜᴇ ᴍᴏsᴛ ɪᴍᴘᴏʀᴛᴀɴᴛ ǫᴜᴀʟɪᴛʏ ᴀ ᴡʀɪᴛᴇʀ ᴄᴀɴ ʜᴀᴠᴇ, ᴡᴇ ᴘʀᴏғɪᴄɪᴇɴᴛ ᴡʀɪᴛᴇʀ's ᴀssᴏᴄɪᴀᴛɪᴏɴ ᴡɪʟʟ sʜᴀʀᴇ ᴛʜᴇsᴇ ǫᴜᴀʟɪᴛɪᴇs.

INSTAGRAM: https://www.instagram.com/proficient_writers/

FACEBOOK: https://mobile.facebook.com'/groups/2455147078097572/

TWITTER: https://twitter.come m/pro__writers?s=09

🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
*BARIKI*
_Auren Soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

_written by FENERH_
Maman Ammar

*Dedicated to*
Fiddausi mainasara feby

*Wannan nakine my Aunty Hajiya Sa'adatu Allah yaraya mana Ummu kulthum ya Albarkaji Rayuwarta Heart you wlh irin so na jini*

33&34

Fadin farin cikin MA bata bakine don da labarin za a daura mai Aure gobe yazo yana office kanin baban shi ya Kira ya shaida mai, sujada yayi tareda godiya ga ubangiji yanzu gobe za a daura Mai Aure da Yasmin? Alhmdulillah yake ta mai mai tawa,

Inter come ya danna tareda kiran Ahmed yana shigowa kafin duk ya saramai yayi saurin rungume shi kam tareda cemai "nagode Ahmad sanadin ka nasamu farin cikin Rayuwa, ya

sakeshi tareda riko hannun shi,

"Karka damu zankula da Yasmin bazan taba wulakanta ta ba ina son ta sosai Ahmad sorry for not comfesing my love earlier to you wallahi komai ya faru a lokacin da nikaina ban shirya ba, "oh my god ya fada tareda dafe kanshi cikin so much excitement "gobe zata zama tawa zan mallake ta zata zama mallaki na karkashin iko na, she is going to be my queen my princess,

Mamaki ya cika Ahmad sosai don shi bai taba tunanin MA zai taba son wata ya' mace ba saigashi yau yanayi wa Yasmin so mai zafi da har zaka iya gani a idanun shi,

Ranar yaranshi sunsha kyauta don saida ya rabawa duk Wanda ke office din dubu Ashirin Ashirin Ahmad kuwa transfer kawai Yamai na one million yace ya Kara Yama iyali hidima,

Arziki kashi ta sanadin Matar Auren shi yasamu ci gaba lallai dole yakara rike maryam gam domin ita din Alkhairi ce a rayuwar shi,

Ranar barin office kawai yayi ya nufi gidan Hajiya, itama taga sambatu ranar Wanda ita tafi kowa farin ciki, "baba na kana son Yasmin sosai na ga Alama duk ka firgice haka, saidai magana daya bazata tare ba gobe sai An shirya,

Tuni ya gimtse fuska "haba wane irin shiri kuma? Mu kammu muna bukatar lokaci a hado mata lefe kamar kowace mace y'ar Gata karka manta yayyinka mata sunci burin Aurenka jiya nakirasu duk nafada musu, Halima zataje Dubai dama nace zanyi mata transfer ta hado mana lefe a can,

Ajiyar zuciya kawai yayi duk da baiso haka ba Amma Shima zaiso a san zaiyi Aure dole a shirya grand wedding

Duk da yaso su tare goben Amma no problem andai daura ai tazama tashi to ai ba damuwa,

Yasmin dai Abin yazo mata a bazata Auren ta da MA gobe? Kutumar uba lallai ta kade har buzunta, duk da tana son shi Amma bata shirya Auren shi ba yanzu taso sai ta gyara kayanta kafin ta shiga don tasan akwai matsala da Y'an matan shi musamman zuby,

Tana cikin tunani ya kirata ta kalli wayar takasa dauka domin jikinta yayi mugun sanyi saida ya Kira kusan Sau uku kafin ta yi karfin halin dauka,

"Hmm AMARYA ta yanga ake mun? Kibari har a daura gobe kinga bakin ma sai nasiya zaki bude kimun magana,

"Wai baby gobe za abani ke baki daya zaki zama tawa komai naki zai zama mallaki na "wallahi daga gobe duk Abinda nace ina so kiyi kawai Inba haka ba kisha tsinuwar mala iku,

Ai tasani kuma sai y'anda Allah yayi da ita yanzu tunda za adaura musu Aure da sarkin naci,

Saidai baby Wai bazamu tare ba sai an gama shiri hmm zaki tare da tsohon ciki kuwa baby don wallahi ki shirya bazan y'arda ba gobe I must loose my virginity on you,

"Ko ba virginity ba shine zai wani Kira kanshi virgin bayan ya gama lalibe Y'an mata, wani daci taji a zuciyar ta data tuna da kalubalen da ke jiranta,

"Baby yakirata domin yaji tayi shiru, ta Amsa a hankali ya ce "yau inaso inzo Amma bazan samu zuwa ba saboda shirin daurin Aure akwai a lot of things da zanyi dole zanyi inviting a bokai na da kuma my god father, the you no burutai na sona like his son Nima I respect him like my on father,

Saidai muntare you will no a lot about me, ya katse kiran badon yagama fadar duk Abinda yakeso ba,

Jikinta yayi mugun sanyi sosai, wayarta ta dauka ta kira Amira nan take fada mata komai,
Umarni Babba yaya ta bada aka fara shigo da akwatuna,  sojojin ne suka rika jido su ana jera su a tsakiyar falon tuni tsoro ya rufe su ganin Anshigo da saiti shida kuma ana kokarin shigo da na bakwai ai tuni mama hindatu da Wasu tsoffi suka fara rangada guda suna shewa "Allah  mai iko ya' tayi goshi tubarkallah,  saida su yaya Halima suka fitoda key na sabbin motoci guda biyu suka Ajiye masu bayan  manyan gana most go guda uku na kayan sa lalle,

Ai su mama tuni sun rasa ta cewa  sai kallo kayan ma sun rasa Wanda zasu bude sai karamar kit guda daya da su yaya Halima suka mikawa mama hindatu "ku adana wa innan gold dinta ne a ciki,  ai tuni mama hindatu ta karbe tace sosai kuwa kodan mutane wannan basai annu nasu ba gaskiya,  ga motocin ta can a waje za a wuce mata  dasu gidanta idan kungani,  ai guda kamar zasu cire kunnen mutane a ranar, saboda farin ciki ganin kayan,

"Ina Amaryar tamu take ne?  Suka tanbaya,  "ai ta gudu tunda ta gano kan zancen,  "dariya sukayi saikace a kauye Aida ta tsaya munga matar Autan hajiya,  bayan ma mara kunyar ya gama dauketa saida ga baya yace wani biki  Ai baban hajiya sai a hankali ba ruwan shi da kunya sai kunyi hakuri da surukin ku,  "aa kubarshi zamanin sune watarana sai labari,
Sun yi hira sosai kafin sutashi tafiya cikeda kayan soye soye na Y'an kawo lefe manyan robobi da kuma carton carton na drinks dai dai karfin su sukayita godiya batareda sun raina musu ba kudi dai suka ki karba sukace basai sun basuba wallahi Allah dai ya karo musu d'an kon zumunci tareda zaman Lafiya  a tsakanin ma auratan,

Bayan sun tafi su mama suka baje kayan abin ba a cewa komai ko lefen Zara sai haka don kayan ciki kawai sai sun girgiza mutum bare gwalagwalan da aka zubo,  fada bata bakine ai,  su baba kam kasa cewa komai sukayi,  mama hindatu ce tace a fadawa mijin kawai ya kwashe kayan ya kai gidan ta yafi gudun mutane ko Barayi tunda anriga ansan tayi aure basai An tsaya kiran mutane suzo ganin kaya ba

Baban zango yace "haka ne har motocin ma ai zasu kawo mana Barayi BMW ce fa daya kuma crv4 ce ina zamu Ajiye su anan a biyo dare don haka zan jira zuwan shi sai ya kwashe su,
baba dai cewa yayi kaya sunyi yawa anyi riya "baruwan ka yaya matar shi ce duk Abinda  yayi mata yanzu bamuda ta cewa don kowa ya shaida sun tara tunda ya dauketa na tsawon sati guda, "tabbas kuwa kilama da rabo, inji mama hindatu,

Ita kanta Yasmin ta tsorata da irin dukiyar da aka kawo mata wai lefe takasa cewa komai tasan MA na matukar sonta kodan irin rawar kafar da yake nunawa akanta ya isa ta gamsu 100% yana mata so mai tsanani da ace ya Aureta domin manufa ne da yanzu da yasamu Abinda yakeso da tuni ya barta kamar sauran mata , wani irin kaunar shi taji ta kara ratsa ko ina na jikinta ta koma dakinta ta kwanta tareda rufe idanun ta "me zata yimai domin farantamai itama? Me zata yiwa MA yasan cewa tana mai so kila fiyeda ma Wanda yake mata, gaba daya tunanin shi ya shigeta bataji shigowar Aunty maryam ba saida ta dafata ta tashi zaune tareda rungume Aunty maryam tasa mata kuka,

"Ikon Allah Meye na kuka kuma keda zaki yi farin ciki yasmin, "Wallahi you are very lucky samun miji irin Oga MA sai an tona kinga motocin ki kuwa yanzufa motocin ki uku yasmin ko sarkokin ki kawai sun isa su sai gidan mu uku Amma duka ke Kadai ba Abinda zanfada miki Yasmin sai dai ki kara hakuri tareda yimai biyayya akan duk Abinda bai kauce hanya ba

"Aunty nasani wallahi me zanyi mai infarantamai rai yau Aunty? "Zokiji ta fada mata tana mai mata rada a kunne ido ta dago tareda zaro ido Aunty su mama fa,? "Ki share kawai baby kije gobe fa zai tafi, shiru tayi kawai kafin ta zabura ta ciro wata Riga da wando damammu rigar ta na dauke da rubutu mai kyalli an rubuta lucky me da manyan harafi rigar ta kamata sosai fara sai kuma wandonta pencil baki yana sheki ta cikin shi golden wajen kuma net ne baki ya hadu sosai duk cikin siyayyar da sukayo A Abuja ne data tanada domin yimai Ado, ta gyara kanta dakyau tareda feshe jikinta da turaruka masu mugun kamshi Aunty maryam ta fito da wani Abu ta bata ungo ki matsa da sauri miski ne mai hadi zaki bani Ibr idan kin dawo,

Matsawa tayi ba musu dontayi kudurin farantamai rai a yau koda zata mutu kuwa sai ta nuna mai tana Sonshi itama a yau tayi wanka da turaruka Kala Kala tayi light make up tareda saka hijabi mai gyale tasaka plat shoe da jakarshi mai kyau Aunty maryam ta ci wow sis kinganki kuwa matar M.G MUHM'D Abdullah kinfito as matar officer dinki, tace muje intake miki kafin su mama su gane zaki fita, "idan suntanbayeki ina inafa? "Zance kina gidan kawata har yanzu baki dawoba ai ba Wanda yaga shigowarki bayan sunfita ta d'an tsaya tayi shiru, "Aunty ya hana ni hawa mashin fa, waya fada miki mashin zaki hau, ganin yaya ismail a gefe yasa maryam ta karasa tareda gaidashi tace Gata nan yaya, dama ta gama tsara komai yazo yana tsokanar ta "Amaryar general muje inkaiki ranki ya dade tunda ankwala ni da Kasa,

Kunya taji sosai ganin ya manta komai har yana shirin taimakon ta wajen farantawa gwarzon mijin nata bazata manta dashi ba a Rayuwa, shiga tayi Saida suka fara tafiya ta fito da wayarta ta kirashi, ringing daya ya daga, "my only wife, yafada cikin gajiya, "kana ina ne? "Office Amma yanzu zanje gida inyi wanko dole inzo inganki kafin intafi gobe
Me zandafa maka? Tafada kai tsaye, "Anything from my wife zanji dadin shi yunwa nakeji gashi na gaji baby tunda nabar wurinki wanka kawai nayi na koma aiki haryanzu gashi ina kai, Ok saikazo ta fada tareda katse kiran, saida ya ismail ya Ajiyeta tareda tsokanar ta ya wuce Abinshi,
Kofar gidan ta nufa cikin natsuwa sojan dake kofar gate din cikin sauri ya bude mata tareda Sara mata don yaganeta itace matar ogan, don yanzu basa yarda kowa yashiga saida izinin mai gida wannan kuwa basu isa su hanata ba su jawa kansu,

Gidan tsab yake ba wani datti ko ina fes yake ta kalli katon hoton shi dake katon bangon yana sanye da kaki kanshi ba hula yayi matukar kyau a hoton ma, ta cire hijabinta cikin sauri ta haye dakin shi dake sama domin bata kaunar shiga dakin da ta ga katuwar banzan nan a ciki ajiye wayarta tayi tareda Jakarta akan gadon ta sakko kicin din tasamu akwai komai ta bude freezer ta ciro naman sa ta wanke ta zuba A wuta tareda hada mai spices tareda Yanka Albasa ta watsa saida ya dauki lokaci kafin ta janyo robobin dake dauke da su daddawa dakakkiya mai citta da kayan kamshi,
Lafiyayyar miyar kuka ta hada mai cikin lokaci kadan tareda tuwon semo yatuku da kyau ba gudaji kodaya yayi d'anko,

A Leda ta zuba mai tareda zubawa a warmers din dake kitchen din nashi tabar miyar akan gas, tana goge wurin ya dawo lokacin har ta feshe kitchen din da kamshin turaren air freshener , tundaga falon yafara jin kamshi Amma saboda ya gaji yakasa tsayawa domin yasan bakowa agidan may be yunwar da yake ji ne, yasa yakejin kamshi, sama ya haura domin yin wanka yana shiga yaci karo da jakar mace hade da hijabi tuni ranshi ya baci ya sakko cikeda fushi domin cin uwar koma wacece, dai dai zata fito daga kitchen din suka gabza karo yayi saurin tarota tareda zuba mata idanu cikeda tsantsar farin ciki, "baby is that you? "Wow yafada tareda rungume ta cikin murna kamar zai ballata,

Dariya tayi "karka shafi zufa kabarni inyi wanka first am All yours, "really my queen wow, yau kin farantamin rai baby wannan irin surprise wallahi kingama biyana baby, daukarta yayi cak sai saman ya direta tayi saurin sa hannu tafara cire mai rigar cikeda jin kunyar shi ya wani kafeta da ido yana kare ma shigarta kallo, "inason wannan shigar baby komai nawa ya fito, "zanrika

yimaka irin shi idan kana so, " da gaske baby? Sosai kuwa tafada tareda shafo fuskar shi, "I love you my hubby so much tank you for everything tafada tareda kara rungume shi, wani irin dadi yaji "why are you thanking me you deserve morethern that my wife kingama bani farin ciki a Rayuwa baby the Amazing first night and this surprise am very happy am lucky to have you as my wife,

Dad'i taji tareda bashi kiss a kumatunshi bayan tayi Dage kadan don tsawon shi ta dariya ya mata
"My short wife dukan kirjin shi tayi kadan cikin tsokana yace "Aouch baby it Hurt me, "oh sorry my dear tafada cikin wani irin salon da yakara shagalar dashi wurin kallon ta, muje Kayi wankan your food is ready, "tank you lovely wife, but in one condition, "what? "Muyi tare, "yes sir your anything for you,

Gaba daya ta gama bashi mamaki ta juya tareda cire rigarta ta Y'ar a kasa tareda kuma zame wandon jikinta ya zuba mata idanun ta da suka shanye don tsabar jarabarshi data motsa ya zubawa hips dinta ido yaga yanda suka kara tudu kirjinta suna wani kyallin cika tuni ya zauce ya fice a hayyacin shi wajen kallon ta, saida ta kwabe komai ta zubar sannan ta juyo tareda taku tana girgiza mai kirjin cikin salon zautar dashi ta matso kadan tareda shafo fuskar shi ya yi suman tsaye ta juya tana juyamai bayanta tace " muje honey yamma nayi.......... 🖊️

*Matar Soja*
[9/13, 8:40 PM] Asli Smasher 💕: 🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
*BARIKI*
_Auren Soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

Written by FENERH

*Dedicated to*
Fiddausi mainasara feby

*Daga marubuciya*
HARAMTACCIYAR SOYAYYA
AUREN SOJA
KUSKURE NA
YA'YAN GATA
NOW BARIKI TYPING........ 🖊️

47&48

Binta kawai yayi kamar wani sakarai tareda jin ko ina na jikinshi na sakewa tareda ruruwa da wutar sha awar ta, bakin kofar bathroom din ya dogare yakasa matsawa nan da can ya zuba ma bayanta ido ko kiftawa baya iyayi saida ta shiga bath tub ta bude mai hannu Alamar yazo, yana hada hanya ya karaso ba bata lokaci ya shiga tareda shigewa cikin jikinta yayi wata irin wawuyar Ajiyar zuciya jin fatar jikinta mai santsi datake karbar gyara ta hadu da jikin shi ga kirjin nan dasuke haukata shi suna tokareshi ai ba bata lokaci ya zame tareda cafkesu tuni ya fara bata wuta tana kara tallabo mai yanda zaiji dadin moreta yanda yakeso,
Itama tana yamutsa shi a hankali take shafo kirjinshi mai haukata mata har zuwa marar shi kafin ta karasa gidan gwamnatin shi,

Wani irin gurnani ya yi tareda Sakin wata irin shashsheka ya kara manne mata, saida suka murji juna sosai a cikin ruwan kafin suyi wanka, jiyake kamar ya mayar da ita cikin jikinshi ya boyeta tsabar yanda yakejin soyayyar ta na karuwa cikin jinin shi, dakko ta yayi cak ya fito da ita tana makale a kirjin shi ta lafe, yana Ajiyeta a gefen ta kara makale shi taki Sakin wuyan shi,
" baby ba inda zanje kawai zan rufe gidan ne banason azo adame mu, sannan ta sakeshi ya fita daure da towel, ta mike ta nufi mirror, hand drayer ta jona tareda baje sumarta tafara busarwa,

Saida ya rufe kofar shigowar kafin ya wuce kitchen din, warmers din ya bude ya yayi murmushi tareda bude tukunyar miyar yasa spoon ya dibo kuka soup din ya sha yana runtse idanun shi

saboda test din dadin da ya ratsa mai kwanya,  "my wife,  yafada cikeda jin dad'i  kafin ya rufe ya nufi frij ya dakko musu holandia milk ya hado da cup ya koma saman yana jin yunwa ga kuma best food dinshi Amma bazai iya tsayawa cinshiba bayan ga Abincin da yafi komai dad'i na jiranshi a sama,  samun ta yayi tana kokarin dunkule sumar kan nata yayi saurin karasawa bayan ya Ajiye milk din,  "nooo karki dunkule min kibarshi haka nafison shi haka inason inji hannu na na yawo a ciki impact idan kintare zanrika kaiki saloon da kaina ko indauki wadda zata rika miki gyaran shi kullum in biyata a wata ina son suma baby  ga naki wow baby am the luckiest man ever to have a wife like you kin hada komai da nakeso,

Juyowa tayi tareda dora hannun ta a saman wuyanshi ta sakaloshi tareda Sakin mai murmushi mai kyau tace "nice nayi dace da samun miji one in town, kirjin shi ta shafa har zuwa kan round and small niple dinshi,  yayi wani irin mika tareda dora kan shi a kafadar ta "Asshh baby idan kina mun haka zakija koda yaushe inrika danne ki fa,  "so Am ready for my husband anytime he needs me,  zaro ido yayi tareda zubawa fuskar ta ido,  "a you sure?  Baby bazan gaji dake ba fa kawai ina tausaya miki ne banason incika takuraki da yawa karki gujeni Amma inkin bani kanki batareda gajiyawa ba kingama da MUHM'D Abdullah sai yanda kikayi dani,  yafada cikin kidima don hannun ta yaki tsayuwa wuri daya sai zautashi takeyi bai taba jin dadin hannun wata mace ajikin shi ba kamar nata,  magic hand,

Nidai nace bawani magic halas kenan ba yanda za ayi ka hada dadin halas da kuma haram Wanda kanayi zuciyar ka na jin tsoro wannan kuwa halalinka ne ko wani yaganka ba komai

A wannan yammaci Yasmin ta kara siye Oga MA da sabbabin salonta da batasan tana dasu ba wani irin manne mata yake karayi kamar wani chewing gum ranar har Wasu hawaye ya rika zubar mata bayan lamura sun lafa,  "please baby karki taba barina zan mutu idan narasa ki a rayuwata,  zan iya hadiyar zuciya in mutu idan naganki da wani namiji koda magana kika yimai, baby ina kishinki sosai kishi mai tsanani banason wani ya ratsamin zumar da nikadai nakeson shanta,  "pray for me  in dawo Lafiya muci gaba da Rayuwar mu cikin jin dadi,  ina so indawo mu Kasan ce koda yaushe muna tare banason inyi nisa dake,  ina son aiki na but today I felt like resigning imbar Aikin saboda ke  am scared for the first time am weak,

"You are a soldier wife ki zama jaruma so that idan yaran mu sunzo suma su zama jarumai, saurin tashi yayi tareda yaye Abin rufar ya shafo marar ta "baby ina son  inga yarana inason inganki da ciki please kibani babban farin cikin da nake jira yanzu,  tashi tayi ta shige jikinshi tareda dora lips dinta a bakinshi ta d'an tsotsa kadan kafin ta cire ta zubamai ido yanda yake kan lashe bakin kamar Wanda yasha Zuma ko sweet "Zuma na ni takace bazan iya Rayuwa da

ko wane namiji ba nasaba da kai ka Riga Kayi training dina nasaba da mijina mara kunya I can't be with anyone  ba wani namiji da zai bani farin cikin da nake samu daga gareka kaine ruhina ina sonka Muhammad so mai girma I tink na fara sonka tundaga ranar farko danafara ganin ka shiyasa nakejin tsanar ganin kowace mace a kusa da kai ko gidan ka,  ko lokacin da kafara kissing dina bawai haushin hakan najiba haushin ganin zuby ne a cikin gidan nan ya bata min rai  ina da kishin da yafi naka bazan iya jure ganin ko wace shegiya  kusa dakai ba Allah zan iya kisan kai akan ka wata rana,

Bakinta yayi saurin kamawa ya tsotsa sosai kafin ya saki cikeda jin dadi,  "oh ana sona dama akayita garani ai bansani  ba meyasa kike jamun Aji kika wahalar dani kikasani kullum cikin tunani kullum banda sukuni I na hango irin ta asar da zanyi idan aka hanani ke wallahi zan daukeki ba Wanda zai kuma ganin ki,  Kinsan har gini nayi miki na musamman  yanzu furniture's kawai zasu kawo daga Dubai a zuba gidan na Unguwar rimi,   sai nadawo zamuje muyi hutun Amarcin mu a can,  "wane Amarci bayan ka shanye romon tun bamu tareba,  "waya fada miki ni ko rabin spoon har yanzu ban shaba,

Jin kiran sallar magrib yadawo dasu daga duniyar soyayyar dasuka Lula ta diro  cikin sauri, "Zuma bari inyi sauri ba asan fa na fitoba nabar Aunty maryam da jirana,  sakko wa yayi Shima yana zubawa kirjinta dake rawa saboda yanda take motsa jikinta,  ya matso tareda shafosu, tafiya zakiyi kibarni?  Ya fada kamar wani jariri,  "Sory honey idan kadawo zamu kasance tare har Abada,  sunkutar ta yayi "sai mun kuma wanka kafin muyi salla sai in mayarda ke,

Wanka sukayi ta mayarda kayanta ta saka hijabin  ya zubawa jikinta ido tareda kankance ido "haka dama kika fito kuma har wannan gayen ya kawoki ya ganki a haka?  "Me nayi?  "Kinga yanda kikayi kyau da shigar  ga komai ana gani gaskiya nidai gobe zaki fara zuwa koyon moto banason kije ko nan da can da driver kije da kanki idan kin iya kuma banyarda da yawo ba,  "ok mijin,  tafada tana dariya,  ya bata fuska "Am serious niba sakaran miji bane ki boyemin kanki ki kulamin kanki ki tsaremin kanki nabaki Amanar kanki please baby,

"Karka damu ai bazaka dade ba zaka dawo muyi Rayuwar mu tare insha Allah,  "pray for me yafada tareda shafo fuskar ta tare sukayi salla ta kawo mai Abin cin yaci sosai itadai fresh milk kawai ta iya sha hankalinta na gida
Saida yayi brush ita kuma ta wanke kayan da tabata kafin ta fito ya shirya cikin kanan kaya yay I matukar kyau yana zabga kamshi suka fito  shiya bude mata ta shiga kafin ya rufe ya zagayo ya tayar da motar gaba daya jikin shi yayi sanyi bayason ya mayarda ita saiso su kwana tare

Amma yasan bazata soba baya son ya bata mata rai don ta faran ta mishi,

Har suka isa kofar gidan bai iya ce mata komai ba saidai yana driving cikin kwarewa yana d'an waigota a hankali yana kallon ta ita ma dai hakan ne a wurin ta har ya tsaya ta bude motar zata fito ya rikota gam "sauri kikeyi kin gaji dani ko? "Aa banason A gane naje wurin Kane za aga rashin kunya ta "inaso kizama kalar mijinki ki cire kunya idan har ba Aikin sabo zakiyi ba, you are my wife don haka ba wani kunya tsakanin mu koda anganmu ba komai,
Shiru yayi nadan lokaci kafin ya ce "um hope kayan da suka kawo sunyi miki? "Sosai har sunyi yawa ma fa baba yayi fada moto biyu fa kuma ka karo, "uhm ni banida lokacin hawa motocina sai na soja ko na siya bana hawa kinga yanzu inada iyali sai insiya musu Kala Kala su hau idan kinga wata ma kina so just tell me sai akawo miki,

"Dashboard ya bude ya ciro ATM ya saka mata a hannun ta "kirika sa mai a moto gobe za akawo miki kayan Amfanin da kike bukata naci if anything needed just used this and buy ya fada tareda janyo wata ledar a bayan motar "I forget to gave you this, ya mika mata ledar na siya mana waya iri daya idan kin shiga ciki kisaka sim a ciki nayi mata caji cire kwalin wayar tayi ta zuba mai ido wayar da tagani a TV tana burgeta galaxy 20 20, rungume shi tayi tareda godiya, "meye haka don nayima mata na Abu take mun godiya? "Uhm ita matar Ajiya tabawa mijin da bazata gode mai ba? "That's my duty my wife to make you happy banason matata ta rasa komai koda kudina zasu kare kuwa,

"Allah yakara budi, ta fada, Amen wifey, bazan samu shigowa ba but zamuyi waya idan nakoma gida kisa sim din zanje wurin hajiya idan nadawo zamuyi waya, tace "tom kafin ta juya zata fita, ya kuma fisgota bakinsu ya hade nadan lokaci kafin ya saketa yana fesarda numfashi "Sory na zama mayenki bana koshi dake yanzu haka inajin kamar in koma irin dazu you are sweet baby, dariya tayi ta bude motar tana daga mai hannu, yace "wait, daukar ATM din yayi da ta barmai that means bazata dauka ba, "saida ya matsa kusa da ita ya d'an ka mata a hannun ta "yanzu ba da bane ke matata ce you have right over my everything don haka feel free kiyi Amfani da komai nawa, "naga ba Abinda zanyi da kudine what if na kwashe maka kudin ka duka ina fa kashe kudi? Ta fada cikeda tsokana, dariya yayi "oh zaki iya cinye kudin ciki ok "I will see that my current Account hhhh yayi baby idan kika cinye duka inaso inga kinyi kiba kuwa kafin indawo,

Saida ta shige gidan yabi bayanta da kallo kafin ya fada motar ya tafi cikeda jin kewar rabuwa da ita ta mugun lasa mai Zuma mai zaki ta tafi ta barshi da tand'e baki, koda ta shiga gidan gaban ta ya fadi ganin yanda suke baje a tsakar gidan sunata hira, yasa ta dukar da kanta

gani ba Aunty maryam da Alama itama ta kama kanta, "yanzu don iskanci yanzu kike dawowa gida Yasmin? Mama ta fara fada "yawon da bakiyi da bakida Aure ba shi zaki tsiri yi yanzu da igiyar Aurenki yanzu da mijin ki yazo nemanki fa me zamuce mai? Ajiyar zuciya ta sauke jin ba agano taba, mama hindatu tace "ya isa yaya Saude tunda gyara taje yi kuma maryam ta fada miki gidan kawarta ne meye na fada,

Hakuri kawai ta bayar ta shige dakin ta saida ta tube kayan jikinta tasa rigar bacci mara hannu Mai silbi batareda ta sa komai ba don zafi takeji, ta dora zani tareda sako hijabi ta fito, gefen mama hindatu ta zauna tace "mama meye akwai yunwa nakeji sosai, "akwai shinkafa da miya kuma tuwo miyar taushe, ya mutsa fuska tayi bataji Abinda take son ciba kitchen din ta wuce ta samu fulawa ta kwaba ta soya wainar fulawa da taji su tarugu da Albasa ta dakko yajin tafarnuwar mama ta zuba ta dakko plate din ta wuce dakinta ta ajiye ta koma dakin mama ta dakko zobo mai sanyi da yaji Abarba dasu cucumber ta koma dakinta ta, saida ta hada wayar da ya kawo mata ta kunna, kamar jira yake kuwa taji ringing, ganin video call ne yake kiranta yasa ta dauka tana dariya tareda janyo plate dinta,

Zuba mata ido yayi kawai bai iya cewa komai ba yana kwance akan gadon shi, "yau na kurma zamuyi? "Eh idan har baki cire min hijabin jikin kiba, "oh shine matsalar Oga? ai umarni kawai zaka bayar in aikata, ta kwabe tareda cire zanin ma ya zuba ma kirjin ta ido, wainar ta ta fara ci tana runtse idanun ta saboda dad'i ya mayarda idon shi fuskarta "meye haka kikeci? "Wainar fulawa "shine Abincin ki? "Shi nake sha awar ci kawai, Hmm kawai ya iya cewa yayi shiru "kidaina cin any how food gwara ma naman kazar naki zansa aka wo miki kirika ci, wai ma me kikafi so a Abinci? "Ummmm indomie spaghetti macaroni and,... "Wait sune Abincin kayan basir noo ki rika cin Abinci mai Lafiya bawai kiyita fama da starch ba shiyasa marar ki a shafe a haka zaki dauki ciki? Any way I love it,

Saida tasha zobon ta yana kallon ta komai tayi burgeshi take karayi komai nata Abin sone a wurin shi, tace ya jirata ta dawo zatayi brush ta na zuwa, ok kawai yace ta Ajiye batareda tayi cut off ba ta fita tayi brush saboda garlic din da taci ta kuskure bakinta da mouth wash sannan ta dawo bayan takai kayan kitchen, duk sun shige daki sun kwanta, ta rufe nata dakin ta haye gadon tace "Sory nadawo sweet ta bude mai kanshin fruit tace open your mouth, ya bude yana kallon ta ta jefa Abakinta, "zaki biya bashi baby idan nadawo you must pay for that sai na tsotsi sweet abakin ki tunda kika samun rai da Ina kusa harda lips din ma zan cinye, naso mu kwana tare yau baby amma bazamuyi bacci ba zamuyi hira for the last time, "no not last saikace bazamu rika yin waya ba kuma ai bazaku dadeba, "eh zamuyi wata daya zuwa biyu Amma bazan yarda ba nan da one month ina bukatar ki a cikin gidana don haka choose ina kikeson zama barracks ko gidanki? "Duk inda kake bukata nan zamu zauna Oga, "to zaki zauna Unguwar rimi idan nadawo gaba daya mu koma BARIKI tare,

"Yes sir ta fada tana dariya,  kallon ta kawai yakeyi  "wannan kallon fa Oga?  "Na so ne da kuma sha awa,  ya juya tareda haska mata jikin shi "kinga fa tun dazu haka nike indai zanganki bata taba ha kura ta kwanta  "dazu fa ta koshi kusan fa sau uku fa,  "uhm kedin ce ai kamar Zuma kike zubawa da madara  a ciki baby,  yafada yana mika,  "kin kama kin rufe min su a Riga ma kibude min ingani please  nida kayana,  har zata bude ta tuna karon farkon su data cire mai , "aa karka kasa bacci kace   zakazo gidan mu da daren nan, "no I want I just want to see ne kawai please,

Zame rigar tayi ya zuba musu ido "baby suna responding fa kinga yanda suke kara girma kuwa hannu na akwai magic gaskiya,  shagwabe mai fuska tayi "to ai ma zafi sukemin ba ka musu da wasa fa ta taba kan kadan kaga nan zafi yakemun sosai dazufa har cizona Kayi,  ido ya zaro "kai baby sharri zaki mun yau ya zan ciji Abin dadi na idan naji mai ciwofa na jawa kaina, "kasani ne ai baka hayyacin ka,  "kai baby sai kace wani Wanda ya suma?  "Eh mana harfa kyautar yaya Halima kamun dazu da Aunty salma,  dariya yayi harda rike ciki "baby sharri? Dama haka kike,  kallon kyawawan hakoran shi tayi  gayen karshen kyau ne karajin shi take sosai a cikin jinin ta batasan lokacin da ta fara fada mai dada d'an  Addu oi ba,  "Allah ya kare mun kai mijina yadawo min dakai Lafiya in faran tamaka har karshen Rayuwar mu Allah yabani yara masu kama da baban su,

Dadin Addu ar yaji har cikin zuciyar shi "Amen my wife Allah yabani masu kama dake dai kinfini kyau baby,  "zagina zakayi kuma ka kalle ka fa   Zuma na,  "me yasa kike kirana Zuma? "Because you are the sweetest thing ever      happened to me ina Alfahari dakai farin ciki na, "Alhamdulillah ko mutuwa nayi yau zan mutu as happy man magan ganun ki yau suna tsuma zuciya ta baby kibarni haka karki hanani yin aiki na a natse fa,

Haka wa innan masoya suka raba dare suna farantawa zuciyoyin su kafin ya umarceta da tashi domin gudanar da salla ta neman kariya da biyan bukata,  saida aka kira sallar Asuba tayi  salla ta koma bacci,  shikuwa training ya taba kafin ya  fitoda manyan Jakun kunan shi guda biyu falo ya fito cikin kakin shi  ya dora hula tareda cire karamar pistol din shi ya makala a gefen kafar shi yafito a sojan shi karfe bakwai motocin shi suka jera Ahmad ne ya fito mai da kayan shi suka zuba a bayan motar har an bude mai zai shiga ya kalli Ahmad "Aunty na nan?  "Eh tana ciki ya wuce tareda tsayawa  Ahmad ne ya bashi izinin shiga,  dai dai ta fito domin tafiya gida itama don bata shirya zama ita kadai ba miji a gari ba,  batayi mamakin ganin shi ba,  suka gaisa batareda ya zauna ba ya ciro envelope  ya mika mata "na gode Aunty don Allah ki kulamin da baby na barmiki  Amanarta,  Abin ya bata dariya wai baby sai kace wata babyn roba,

To kawai  tareda godiya ya juya ya fita Ahmad ya daga mata hannu ya tafi Shima,    suka kama hanyar su ta birnin gwari  sai muyi musu Addu ar kariya daga duk kan sharri,

Yasmin kuwaSaida Aunty maryam ta isa gidan ta tashe ta "ke kina nan kina bacci mijin ki ya kama yana faman tunanin ki bayan ya gama danka min Amanar ki, murje idanun ta tayi sannan ta tashi zaune "wallahi Aunty jiya banyi bacci ba muna waya, "kaji masoya bari inga meye aka bani ta fito da envelope din ta bude idanun ta ta zaro ganin mikakkun kudi Y'an dubu dubu sunkai hundred tace "kaga kyautar manya yasmin "kingode ai, wayar ta tagani ta waro ido "kaga matan manya komai a wurin ku ake fara gani,
Kai Aunty , to kitashi nakira kawata y'ar sokoton nan zatazo zamu fara gyara kafin mazan mu su dawo nasan kudi ba matsalar mu bace tunda munada matar Oga MA sosai kuwa ina nan a kusa ta fada tareda fita da sauri domin yin wanka,
Su mama suka fara mata tsiya "kaga manya idonki kenan? Gaishesu tayi sannan ta wuce domin yin wanka,

Baban zango dai ya baje kudin shi wajen zabowa yasmin best furniture's na yayi masu matukar kyau da tsada ko y'ar wani Babba sai haka su mama ma sun kwaso mata kayan kitchen masu kyau na yayi siyayya dai sunyi Masha Allah ita kuwa ta Dage wajen gyaran kanta domin burge mijin nata idan yadawo,

Tunda ya tafi bai samu natsuwa ba yana matukar kewarta Amma ba halin kira suna cikin hadari domin kowa yasan hadarin dake tattare da kauyen, ita kanta tana kewar shi sosai,

**********
Two weeks
Idan ka kalli yanda ta murje ta kara cika don batada matsalar komai sai ta rashin mijin nata domin tana tareda y'ar uwarta koda yaushe ga familyn ta masu matukar jida ita domin baba ma yasan haihuwa nada rana don shi kanshi ta dauke mai lalurori da yawa ga kayan Abincin da ake kawo musu duk bayan sati daya, hannun ta ya fara fadawa a tukin da take zuwa mota daya kawai ta Ajiye a gidan sauran baba yasa ankwashe an mayarda su BARIKI gudun Barayi KO sa idon mutane,

Yau ta dawo da wuri daga driving school tana zaune a gefen Aunty maryam tace "Waini Aunty kina damuwa kuwa? "Dame fa? Bakyajin labarin baban Auwal naga kuma ko q jikin ki, "Lafiya lau suke yanayin aiki ne madam MA welcome to the Army work madam, "hmm gaskiya matan soja fa na hakuri , "jarumai ne idan bakida hakuri sai ki jefa kanki a halaka wallahi don haka Wasu ke karuwan ci da Auren su, Allah ya kyauta, "Aunty d'an malele nake jin ci wallahi, wani irin kallo tayi mata ke banfa gane ba kinga Al adarki kuwa? "Fesar da ruwan data fara

kurba tayi tareda dafe kirjin ta tace "wallahi kusan kwana  goma kenan da wucewar Al adata kanbu,  ta fada tana waro idanun ta waje,

Dariya Aunty ta tuntsire dashi "meye haka?  "Ciki na shiga uku wannan ai Abun kunya zanyi ciki ban tareba wayyo Allah na,  "banson shirme nidama kallon ki kawai nake kinga yanda kika cika kirjin ki yayi full ga hips dinki ya kara budewa fuskar ki har wani sheki takeyi in anyi magana kice wai gyara ne don haka k8daina shan hadin nan saboda gudun matsala,  itadai tana tunanin kar a gano tasha kunya,   dafe  kanta tayi kawai tayi shiru MA ya gama da ita shi yanacan Abinshi,

Ai fa kunsan sharrin Abin kamar karta Ankare  da cikin ai kuwa ta fara kananan laulayi don ma gidan nasu sukadai ne sai Aunty maryam da mama,  cikin sati daya kullum sai ta kyelaya Amai da safe  yauma  tana kwance a katifar ta tana jin yanda zuciyar ta ke tashi takasa fita don tasan mama na wajen,  ganin zata gala baita dole ta fito da gudu tundaga kofar dakin ta fara kelaya amai mama ta tsaya kawai tana kallon ta,  saida ta gama tace to zoki wanke bakin ki maryam gyara wurin,  idan kuma kungama boye boyen ku kya rakata Asibiti taga likita ai,
Ko akwai d'an da kuka haifa a gidan nan ne ban sani ba  waye yaro a nan dazaku raina mai hankali,  ai sai ki yi rainon ciki   a gida kya tare da d'an ki,  "kunya dai ta shata ranar haka ta koma dakinta Aunty maryam tayi tsit saida mama ta gama sannan tace "bayan sun kwashe sati daya a Abuja mama dole kisa ran hakan ai,  "to yayan zamani,     jan bakinta tayi ta  shiga cikin dakin nasu domin ganin halin da yasmin ke ciki,

Saida suka kwashe sati uku a kauyen kafin yasamu lokaci ga rashin network a daren ranar ya fadawa     Ahmed ya shirya zasu shiga kaduna gobe ya yi kewar matar shi sosai  ga shi tunda yazo bai suyi waya ba don haka he will surprised her,    bana bukatar escorts  mukadai zamuje, yace ok sir,

A  daren yasmin zazzabi yasa ta gaba sosai don haka tunda safe suka nufi Asibiti wani  private hospital   suka bata kulawa sosai bayan sun yi mata scarning kafin subata gado domin tana bukatar ruwa saboda rashin karfin jikinta da kuma Aman datake tayi, ........ 🖊️

"Afuwan my fans nima jikin sai a hankali ina lallabawa ne yau ciwo gobe lfy bansani ba ko ciwon tare mukeyi da yasmin🙈

*Matar Soja*
[9/15, 8:14 PM] Asli Smasher 💕: Follow this link to join my WhatsApp group: don Allah duk wadda take cikin grp dina kartayi joining wann ina rokon ku,
https://chat.whatsapp.com/KurmEtaqVGVByLrCjiVwZF🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
*BARIKI*
_Auren Soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

Written by FENERH

*Dedicated to*
Fiddausi mainasara feby

49&50

Sun iso garin na kaduna Ify direct Unguwar dosa yace Ahmad ya wuce dasu
Don ya mugun matsuwa ya ganta kewar ta yakeyi kamar hauka don baida yanda zaiyi ne yasa ya dauki satuka bai ji koda muryarta ba ya wahala sosai ji yake kamar yayi tsuntsu ya ganshi a jikinta, saidai yataki rashin sa a suna isowa suka tarar basa gidan mama ta fada musu sunje Asibiti, cikin kidima yake tanbayar ta waye ba Ify? "Yasmin din ce ta kwana biyu tana jin jikin shiyasa yau nace su tafi Asibiti, wani iri yaji a cikin zuciyar shi kamar yayi kuka yace "mama meke damun baby? Wane Asibiti sukaje kuma? Kunyace ta rufe mama wai baby,

Taji dadin ruwan da suka samata don taji karfin jikinta sosai sun bata magun guna tareda shawarori kafin su dawo, driver ne ya tukasu don bazata iya driving ba, sun dawo gida suka samu bakuwar mota a kofar gidan nasu, Aunty maryam tace "yasmin ko su baban Auwal ne suka zo? Wani irin dadi taji tareda Addu ar Allah yasa sune don tana cikin damuwar rashin jin muryar shi sosai cikin rawar jiki ta nufi cikin gidan Aunty maryam ta dauko mata magun gunan tareda takardar scarning dinta, ta shigo dai dai yana famar tanbayar wane Asibiti sukaje,

Sallamarta ya dawo da hankalin shi gareta, wata uwar Ajiyar zuciya ya sauke tareda zuba mata

ido cikeda tausayi don ya hango y'ar ramar da tayi saidai ta kara kyau sosai duk da ba make up a fuskar ta, ba bata lokaci ya taso cikin sauri tareda riko kafadunta ya zuba mata ido "baby meke faruwa meke damunki don Allah kinga likitan? Takasa cewa komai sai kallon kwayar idon shi takeyi duk ya rude mama dai shigewa kawai tayi don gudun ganin Abin kunya don ta lura ko makobtaka MA baiyi da kunya ba, yama manta da cewar tana wurin ga kuma Ahmad dake rungume da yaron shi a gefe maryam jan kayan ta tayi ganin Sam su Yasmin sun manta da mutane a wurin ko ince MA, falon baba ta bude mai suka shige Abinsu, bayan ta Ajiye musu magun gunan tace "idan kun gama kallon soyayyar love birds ga result din da magun gunan ta wuce, yasmin kadai taji ta shi ya Riga ya gama rudewa da kallon ta Abu biyu ya daga mai hankali, na farko ciwon nata nabiyu cikarda yakara ganin kirjinta yakarayi gaba daya yasa baima san me yakeyi ba saida tace "ka kori mutane ai sai mu zauna ga kujera,

Waigawa yayi tareda kallon ta "akan me zan zauna A nan muje cikin dakin ki indan latsa ki kadan wallahi a matse nake nayi kewan zumar ki baby nayi full dayawa, dagata yayi cak suka shiga cikin dakin nata saida ya Ajiyeta ya yaye katon gyalen ta ya tsuguna a gaban katifar ya zubawa ko ina najikinta ido, "baby meke damun ki? Bakida Lafiya but ki kalli nan dinki sunkara cika, yafada tareda dora hannun shi saman kirjin ta, bata fuska tayi bakai bane kaja mun ciwon, zaro ido yayi "saboda rashin jina kike ciwo baby ai nafiki damuwa sosai kullum bana iya bacci, "nidai zanci Abinci yunwa nakeji ban karyaba, "ok ko zamu tafi gidan mu ne? "Aa nidai bazanje ba sai muntare baki daya, dafe kanshi yayi " yazakiyi da damuwata tom bayan saboda ke nazo, Kayi hakuri, "hakuri meye kuma hakuri ai bansan wane yare bane haka?

"Nikaga banda Ify kuma Anbani magani ance sai naci Abinci zan sha gashi ka hanani, "noo ina magun gunan da kuma Abincin,? "Aunty maryam zata bani, wayar Ahmad ya kira yana dauka yace "ina Aunty please tazo, tom kawai yace ya kife wayar tareda zama gefen ta kafadar su na gugar na juna ya dora hannun shi saman kirjin ta yafara shafawa yana lumshe idanun shi, tayi saurin turewa "Aunty fa na zuwa, "so ita kikasan me sukeyi?
Sallamar Aunty maryam yasa ta yi saurin matsawa daga kusa dashi shigowa tayi da jakar Yasmin tareda kuma magun gunan da suka bari a waje Sannu da zuwa tayi mai tareda kallon yasmin "wato kinga miji kin manta da maganar likita ko? "Aa Aunty ai shiyasa na kira kizo tace yunwa takeji Abata Abinci, "to nidai zanje inji da mijina yanzu Aikin ka ne nayi nawa ga result din da kuka bari da kuma scarning, "ciwon har yakai Ayi scarning meke damun matana haka Aunty? Mikamai takardar tayi ya bude,

Wata irin zabura yayi tareda mikewa tsaye ya zubawa Yasmin ido "what? Ciki' ya fada tareda zama yana kara janyota jikin shi "tell me baby ciki gareki? Duk ya rude ya gigice "ciki Aunty ciki takeda shi cikina? Am going to be a father,,? Tasan zaiyi farin ciki Amma bata tama tunanin farin cikin shi zai kai har haka ba, ya manta da Aunty maryam tuni ya rungume ta tareda Dora

hannun shi a marar ta cikin kidima "Tnk you baby tank you tank you Wasu irin hawayen farin ciki ya ke fitarwa ya zabura cikin rashin Abinyi ya saka hannun shi cikin wandon shi ya zaro duk kudin ciki ya zubewa Aunty maryam a kasa Aunty kiyi manage zan kuma ganin ki idan na natsu,

Aunty Abin ya mugun burgeta irin wannan farin ciki sai kace akan shi aka fara haihuwa, zama yayi tareda rungume ta gam "baby me zakici? Kici Abinci baby na ya yi kiba "oh zaki wahala inya yi girma sosai wurin fita please me zaki ci tell me Aunty kibata Abinci don Allah karta yi aiki ko kadan karta wahala, to Abu yazo wurin masuyi fa, inji Aunty, wayar shi ya ciro yafara shedawa hajiya, "mama na Yasmin nada ciki zaki samu jikan da kike ta Addu ar samu a wurina mama zan zama baba, "to sarkin Y'an rashin kunya ina fatan ba gaban surukan naka kake tabargaza ba? Sosa keya yayi tareda kallon Aunty maryam yace "Aunty maryam ce kawai hajiya, to tunda ciki yasamu sai ta tare karta haihu a gidan su KO kuma ta dawo gidana sashen ka da zama, "zanzo muyi maganar yanzu,

Ajiye wayar yayi bayan ya gama kiran sauran Y'an Uwan shi suna mai tsiya, hajiya dai tafi kowa farin ciki d'an baban ta Alhmdulillah Allah ya kawoshi Ify, Aunty dai kama kafarta tayi ta fice tareda mijinta, suka nufi gidan su don Oga yace shifa yau yana gefen Yasmin zasuyi raino, mama dai ta rufawa kanta Asiri ta yi zamanta dakinta Amma bata tsira ba ya bita tareda sallama ta fito yace "mama baby ciki takeda shi zan zama baba don Allah mama ki kulamin da ita zanje inga hajiya indawo bataci Abinci ba gashi Aunty maryam ta tafi barracks da Ahmad nace mutafi tare taki yarda muje mama kisa mata ido karta yi aiki,

Ikon Allah mai karfi na bara, yau tana ganin ruwan rashin ta ido Allah dai yasa malam baya gida da Yau zatasha mitar surukinta baida kunya duk da yau ta shaida haka ya gama sanbatun shi ya fita bayan ya koma ya gama bata warning, "karki wahalar min da baby please ki jira bazan dade ba zandawo me kikeso inkawo miki? Shiru tayi kawai don ya gama bata kunya don tanajin yanda yake sakin layi gaban mama, saida ya bude shaffen cikinta ya bata kiss tareda cewa "baby yaushe zai girma cikinki yai kato? Itadai ya isheta wallahi ranta ma ya fara baci don ita yama daina damuwa da ita tun ba aje ko ina ba soyayyar ta koma kan cikin da ko kosawa baiyi ba, daure fuskar ta tayi tamau ya zauna "come on baby please karki sa damuwa ki cutar min da ciki please, "katafi don Allah kaina zaiyi ciwo tafada cikeda kufula, "ok ok sorry bari inje sai nadawo ya tashi ya fita,

Dawowa yayi "aramin key din motarki Ahmad ya tafi da tawa, Nuna mai Jakarta tayi ya bude tareda yin dariya ganin agwaluma a ciki, "mai ciki an fara kwalama, tayi mai banza ya dauka ya tafi cikeda wani irin farin ciki gaba daya ya manta da wata Abu wai sha awa farin cikin da

yake ciki tuni ya mantar da shi wannan shafin,
Gidan su ya wuce kawai, a can suka gama tattauna komai kafin ya dawo bayan hajiya ta bashi sakon danbun naman kaza mai yawa da kuma soyayyun kajin ya kawo ma Yasmin din, saida ya biya bakin dogo ya jido mata su lemo dasu kankana da duk kayan da yasan zasu kara mata kuzari da lafiyar jiki ya iso da kaya Niki Niki,

Lokacin baba ya dawo ya fara tanbayar ina Auwal yau baiyi mai Oyoyo ba, "ai yabi uban shi suntafi BARIKI, baba yayi dariya "to sun shigo kenan? Don yasan dole tare zasu zo da uban gayyar, ina ita yasmin din take? "Tana ciki inaga bacci takeyi tunda an hanata motsi saboda kar d'an so ya wahala, "bangane ba wane irin Dan so ina d'an yake? "Au kai fa bakasan zaka samu jikaba tom ciki take dashi kuma tun muna gani da idanun mu ka bashi matar shi su tare bazan iya shirgin rashin kunya ba, "tofa ciki to bari yazo ya kwasheta su tafi tunda haka suka zabi nasu Auren ya kasance gashi mamuda ya kama ya kashe mata kudi kamar ita kadai ce ya, "ya kuma rage tsakanin ku yanzu, suna maganar ya iso,

Cikin girma suka gaisa da baba ya mai fatan Alkhairi tareda Addu ar Allah ya kara tsaresu yace Amen, "Amm tom sai ku shirya tarewa zuwa jibi zan kira uwarta suzo sai a gyara mata gidan ta ko, "ai baba ba wani Abu da za a saka a gidan na gama sa komai kuma gidana zamu zauna saina dawo zamu zauna tare a BARIKI Amma yanzu Unguwar rimi zamu tare, "yanda duk kuka tsara Abinku ba damuwa matarka ce Amma maganar kaya ku nemi inda za a zubasu baza a yi hasarar dukiya ba tunda anriga anyi hasarar dukiya an siya, toh baba mungode Allah ya kara girma da Arziki, Amen yace tareda yimai fatan Alkhairi a Rayuwar su da kuma rokon Allah yakara karesu,

Baccin ta taci sosai ta koshi bayan taci d'an waken da mama ta jefa mata da yaji cucumber da kayan miya harda dafaffen kwai taci sosai tasha magani shiyasa ta more idonta ga Kasan zuciyar ta tana farin cikin ganin farin cikin zuciyar ta mijin ta Abin Alfaharin ta, wani Annuri fuskarta ke fitarwa, jin ana shafa cikinta harzuwa saman kirjin ta ta bude idonta a hankali ta sauke akan kyakkyawar fuskar shi, "Sory for waking you up ina gaisawa da lovely daughter na ne "Kasan mace ma zan haifa kenan? "Insha Allah zaki haifamin baby girl mai kama dake baby da suma irin taki, tashi tayi tareda zuba mai ido "wai Zuma ta ko kewata bakayi kana zuwa ta cikin ka kakeyi ko, ta fada tana tura baki cikin shagwaba, "oh no ni na isa baby wallahi ke Kinsan ina sonki fiyeda komai a duniyar nan kuma wannan cikin yafada yana dora hannun shi saman cikinta bansan yanda zankwatan tamiki yanda nakejiba, wallahi bazan so ko guda ya sauka akanshi ba I love you so much dole inso duk abinda yafito a jikin ki,

"Saboda farin cikin samun wannan babyn ko Abinda ya kawoni banyi ba don banason in wahalar dashi,  harara  ta balla mai "oh duk saboda babyn ka harda jarabar ta ragu?  Kai naji dadi kuwa Allah yasa   har sai na haihu,  "what?  Hmm jibi zaki  tare baby don haka ba wani sauri da  zanyi  duk da ina matse farin cikin da kika bani ya rage min komai,  shiru kawai tayi ta zuba mai ido don ta lura ya zauce akan wannan d'an tayin cikin,  "baby gobe zamuje muyi wa baby shopping ko?   "Wai me yasa kadawo ne ba yanzu katafi ba,  ai Inba bani iyali na akayiba yanzu kika fara gani na a nan gidan,   shigewa yayi jikinta tareda cusa hannun shi ta Kasan rigarta ya fara lalubarta a hankali,  ta riko hannayen shi "meye haka zaka wahalarda baby fa, "oh come on ba wani Abu zanyi ba just play  kwantar da ita yayi tareda hade bakinsu wuri daya yafara bata wani irin salon da bazata taba iya kawarda kanta. Ba,

Jindadin Abin takeyi sosai kamar karya cire lips dinshi a bakinta jin test dinsu takeyi sosai sai kara rikoshi takeyi tana kara haukata shi,  ganin yana kokarin janyewa daga jikinta yasa jikinta na rawa ta tashi tareda maida kofar ta rufe gam tadawo ta fara cire kayan jikinta don mugun bukatar Abin takeyi tarasa dalilin hakan  zuba mata ido yayi cikeda mamakin ta don bata taba nunsmai tana bukatar Abun ba sai yau saidai shi yayita kwakwa,  fadomai tayi yayi saurin rikota "oh baby kibi a hankali mana cikina karki mun asara,  ko jinshi batayi ta dora hannun ta saman wandonshi saida yayi y'ar kara ta balle belt din tareda sanya hannu ta bude rigar jikinshi yana taimaka mata tuni ta zautar dashi baijin zai iya barin wannan garabasa ta wuceshi

Tuni ya fita zakewa suka fara tumurmusa juna cikeda kewar juna da sukayi,  karar wayarshi ya dawo dashi daga duniyar tsotse tsotsen da yatafi  dakyar yake iya bude idanun shi ya daga wayar  saida ya gama sauraren su kafin ya mike ya ware idanun shi  oh my god ya fada da kyar sannan ya Ajiye wayar ,  dakyar ya bude bakin shi "baby zanje office am sorry I will be back for you get ready  for me in the night kintayar min da kwadayi ga shi sunkira ni a wurin aiki,   cikin sauri ya mayarda kayan shi  ya tsuguna tareda manna mata kiss  take care of my baby,  ya fita da Sauri tabi bayanshi da kallo,

Tashi tayi tana murmushi tareda jin soyayyar shi na da da karuwa koda yaushe cikin zuciyar ta shi na daban ne a cikin maza tana son Muhammad Abdullah so mai tsanani  tanajin kishin shi gani take har gobe mata nabi mata miji,

Baisamu dawowa ba saidai kiranta yayi yabata hakuri saboda soja baida hutu koda yaushe yana bakin Aikin shi,  duk da yazo ya huta ne amma bazai taba hutun ba sai ranarda yayi ritaya,

Da safe su mama hindatu da Aunty maryam da kuma wasu Y'an Uwan mama suka zo domin rakata gidan mijinta baba yace ba wani taro da za ayi ta bari idan ta haihu sai ayi taron tunda ga ciki nan, saidai uban gayya tuni ya shirya kwarya kwaryar liyafa a officers mess domin Abokan Aikin shi yace maza zalla ne kawai zasu hada barbecue domin tayashi murnar Aure da kuma samun karuwa,

Cikin sirri yasa aka kwashe kayan da akayiwa yasmin yace akaiwa Aunty maryam mama kawai ta sani da mama hindatu don gudun fadan baba, itadai Aunty maryam tayi farin ciki sosai domin ko a Aurenta bata samu wannan dama ba, kayan kitchen dinta ma da suka kai mata ajiyewa akayi domin ba abinda ba a zuba a yafjeken gidan da suka kira da Aljannar duniya nera tayi kuka gidane d'an karere ga katon garden da yaji kayan marmari Kala Kala gefen shi da sweeming pool mai burgewa, furniture's din kuwa set ne na royal Italians masu shegen kyau masu ruwan Zuma da fari gida dai Masha Allah , tuni sunkai mata kayanta gidan harma da motocin hawan ta,

Washe gari karfe biyu baba yasa ta shirya da kanshi ya dauketa domin yimata rakiya dakin mijin nata domin ya nemi Alfarmar yanason tazo da wuri akwai party da aka hada mai,
Tasha nasihohi masu karya zuciya da shiga jiki daga gefen mama harma su baban da suka zaunarda ita, su mama sun mata Nasiha mai Amfani sosai saida tayi kuka Aunty tace sai sun hadu a BARIKI yanzu ta zama matar manya gidan ta shigasaida izini saboda sojojin dake kofar gate dinta, zuciyar ta ta karye sosai ganin da gaske shikenan yau zata koma gidan Muhammad gaba daya,

Hawaye ta share tareda yin shiru, komai nata yazo daban da na mutane Aure ba shiri tarewa da ciki kuma ba taro, ba kuma mai rakata, haka suka isa gidan nata tafkeke, shi kanshi baba ya tsorata da ganin irin wannan katon gidan yanzu a nan y'ar shi zata zauna, Allah mai iko da kuma girma , bude musu katon gate din sojojin sukayi baba ya shiga da motarshi suka fito wata dattijuwa ce ta fito tana musu Maraba da isowa tayi musu jagora saida ta sadasu da falon tace.
"Sannu da zuwa uwar gida Sannu da zuwa gidan ki Allah ya kade fitina, fitowar su Aunty Halima dukan su suka fara mata Maraba da Amaryar baban hajiya yaudai zamu ganki ko, dukarda kanta tayi tareda kara janyo hijabin ta, har kasa suka duka suka kara gaida baba tareda godiya ya Dan ka musu Amanar ta tareda sa Albarka ya tafi, sunata mai godiya,

Kamar ta riko shi takeji tana ganin ya fita tasa kuka shikenan itama An sallame ta daga yau tabar gidan su, su Aunty suka ce tayi hakuri ta tashi ga mai make up tana jira za aje partyn yanzu bata da zabi haka ta mike suka Nuna mata wani daki ta shiga saida aka hada mata ruwa tayi wanka tareda yin Alwala ta fito saida tayi LA asar sannan ta zauna aka fara tsantsara mata

make up,

Wane irin party MA ke shiryawa tana da ciki meye na wani taro itadai batasoba gaskiya gashi tun shekaran jiya da yazo bata      bata kuma ganin shiba saidai waya a gurguje,
Wani  farin less suka bata Riga da zani na buba suka daura mata zani a saman rigar tareda daura mata  wani head mai golden yana sheki suka Ajiye mata  poss da takalmi mai tsini sai a shoken kalar head dinta   tayi kyau fiyeda tunani,  suka rika Masha Allah baban hajiya ya iya zabe gaskiya tubarkallah sai kunya take ji yanda suke kod'ata,

Kiranshi sukayi akan sun shiryata,  yace motoci nanan a waje su fito harda su zasu iya zuwa don yaga Y'an gayyar sodi ma  da ba gayyace suba duk sun shirya zuwa kwasar gara,  domin na hango Aisha dahiru da katuwar Jakarta  tareda Ummu jidda  da ta kwashi katon no respect gudun raini  a hankali nafara ankarewa gaba daya ma  BARIKI fan's sun cika gidan harda su hussy Ali gasu maryam dina andauki wanka nace to nima dole in dauki nawa Gayun muje kwasar gara........ 🖊️

Mu cigaba da hakuri da juna my fans  muna nan zuwa inda mukeson mu isa da ikon Allah komai yayi farko zaiyi karshe,

*Matar Soja*
[9/16, 10:05 PM] Asli Smasher 💕: (¯`*•.¸,¤°´✿.｡.:*ᵽɌØ₣ł¢łɆ₦₮ ฬɌł₮ɆɌ$*.:｡.✿`°¤,¸.•*´¯)

ᴛʜɛ αʙɪℓɪᴛʏ ᴛσ gυɪ∂ɛ ɪѕ ᴛʜɛ мσѕᴛ ɪмρσяᴛαηᴛ qυαℓɪᴛʏ  α ωяɪᴛєя cαη нαvɛ, ωɛ ρяσғɪcɪɛηᴛ ωяɪᴛєя's αѕѕσcɪαᴛɪση ωɪℓℓ ѕнαяɛ ᴛнɛѕɛ qυαℓɪᴛɪɛѕ.

INSTAGRAM: https://www.instagram.com/proficient_writers/

FACEBOOK: https://mobile.facebook.com'/groups/2455147078097572/

TWITTER: https://twitter.come m/pro__writers?s=09

🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
*BARIKI*
_Auren Soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

Written by FENERH

*Dedicated to*
Fiddausi mainasara feby

51&52

Motocine guda shida aka ajiye musu sababbi dal suna sheki ta tsakiyar tasha Adon balloon kana gani Kasan motar AMARYA ce ta fito tareda su Aunty Halima  driver ne ya bude mata ta shiga suka shiga sauran motocin,  BARIKI  suka nufa basu tsaya ko ina ba sai 2 batallion officers mess,  tundaga titin farko zakasan an kawata wurin sosai ga sojoji  tundaga farko baka ganin karshen su kowane sanyeda ceremonial dress sunyi matukar haska wurin ga fulawowi da aka watsa saman red carpet  suna tsayawa aka bude mata tafito wasu Y'an mata ne suka jero suna paret sanye da ceremonial dress na mata mai sket  su goma,  suka sata a tsakiyarsu gaba daya tafara rudewa don bata taba tunanin haka taron zai Kasan ceba,   ko ina shi uban gayyar yake oho?  Fushi ma takeyi dashi tunda rabon da ta sanya shi a ido tun ranarda yazo aka kirashi  saidai yakirata yaji lafiyar babyn shi ya kashe that's means ta tashi aiki ita tunda yasamu ciki a jikinta tana haihuwa kuma shikenan,

Hango shi tayi yana takowa cikin nashi ceremonial dress din da yaji stars da igiyoyi dauke kuma da aninan shi da zasu Nuna maka he is the boss wata sandar girma ce a hannun shi yana dogarawa yayi masifar kyau tundaga nesa suka zubawa juna idanu yana mai jin farin cikin ganin ta gashi ta  fito kamar wata tauraruwa  karasowa yayi,  ta dauke kanta tareda hade rai ya na zuwa ya rungume ta batareda ya damu da mutanen dake wurin ba ya dora hannun shi a marar ta "ya baby na?  Rage murya tayi a hankali tareda cewa "ni nazama hoto ai yanzu wallahi a matsa inyi flushing din shi inga tsiya,  "what me kikace?  Tayi mai banza ya matse fuska sosai ya riko hannun ta suka shiga ana take musu baya ga masu hotuna tuni sun fara Aikin su,

A she kallo na ciki don Fadin kawatuwar wurin kawai zai cinye fejin yau saidai BARIKI fan's zasu baku labarin haduwar wurin ba Abinda ya burgeta irin ganin y'ar uwarta datayi a wurin ga yaronta da ke cikin nashi ceremonial dress din na yara harma da hula yayi kyau da y'ar karamar pistol ta wasa a soke a Aljihun shi, wurin zaman su suka nufa batareda ya kuma ce mata komai ba don yaji mai tafada, ga Army bands sai sakin kida sukeyi da kuma busa wurin ya tara manyan sojoji da matayen su Abokan Aikin shi gefe daya matan NAOWAS ne wato NIGERIA ARMY OFFICER'S WIFE ASSOCIATION ne suncian anko mai dauke da tanbarin gauraka Abin ba a cewa komai Abin ya mugun kawatar da ita su Aunty Halima ma gefe guda aka ware musu man yan yayyi Aunty maryam ta jone cikin su, aka fara gudanar da taro party ne mai Aji ba wani hayaniya harka ce ta girma sai masu raba drinks da kayan motsa baki keta kai da kawowa snacks ne da su namomi Kala Kala kawai kake gani, tuni na hango Ummu jidda na boye kularda ta yo guzuri don zuba rice sai yakasan ce bikin ba na rice bane,

Wani cikin manyan sojojin ne ya mike tareda gabatar da taron ta hanyar taya Abokin Aikin su murnar Aure tareda fatan Allah yabada zaman Lafiya gefe daya suka gabatar dashi a matsayin jarumin soja mai hazaka da gaskiya akan Aikin shi sun yaba mai sosai a irin kokarin da yakeyi akan Aikin shi, tareda bashi A word a kan nasarar da yake samu a operation din da aka turashi, yanda suke yabai tareda saramai lokacin da ya karbi a word trophy din ya mugun burgeta ga wani paret da ake bugamai tun tasowar shi a yau ta kara sanin waye take Aure taji takarason shi ko ba a fada ba tasan mijin nata jarumi ne,

Saida ya karbi trophy din ya karbi speaker tareda godiya cikin halshen turancin shi mai tsada, kafin ya juya wurin Y'an Uwan shi ya kara musu godiya akan irin soyayya da goyon bayan da suke nuna mai kafin ya juya kan yasmin data hakimce ta zubawa tsadadden mijin nata ido,

Ya tako zuwa gaban yasmin data zuba mai ido yafara zubo mata kalamai batareda ya damu da duniya na kallon shi ba "you are my happiness you are my world, yaci gaba da koro mata kalamai cikin harshen na nasara, samun ki a rayuwata shine babban farin ciki yasmin Kasan cewar ki a inuwar gidana shine muradin Rayuwa ta kece kika cikamin burin Rayuwa you thank you for being my wife tank you for giving me the best happiness in the world that's my unborn child in your belly please take care of my baby I love you now and I will continue loving you,

Mika mata hannu yayi ta taso tareda zagayowa ya ajiye sandar hannun shi tareda cire hular kanshi yasa guiwar shi a kasa saida ya manna mata kiss ya tommy dinta kafin ya saka hannu ya ciro wani karamin akwati mai dauke da wani diamond ring ya riko yatsar ta ya saka mata tareda bata kiss a hannun ba Abinda ke tashi sai ihun sojoji da shewar mata dayawa mata wasu sun mugun bugesu wasu kuwa wutar kishi ke ruruwa musu don sun san mijin Yasmin yafi nasu, tasowa yayi tareda zagayeta ya hade fuskar su ya tsotsi hawayen da yaga duna zubo mata na

farin ciki kafin  ya sauke bakin shi kan lips dinta yabata wani irin romantic kiss ga kidan da aka saki na  D banj na baby don't make me fall in love kidan na kara kawata romantic moment din gaba daya kowa ya mike a hole din ana musu tafi,  saida yayi kissing dinta na minti biyar kafin ya riko hannun ta bayan ya mayarda hular kanshi ya karbi pos dinta ya rike suka matsa gaban wani katon table da aka kawatashi da wani jan kalle,  wata soja woman ta bude shi saiga wani katon cake mai dauke da hoton su ita dashi  Abin ya mugun kayatuwa   saida aka zagayesu kafin Abasu umarnin yankawa bayan ansaki wakar sojoji na this is the way I wanted to be,

Ya sanya spoon ya saka a bakin shi kafin ya nufi bakinta ta bude suka cinye tare ya tsiyayo ruwan champagne  ya bata kadan gaba daya zuciyar ta tashi ta farayi don Sam batason cin cake din  saboda zakin shi Sam batason Abu mai sugar yanzu, ,  Allah Allah take su tashi a wannan taron ga kidan dake tashi yana hawa kanta ya lura da yanayin ta don haka ya sa ayi sauri a tashi yanzu madam is exhausted,  ya rikota suka dawo mazaunin su Aunty maryam ta taso ganin kanwar tata ta gaji ta tsaya kusa da ita "Lafiya madam MA,  "Aunty Amai nakeji wallahi,  fito mata da tom tom tayi tace ta jefa a baki zata rage jin tashin zuciyar,  hakan tayi saidai a matukar takure take gaskiya,

Gift ake ta Ajiye musu a katon table din dake gaban su  wasu ma harda baby set suke kawo musu wasu kuwa envelope masu kauri kai a dai haka wannan taro ya tashi cikin farin ciki duk Wanda zai fita sai anbashi jaka mai dauke da atanfar Ango da AMARYA da kuma agogon bango  ba Wanda bai samu ba harda Y'an gayyar sodi ma don Ummi zaria bayan Anbata da farko komawa ta kumayi don neman kari,
Saidai muce Alhmdulillah  Allah ya kade fitina,

Suna shiga mota ya biyota Shima ya shigo ya rungumota sosai zuwa jikinshi " Sory madam bari muje gida ki huta ko, shigewa tayi jikin shi sosai tareda shakar kamshin shi har Allah yasa suka isa gidan nasu Lafiya yaso su tsaya BARIKI taki domin tana dokin zama cikin katon gidan  nata da ya hadu da kayatuwa,
Daukar ta yayi cak batareda ya damu da masu gadin ba ya shige da ita cikin gidan  saida ya kaita cikin wani tafkeken dakin baccin su ya Ajiyeta yafara rage mata kayan jikinta da kanshi  ,
Ruwan wanka ya fara hada mata ta shiga batareda ya bitaba don ba karamin dauriya yayi ba wajen  kyaleta batareda ya jagwal gwalata ba yasan ta gaji idan ya bita bathroom akwai matsala,  don haka ya barta saida ta fito ya shiga Shima,

Shafe jikinta tayi da mayuka masu shegen kamshi da gyara fata tanayi tana karewa lafiyayyan

dakin da kallo tasan ta gama sa a a Rayuwar ta samun miji one in town daula irin wannan dole ta godewa Allah tana nan zaune ya fito tareda matsowa gaban mirror din ya rankwafo tareda dora lips dinshi a saman wuyanta, "why are you thanking Mrs Muhammad? And what are you tinking? "Am thinking of my husband, tafada kai tsaye domin faran tamai kamar yadda yake kokarin bata farin ciki, daga ta yayi ya zauna tareda dorata saman laps dinshi, "fadamin Abinda mijinki yayi da kike tunanin shi?

"Yayi min komai a duniyar nan ya bani duk wani farin ciki, magan ganun da ma fadamin dazu sunfi komai sanya ni cikin farin ciki ka nuna ma duniya cewar nidin mace ce mai sa a Ina jin kaina kamar wata sarauniya, "you are my queen I can shout out and tell the world I love my wife so much zan iya miki komai a duniyar nan idan baifi karfina ba Ina son ki yasmin I have change because of you kin nunamin ni imar dake cikin Aure tundaga ranar da na Aureki nake jina as complete man da ni kaina nakanyi tunani inada komai inada mata Kala Kala Amma I always think that something is missing, "yes gani nazo yanzu you are complete dama ni kake jira, yeah jirana ya kare dama am waiting for my woman to arrive, yafada yana janye towel dinta zuwa west, ya dora bakinta shi akan boosty boob dinta yafara bata wani irin salo tuni tafara turo mai su sosai tareda dafe kanshi takara taimaka mai wajen wasa da sumar kirjin shi, Ganin zaman wurin na kokarin gagar ta yasa ya sunkuceta zuwa katon gadon sukaci gaba da ya mutsa juna, sunyi matukar kewar junan su don haka kowane kokarin farantawa d'an Uwan shi rai yake ta ko wane fage gama daya sun gama lulawa duniyar maji dadi yasmin ta mugun zama y'ar hannu shi kanshi yaji dadin moment din fiyeda ko wane lokaci gashi batayi mai complain ta gajiba duk da yana yi yana tausayawa babyn shi, saidai yaga Alamar hajiya yasmin ta zama oganniya a wannan fagen,

Saida suka natsa tafara mai shagwabar marar ta, ya zabura tareda shafa mata marar a hankali tareda zuba mata idanu yana bata wani irin salon kallo, irin kallon kingama yi a Rayuwa, saida suka kuma yin wanka tare suna likeda juna kafin ya bude walldrp ya fito mata da wasu English wears Riga da wando masu hannun shimi wandon ya kama jikinta komai nata ya fito shagala yayi wurin kallon ta ya ce " wow baby naso mu zagaya gidan nan ki ga ko ina gashi bazan iya bari kifita a haka ba bari inkawo mana Abincin a nan muci nasan baby na najin yunwa ko,

Fita yayi bayan ya zura jallabiyar shi ya nufi kitchen din da ya zuba mata masu yimata hidima harda wata tsohuwa da Y'an mata guda biyu sai shirya dishes sukeyi yace su kawo ma madam Abinci yanzu kafin ya koma dakin, ya sameta zaune tana cin pop corn mai madara data samu a dakin, zaro ido yayi "meye kikeci haka? Karfa ki zukewa yarona jini bakomai zaki rika ciba, zama yayi a gefen ta tareda rungumota sosai, kafin ta bashi Amsa budurwar ta yi sallama tareda shigowa ta Ajiye musu a bincin akan d'an karamin table din dake dakin, wani irin kallo yasmin kebin budurwar dashi tana sanye cikin damammun kaya Riga da sket na atanfa ga uban atarch har gadon baya domin kanta wani mayafi ne mai shara shara, tana tafe tana faman

rangwada da motsa jiki,  duk da tana nan kamar maburgi Abin ya bata haushi sosai,

Saida ta gama salon ta face "Sannu madam,  sir komai yayi ready ta juya tana fita tana karairaya shi kuwa ko kallo bata ishe shiba baima san tanayi ba yana danna wayar shi saida ta fita yace "madam ga Abinci,  mugun tsaki taja tareda tashi daga gefen shi tayi saurin  komawa kan kujera tana girgiza kafarta cikeda kishi wato budurwa zai kawo mata cikin gida da sunan mai aiki  tazo tana daba mata Abinci tana kokarin nuna tsiraicin ta don ta jawo hankalin shi gareta,  tasowa yayi cikeda mamakin ta me ya faru bayan yanzu yanzun nan suna cikin farin ciki,  dafa ta yayi tareda cewa "what is wrong madam?  ", oh baka saniba ko wacece wannan? Dariya yayi "baby wacece kuwa bayan y'ar Aikin ki,  "wannan da takejin kamar ta ciro kirjinta ta dorama a tafin hannun itace zaka kira da y'ar aiki,  wallahi bana bukata I can cook for my house ko na fada maka ni ban iya girki bane ko bazan iya yima Abinci ba zaka kawomin  Y'an matan ka cikin gida wallahi sai sunbar min gida bana bukatar su,

Ta fada tareda mikewa saidai tana tashi jiri yafara kwasar ta ta koma ta zauna,  gaba daya ya sarawa Aikin hankalin ta Yau,  saurin zama yayi kusa da ita "kingani ko kishi zaija ki mun asarar baby na come on relaxed mana madam  irin wannan kishi haka,  buge hannun shi tayi yayi saurin tsugunawa a gaban ta,  "listing  bansan waye suke aiki a nan ba hajiya tasa aka nemo su KO fuskar su ni ban sani ba idan bakya bukatar su zaki iya sallamar su dama saboda su taimaka miki nace akawo su kuma in banda  Abinki yasmin me zanyi da wata house help please am not that kind man da ke neman ko wace irin mace and believe me  idan har zanyi wani Abu zan fada miki yakamata kisani bana boyo kuma bazan taba miki karyaba, I wanted to tell you something a bout zuby.... Saurin daga mai hannu tayi "please nasani tunfarko kafada min cewar bazaka iya rabuwa da itaba,  to wallahi kasani nima bazan yarda da tarayyar ku ba kuma na shirya cin uban ko wace shegiya cikin gidan nan dama barikin baki daya kuma kana tafiya zan koma can inga tsinanniyar da ta isa ta kuma takomin gida,  ta fada cikeda masifa tareda mikewa ta kwashi tray din Abincin tayi waje,  dariya Abin yabashi sosai "my jealously wife,

Tana shiga kitchen din ta samesu su biyu suna hira a tsakanin su ba tsohuwar basu maga shigowar ta ba,  dayar data kai musu Abinci kebawa dayar labari "ladi bakiga yanda naga gayen nan ba dagashi sai singlet da short wow wallahi gayen yakai karshen haduwa a gaskiya zan iya yin komai domin samun gayen nan a bed irin su akwai lasting a gado ga kyau ga kwarjini ga.... Watsar da tray din da tayi ya dawo dasu cikeda tsoro suka zuba mata ido  tareda fara kame kame,

"Wallahi yanzu right away right at this moment I want you All out of my house before I open my eyes Inba haka ba zan illata ya'  shegu matsiyata masu bin mazajen mutane ankawo ku ku

nemi Abinci kuzo kuna neman bin mazajen mutane to kuyi gaba ba gidan Fatima ba, cikin rawar jiki suka fice da gudu ta bisu da harara, a tsaye yake yana kare mata kallo yana fitarda wani irin murmushi na farin ciki kafin ya karasa shiga ciki ji kawai tayi ya rungume ta ta baya "my madam Karfa kija wata rana a daureni inkin daki ya'yan jama a saboda kishi irin wannan kishi haka madam, tureshi tayi tafara kokarin dafa musu Abinci shaf shaf ya haye kan durowar kitchen din yana kallon yanda take komai cikin korewa,

Tsohuwar ce ta shigo cikin rawar jiki tafara tanbayar ta "hajiya ina fatan bamuyi kuskure ba naga ankori sauran yaran don Allah nidai Karku koreni ina neman Abinda zan rufawa yarana asiri inada marayu, juyowa yasmin tayi cikin sauri "aa baba baza akoreki ba kuma zaki tayani wanke wanke da kuma dafawa masu gadi Abinci idan Oga nanan ni zanrika dafawa da kaina Amma wa incan bana bukatar su na sallamesu a gidana, "to nagode hajiya Allah yakaro Arziki, ta fita yasmin ta ci gaba da Aikin ta wani irin burheshi yaji tana karayi gashi ta nuna cewar ita din matar shi ce mai kishin shi that's the best thing ever, cous cous ta hada musu da yaji kayan lambu tareda bushashen kifi ta hada musu lemon kwakwa saida ta gama hada komai ya sakko tareda daukar kayan Abincin yana mai kallon fuskar ta data hade tamau,

A katon falon ya Ajiye musu a tsakiyar carpet ta biyo shi rikeda plate da kanta ta zuba musu bayan ta kira matar tace ta dauki sauran idan zata tafi don bata kwana a gidan, janyota yayi zuwa tsakiyar kafafun shi yace "that's enough madam banason kina fushi akan abinda baida wani fa ida let us be happy for ever kinsani ina bakin aiki ne nabarshi na zo saboda ke kawai I have only two days to go back don haka banason wani Abu ya gitta mana na bacin rai, sakin fuskar ta tayi ita kanta ta rasa dalilin jin bacin ran nata sosai, sakin jikinta tayi yafara feeding dinta yana ba kanshi Shima saida suka cinye tas ya tsiyayo musu lemon kwakawr yakai mata bakin ta ta kawar da mai don ta mugun koshi batason ta kara wani Abu duk da Aman nata bakoda yaushe take yinshiba sai taci Abinda bai kwanta mata ba,

Shidai yasha sosai saida suka kammala suka kwashe komai suka kai kitchen kafin suyi sallar magrib data kawo jiki, tayi matukar gajiya bacci kawai take sonyi, wayar ta ta janyo domin kiran Auntyn ta, taga miss call dinta har uku, ta kirata back, "Yasmin yaushe zaki dawo gidan ki na BARIKI you have to live here nan ne wurin Aikin mijin ki hakura zakiyi da Rayuwar wannan gidan ki dawo nan kodan kare mutuncin gidan Aurenki tareda kore duk wasu kadan garun dake neman bata miki ruwa........ 🖊️

"That is fact kowace matar soja tanada kalubale a Rayuwar ta ta BARIKI ko sharrin matan banza ko kuma sharrin shaye shaye duk macen da Allah ya kare mata mijinta a BARIKI ta

godewa Allah duk da a kowace Rayuwar Aure ba matan soja kawai ba KO civilian din akwai kalubalen don haka Allah yabamu ikon cinye jarabawo yin mu baki daya,

*Matar Soja*
[9/18, 6:30 PM] Asli Smasher 💕: (¯`*•.¸,¤°´✿.｡.:*ᵽɍօʄɨƈɨɛռȶ ԝʀɨȶɛʀֆ*.:｡.✿`°¤,¸.•*´¯)

ᴛʜɛ αвιℓιтʏ тσ gυι∂ɛ ιѕ ᴛʜɛ мσѕт ιмρσяᴛαηт qυαℓιтʏ  α ωяιтɛя cαη нανɛ, ωɛ ρяσғιcιɛηт ωяιтɛя'ѕ αѕѕσcιαтιση ωιℓℓ ѕнαяɛ тнɛѕɛ qυαℓιтιɛѕ.

INSTAGRAM: https://www.instagram.com/proficient_writers/

FACEBOOK: https://mobile.facebook.com'/groups/2455147078097572/

TWITTER: https://twitter.come m/pro__writers?s=09
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
*BARIKI*
_Auren Soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

Written by FENERH

*Dedicated to*
Fiddausi mainasara feby

53&54

Shiru tayi tareda kallon shi,  kafin tace meyake faruwa ne Aunty wani Abu ya faru ne?  "Aa kawai ki dawo nan da zama zaifi miki nidai Abinda zanfada miki  kenan,   kashe wayar tayi kawai tarasa meke faruwa da yasa Aunty maryam tace ta dawo BARIKI,  matsota yayi sosai tareda  dora hannun shi saman kirjin ta dake tsokale mai ido,  "ya akayine matar MA?  "Meyake faruwa ne a gidan ka na BARIKI?  Tafada tareda cire hannun shi a jikinta ,  d'an matsawa tayi kadan tana mai kallon tuhuma,  "oh come on baby kidaina rigimar nan haka mana kece fa matata kibarsu da da shirmen su I will handle them in my way I just  want you to believe  me, wai what is going on?  Kafada min,

"Tundazu naso inmiki magana akan zuby baki bani chance ba tun ranarda nadawo aka kirani tana son ta batamin suna a wurin aiki na last ta turomin wata da sunan tanada cikina this time A round ta dakko ciki da kanta ta dawo gidana bayan ta yi report a office din mu cewar tana dauke da ciki na nakuma koreta yanzu an bani umarnin dole in kula da ita har ta haihu, "but the truth is ba cikina bane bantaba Tarawa da kowace mace ba turmi da tabarya ni nasan ina tsayawa suyi romancing dina domin insamu relief saboda sha awar dake mun yawa Amma bantaba kusantar zina ba impact kyamar tsoma jikina nake a jikin kowace kazama, kece mace ta farko da nafara jin feelings irin haka a tareda ni tundaga ranarda na dora idanu akan ki naji a jikina you are the one for me , Yasmin ke kadai ce mace ta farko a Rayuwa ta and you are the last insha Allah, inkin lura tun ranarda na dawo ban samu kaina ba Abin ya dameni sosai ba komai nake tsoro ba sai banason Abinda zai daga miki hankali zuby ta bullo ta inda banda yanda zanyi da ita Amma nabata dama har zuwa lokacin da zata haihu muyi DNA test a lokacin zan mata nawa wulakancin,

Ajiyar zuciya ta sauke tareda shigewa jikinshi to yazatayi da kaddarar ta haka ta sameshi bata isa ta canja mai Rayuwar da yariga yayita Abaya ba dole zata taimaka ma mijinta har ya fita daga kaidin matan BARIKI, "oh baby nagode da kika fahimceni dama ina tsoron Abinda zaifaru ne nakasa miki bayani tunfarko am afraid of loosing you in my life, zame kayan jikinta yafarayi tayi saurin riko hannayen shi, ya bata fuska kamar yaro "why now? "Dazu fa munyi kuma kaga ana kiran sallah " yeah I no muje muyi sallah yau ba bacci sai kinbiya bashi Kinsan ni mayen ki ne bazan taba gajiya da keba,

A daren sai da taso guduwa domin ganin tayi ya kara like mata daya huta zai nemi kari saida tasa mishi kuka tareda pretending marar ta na ciwo ya sarara mata, washe gari basu tashiba sai karfe goma suka tashi tunda sukayi sallar Asuba kawai suka shige bargo, ita tafara tashi ta hada musu simple breakfast tareda taimakon baba jummai mai tayata aiki saida ta kammala ta nufo dakin nasu tayi wanka tareda gyara kanta ya zuba ado cikin Riga da zani na atanfa tayi matukar yin kyau saida ta feshe jikinta da kamshi kafin ta matsa kan gadon. Ta zubawa kyakkyawar fuskar shi ido ta yi murmushi tareda shafo saman kirjinshi mai daukar hankali da tafiya da hankalin mata, bai bude idanun shi ba ya Dora hannun shi a kan nata kafin ya bude idon shi ya sauke a kanta, kara ware idanun shi yayi ganin yanda tayi kyau sosai ya shafo marar ta tareda maida idon shi kan kirjinta dake kunbure har yana hango tsagun su ta sama, ya finciko ta ta fada kanshi, "a bani breakfast madam tunda antashe ni,

"Good morning tafada tana kara lafewa kan kirjin shi, "how are you? "Fine, muje Kayi wankan your break fast is ready, "noo ba wannan nake magana ba Abincin cikin zani nake magana bana kitchen ba, ido ta zaro "haba mana kusan kwana fa mukayi fa muna Abu daya, "uhm ai kece kike ja Kinsan bazan iya jin dumin jikin ki in hakuraba gashi kinzo early morning kinkuma tayar min da hankali don haka kiji dani idan kinaso intashi mu karya, so take ta zama jaruma ta

fagen bashi goyon baya a duk lokacinda ya nemeta don haka tashi kawai tayi tareda zuge zip din rigarta saida takaishi karshe kafin ta tashi tsaye,  gaba daya ya zuba mata na mujiya ya matsu bata bude mai Abin kaunar shi ba,  cikeda tsokana tafara sauke rigar daga sama tana jamai rai,  duk ya k'agu ji yake kamar ya fisgota,  saida ta cire dama batasa bra ba saboda Sam batason sawa yanzu saboda kirjinta sai ya rika yimata zafi,

Saida ta cire ta juyomai su tareda Dan juyawa saida suka motsa sannan ta daga rigar zata mayar ta juya tana shirin gudu,  saika tashi Kayi wankan zanbaka kasha Inba...  Tsit tayi jin hannayen shi duka biyu akan su ya musu wani irin salon kamunda saida ta hadiye sauran maganar ta tuni kasala ta rufeta gashi ya manna mata jikinshi tanajin yanda yake sukarta ta baya,  "kinaso ki karasa ni ne zaki jamun rai ki gudu to baki isa ba,  dagata yayi cak ya maidata gadon sannan Shima ya haye tareda maida bargo ya rufesu ruf  saida ya kuma gurzarta kamar ba gobe kafin ya sarara mata ya koma gefe yana lallashin ta "sorry baby gobe zantafi zanyi kewarki sosai,   wancan karon nikadai nasan irin wahalar da nasha don wurin ba kyaune da bazan iya tafiya inbarki ba a nan,

Juyowa tayi tareda rungume shi,  "yanzu ma bazamu kuma yin waya ba sai kadawo?  "Noo nasa an kara service a wurin kullum zamuyi waya  yanzu ai bazan iya zama Banji muryarki ba sai jini na ya hau gashi inaso inrikajin lafiyar baby na,
Ok tashi muyi wanka yunwa nakeji,  sauka   yayi bakomai a jikinshi ya dagata cak sai bathroom bajewa yayi ya bubbude a tub din yace ita zatamai wanka,  haka tafara wankeshi yana lumshe ido tareda yawo da hannun shi a ko ina najikinta,  dakyar tasamu tayi escape suka gama wankan haka suka fito yana layi domin jinshi yake kamar ma baiyi komai ba Amma yasan inyace zai kara zai cutarda babyn shi,

A dakin ta kawo musu komai  suka karya sannan  ta shirya cikin wata  shigar na purple code less mara nauyi Riga da sket ya zauna cif a jikinta    ta murza dauri  Shima ya fito cikin farin yadi mai shara shara kana hango farar singlet din shi yayi kyau yana baza kamshi,  yace ta dakko gyalenta zasuje malali sugaida hajiya,  cikin farin ciki ta ce tom tareda ciro farin mayafi da gyale harma da jaka,  ta kara fesa jikinta da turare yana tsaye ya zuba mata idanu,  wani farin ciki yakeji domin yasan yayi sa ar mata ga kyau ga kuma nasaba don ta cika mace ciki da waje,

Rikota yayi suka fito ta sallami baba jummai tace sai sundawo  cikin sabuwar motar lefen ta daya fara suka shiga yace yau ke zaki tuka mu ina gefe,, tace tom muje,  ta murza key ya zuba mata ido kamar ya cinye ta,  ta fita a gate din suka dauki titi " kaifa zaka rika nuna min hanya bansan ta ina zamu bi ba,    gyara zama yayi ya zuba mata ido tareda janye gyalen daga

kafadar ta ya mayarda hannun shi wurin da yakeso,  "ina tuki nefa karka sa in watsar da mu a titi Kasan ba wani iyawa nayi kamar kaiba,  "uhm sai mu tafi tare mu duka Kici gaba da tukin ki kawai kibarni inyi wasa da kayana,  haka yaketa motsata yana lumshe ido har suka isa Lafiya tareda taimakon shi,  katon gate din sojoin suka bude mata ta kunna kai tuni suka fara saramai ya wani hade gira bayan ya gama lalibeta a cikin mota matsowa yayi kusa da ita,

"Baby hajiya zata gane kin gama more mata yaro a mota kinga yanda nakoma,  yafada yana mai manna mata jikinshi a gefen ta,  ido ta zaro "baka gajiya ne wai kai,?  "Indai da gidan dadi ne bana yi muje ciki ma kibani gaskiya bazan iya hakuri nida Abuna ba,  "you are jocking?  "Am not,  tasan ba karamin Aikin shi bane zai aikata,  tundaga kofar main falon sukafara  jiyo hayaniyar Y'an matan na hajiya,  ya hade fuska yakara rike mata hannu gam duk da tana kokarin yasaketa,  "stay still ko indaukeki gaban hajiya  dole ta natsu,  suna jin sallamar shi suka shiga taitayin su,  gaba daya suka zubawa matar tashi ido tuni kowacce ta raina kanta, sunga kyau haduwa da kuma wayewa dole ya rika musu kallon Y'an kauye kuma munana akoda yaushe tunda yanada indiya,

Da ruwan masifa yafara "wato ku kullum kamar akuyoyi Sam bakwa girma ko,  yafada yana watsa musu mugun kallo,  itadai neman wuri tayi ta zauna bayan ta samu ya saki hannun ta, zamewa sukayi kowace ta kama gabanta shi kuwa zama yayi kamar zai shige jikinta "muje side dina mufito kafin ku gaisa da hajiya baby,  nidai bazan iya wannan Abun kunyar ba ni nasan kunya idan kasaba yi a gidan mu nan bazan yarda ba. Dariya yayi,  baby saidai kar akuma kin manta ranarda nazo na kwakuleki a gidan nan kenan,..

Kafin tayi magana suka jiyo muryar hajiya "oh ni baba na ka kawomin yata kuma kabarta a falo ka tsareta da shirmenka ko,  shagwabe wa yayi kamar karamin yaro "hajiya nace muje dakina na gaji inason tausa taki,  matsowa tayi tareda riko hannun ta tana cewa "mara kunyar banza da wofi taki taje  taso kinji mu shiga ciki y'ar Albarka kiyi hakuri kinji da halin baba na,  "kai hajiya yau ni zaki y'ar ki kama wannan ko da ban kawota ba ai,  "ai Kasan batada kafa ko batasan hanya ba,  juyowa tayi ta mai gwalo yace "lalala ni kikewa gwalo zamu hadu a gida,

"Sai inrike ta a nan dama gobe zaka koma  tashi yayi yabi bayanta, " kice zamu kwana tare kenan ba inda zanje kuwa,  saida suka shiga dakin ta ta zame kasa tafara gaisheta tayi saurin dagata tashi y'ar Albarka Allah ya miki Albarka Fatima Allah ya Albarkaci zuri arku,  ta Amsa a hankali, kanta a duke da kanta ta kawo mata kayan motsa baki Shima ya shigo,  "wai yau nine bare aka ware ni,  ka fita magana zanyi da suruka ta katafi dakin ka a gyare yake,  "bakin shi ya turo. "Kai hajiya to tazo muje mana tare,   nace ka fita ta tashi   ta raka shi tareda maida kofar ta rufe,  yayi dariya daman yasan kaunarda ke tsakanin hajiya da Yasmin tunfarko tun batasan cewa zata zamo matar shiba,

Zama tayi ta fuskance ya da kyau,  "dama naso sai yatafi insa akaini gidan naku muyi magana akan babana Fatima nasan Kinsan komai dake faruwa,  yanzu kinfini kusanci da babana kece matar shi duk yanda zakiyi a matsayin ki na matar shi ki taimaka mai Allah kuma ya raba shi da sharrin matan banza tunfarko sakacin shine,  da yasaki jiki da yarinya mara tarbiya tayi sanadin fadawar shi harka da matan banza, Nagode wa Allah ma da baya wasa da salla baya shaye shaye da illar da zata yimai ba kadan bace don malamin dake bashi taimako yafada min anyita jifarshi da sihiri Kala Kala don dai yayi riko da ibada ne Abun baiyi wani tasriri a jikinshi ba amma wannan shedaniyar yarinyar ina kan kai kukana a wurin ubangiji Allah zai mana maganin ta cikin ruwan sanyi,  kiyi hakuri haka Allah ya tsara Rayuwar shi tunfarko saidai mu tayashi da Addu a,

Shiru kawai tayi domin tanajin matukar bacin rai duk lokacinda ta tuna da Rayuwar shi ta baya wadda take kokarin taba farin cikin su a yanzu,  hajiya ta fito mata da wani Dan madai daicin galan,  ki rika shan wannan baida illa ga cikin ki Amma zakiji dadin Amfani dashi Zuma ce hadin Sudan nasa aka kawo muku keda yayyin ku ta ciro wata gumba mai kwakwa da su gyada da Aya tace kirika damawa da nono duk basuda illa kuma ko shekara zatayi bazatayi komai ba, godiya tayi. Sosai tareda jin matar ta kara shiga ranta ta diddila da murfi ta sha tareda karawa domin zumar harda dabino tanajin gardin ta sosai  ,  tace kisha a hankali saboda zaki duk da batada damuwa Amma kodan gudun tashin zuciya,

Kunya taji kadan ta rufe Domin ita dadi tayi mata kodan kwadayi zata sha ta,  ta tanbayeta ya Y'an Aikin ta sunyi?  "Eh kawai baba na ce ta tsaya kodan su gyaran gidan da girkin sojojin dake gidan  " to Aikin bazai mata yawaba ko za a karo wata tsohuwar ne inbakya ra ayin Y'an matan,  "aa itama ta isa zandauketa gobe mu koma BARIKI kafin ya dawo,  "ai ba damuwa duka gidan ki ne,    inkina bukatar wani Abu ki fada sai atanadar miki,  godiya tayi sosai tana kara godewa Allah da yabata uwar miji ta gari,  wayarta tayi kara ta daga ganin sunan shi ne yasa taki dagawa,

Saida ya kirata sau uku taki dagawa,  tana zaune tana kara kurbar zumar ta ya turo kofar tareda hade fuska,  don wulakanci bakya ganin kirana ne?  Kallon shi kawai hajiya tayi ta kada kai "Fatima tashi kije ya baki uwar da zai baki sarkin naci,  shidai juyawa yayi ta mike tareda gyara gyalenta ta nufi gefen nashi gidan ba bakonta bane don haka tasan hanyar da zata sadata da gefen shi,  batasan meke damun shi ba da ya dame ta sai tazo,  tana shiga falon taji yayi sama da ita bai direta ko inaba sai kan gadon shi ya fara haukata ta fa zafafan touch,  tareda hade bakinsu wuri daya tuni yaji gardin zumarda take sha ya mai welcome tuni yafara bata tsotso mai cikeda dokin Kasan cewa da ita,

Duk ya rura mata jiki,  haka suka farantama juna duk da kasanta na neman agajin gaggawa haka ta sake mai ya murjeta son ranshi sai la asar sukayi wanka suka fito domin tafiya,  a falon suka samesu itada Y'an matan ta,  "ai har cigiya na bayar ko kun wuce a she kuna ciki,  itadai Yasmin kunya rufeta tayi ta dukar da kanta kasa "ina hutawa ne hajiyata gobe fa zankoma yanzu ma idan na shiga gida sai gobe idan zantafi zanfito,  yafada  ko a jikin shi,  "to naji mara kunya a sauka Lafiya,  shiga daki tayi ta fito mata da zumar ta da turarukan wuta ta hado mata tabawa cikin Y'an matan suka kai musu mota,  ta rakasu da Addu a suka  tafi cikeda farin ciki,  shi ya tuka motar har suka isa gida Lafiya taso ya kaita gida yaki yace yaushe tabar gidan,  ta kuma so ya kaita BARIKI yaki yace basai tajeba ga gidan ta,  Shiru kawai tayi mai ita Kadai tasan me ta shirya bayan tafiyar shi,

A daren ji sukayi kamar kar gari ya waye saboda kar su rabu sun raya wannan daren hade da taimakon magun gunan da hajiya ta bata shi  kanshi ya haukace da jin wani sabon gardi da galmi tayi mugun laushi koda Asuba saida ya kuma lallabe ta kafin yayi wanka,  cikin kakin shi ya shirya tareda baza kamshi ya fito a sojan shi,  karfe bakwai Ahmad yazo ,  rungume shi tayi tsam taji wasu irin hawaye masu zafi nabin kuncin ta  tuni tafara jan sheshsheka ya tallsbota sosai a jikin shi,  "karki karya min guiwa madam kiyimin Addu a sannan ki kulamin da baby na please take care of your self and my baby bakuda matsalar kudi kunada komai a hannun ki inkina son Aike you can send those soldiers,  ya duka yabata kiss a cikin ta kafin ya bata  a lips dinta saida ya lashe hawayen fuskar ta tas sannan ya saketa tareda yin dariya "haba matar soja ki zama jaruma mana yanzu idan baby yazo yaga zantafi yaga Maman shi na kuka Shima kukan zaiyi kenan,

Murmushi tayi tareda cewa "kaje baban Auwal na jiranka Allah ya kare mana ku,  "Amen sweet wife Allah yasadsmu da Alkhairi,   bata iya rakashi ba saidai yana fita tasa kuka mai sauti ta koma dakin sai taji gidan ya mata mugun girma yanzu dama ganin shi tare da ita yasa Sam bata ganin girman gidan,  komawa tayi tareda kunna wayar ta tafara chart a grp domin rage zaman Kadai ci,

A haka Rayuwa taci gaba da tafiya yanzu tana samun shi akoda yaushe idan ya kirata  saidai kullum Kara tuna mata yake ta musu Addu a,  tayi matukar kewarshi Shima haka ne a gefen shi saidai aiki bazai barshi yazo ba,  a cikin wata daya duk sati suna haduwa a gidan su itada y'ar uwar ta sometimes ma tare suke zuwa gidan hajiya ta jajje gidan Y'an uwanshi dake nan kaduna suma sukanzo mata,  ga cikin ta baya bata matsala Allah ya bata ciki mai saukin gaske

Bayan wata uku itada Oga saidai waya ko video call duk lokacinda yayi video call da ita sai ya rikice mata ga cikin ta ya fara bayyana sai budewa takeyi tana Kara haskawa   batada damuwar komai saita rashin mijinta,  yau ma da sukayi waya rigima tasa mai ita dai Tanason ganin shi,  dariya yayi "madam kina tunanin kinfini damuwa ne?  Kawai ina matsewa ne ji nake ko yanzu kamar in janyoki a wayar nan inji ni a jikin ki,  kullum hadarin wurin nan karuwa yakeyi duk lokacinda muke tunanin Abin yayi sauki sai su kuma bullo mana ta wani wurin don haka ko zamu samu  shigowa sai karshen watan nan  please take care of your self and my baby kice dadyn ta na missing dinta da Maman ta,

Tarasa dalilin da take yawan jin faduwar gaba gashi ya hanata zuwa gida ko zata rage damuwar sai yawan mafarkai da kuma take yi akan mijin ta kullum sai ta kira shi taji ko Lafiya yake yace mata kalau yake tadai Kara Addu a akan Wanda sukeyi,  ganin hankalin ta bai kwanta ba Yau ta shirya ta tafi gidan hajiya tareda fada mata Abinda takeji,  "nima Fatima kullum hankali na ba akwance yake ba idan na kirashi zai ce min kalau suke ,

A gidan hajiya ta kwana a ranar don bazata iya komawa gidan ba gaskiya hajiya sai Kara kwantar  mata da hankali takeyi,   da sassafe tana zaune akan daddumar salla tana lazimi wayarta tayi Kara hajiya ce ta mika mata gashi ana kiranki,  saida gabanta ya fadi kira da sassafe waye wannan ganin bakuwar numba yasa  gabanta faduwa,  taga bakuwar numba,  dauka tayi kawai tareda hello,  "please  am I talking to Mrs Muhammad Abdullah?  Gaban ta ya mugun faduwa tareda cire wayar akunnen ta domin dagaji ba Alkhairi za a fada mata ba ta saki wayar hajiya dataga haka ta taso tareda daukar wayar jin Ana kan magana,  tuni ta sulale kasa tayi zaman yan bori,  jin salatin hajiya yasa ta dawo hankalinta,

"Ba Abinda ya sameshi ko hajiya kifadamin Lafiya lau mijina yake kifadamin ba Abinda zai faru dashi yafada min zai dawo ya gan mu nida babyn shi,  sambatu kawai take yi duk ta rude  , hajiya tace shirya muje Asibiti mijin ki na can 44 ance Y'an fashi sun kawo musu hari wasu sun mutu tashi muje inga halin da yake ciki Fatima,  ta fada jikinta na rawa....... 🖊️

*Matar Soja*
[9/20, 11:17 AM] Asli Smasher 💕: (¯`*•.¸,¤°´✿.｡.:*ᵽʀoʆɨƈɨɛռȶ ɯʀɨȶɛʀֆ*.:｡.✿`°¤,¸.•*´¯)

тнε αвιℓιтү тσ gυι∂ε ιѕ тнε мσѕт ιмρσяαηт qυαℓιтү α ωяιтεя cαη нανε, ωε ρяσғιcιεηт ωяιтεя'ѕ αѕѕσcιαтιση ωιℓℓ ѕнαяε тнεѕε qυαℓιтιεѕ.

INSTAGRAM: https://www.instagram.com/proficient_writers/

FACEBOOK: https://mobile.facebook.com'/groups/2455147078097572/

TWITTER: https://twitter.come m/pro__writers?s=09
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻
*BARIKI*
_Auren Soja_
🌻🌻🌻🌻🌻🌻🌻

Written by FENERH

*Dedicated to*
Fiddausi mainasara feby

55&56

A rude ta mike ko canja kayan baccin ma bataji zata iya yiba,  dama da katon hijabi a jikinta suka fito harabar gidan motar ts suka shiga gaba daya ta gama rudewa ga wani irin juyi da cikin ta keyi,  sai salati  kawai hajiya keyi,  ikon Allah ya kaisu Asibitin,  hajiya tace yanzu ki kira mana number Ahmad muji suna ina, ?  Anan taji hankalinta ya kuma   tashi tunawa da Ahmad da tayi yakamata a ce shiya kirata ba wani ba Allah ya rufa musu Asiri kuwa,

Tunda daga bakin gate suka fara tanbayar  sojojin da aka kawo daga birnin gwari a yau ne ko jiya?  Wani yace "oh MG Abdullah suna operation Lafiya dole word madam,  ya nuna mata wajen gaba daya basa iya cewa komai karfin hali kawai takeyi ga hajiya ma gaba daya ta gama rudewa,   a zaune suka samu Ahmad hannun shi nannade da bandages ga goshin shima da plasta  tayi saurin karasawa wurin shi jikinta na rawa,  duk ta rikice hajiya ce tafara cewa "Ahmadu ina baban nawa,?  "Mama meyasa kukazo waya fada muku?  "Wani yakirani a waya yanzu, yasmin ta bashi Amsa,  "Oga na emagency ya samu rauni sosai akai da hannu koda muka iso nan baima sani ba zasuyi mai xray kafin musan koda wani raunin,  kuka yasmin tasa mai cin zuciya tareda rungume hajiya da itama karfin hali kawai takeyi,  "meyafaru daku ne Ahmadu,?  "Wallahi mama tunfarkon watan nan sai ankawo mana hari Allah baya basu sa'a jiya

kawai sunyi Ambushed din mune amma munkashe su sosai Oga yayi kokari sosai wajen fada dasu gashi ba muda makamin da sukeda shi,  duk da yaji rauni haka yake fighting dinsu sai daga bayane ma muka gane yaji rauni bayan mun samu nasara akansu munkama wasu wasu sungudu sun kashe mana sojoji shida a ciki harda Oga umar makocina,

Wani irin kuka ta sa Mai Kara "yanzu bazamu ganshi ba?  "Sai sun kaishi resting room in sun gama dubashi,  kutaya shi da Addu a kawai mama,  "innalillahi wa inna ilaihirraji un,  hajiya keta mai maitawa,  wuri ta samu ta zauna Yasmin ma ta zauna har wani jiri takeji yana neman kadata,  yanzu shikenan baban Amla ya rasu wayyo duniya duk da batada halin da mijin nata yake cikiba Amma ta mugun tausayawa Maman Amla,  matsowa yayi yace ta aramai wayarta zai kira maryam,

Shiya fada mata halin da ake ciki tareda bata umarnin zuwa da breakfast saboda su hajiya , hankalin maryam ma yatashi ta kira su baba ta fada musu suma,  kafin kice me Asibiti ya cika taf da Y'an uwa da abokan arziki harda Y'an Uwan shi duk sunzo kowa sai Addu ar Allah yasa suga Alkhairi sukeyi,  yasmin dai tayi kuka hartaba uku lada  sai lallashin ta akeyi "kidaina kukan nan haka kinga bake Kadai bace ga tea an hada miki kisha karki fadi kijama mutane wata damuwar,

Hajiya keta lallashin ta mama ce tace barta hajiya tunda batada hankali tazama yare bazaki tayashi da Addu a ba zaki zauna kina kuka ko shine zaisa ya warke ko kuma kaddarar shi ta canja,  "bita a hankali Saude,  baba yafada yana maijin tausayin y'ar tashi,  wasa wasa har karfe goma ba su sashi a idoba ga kukan ta yaki tsayawa kowa dake wurin ita yake tausayawa domin kukanta irin mai ban tausayin nan ne,   jiya ta gama waya dashi yau akirata ya na cikin mugun hali ba Abinda take tunawa irin Alkawuran da yake mata kwanan nan "baby ina dawowa zamuje muma baby na shopping baby yafara kicking?  Kullum maganarshi kenan babyn shi da kuma kewar ta,

Shafo cikin tayi tareda runtse idanun ta tayi magana a cikin zuciyarta "insha Allahu babanka zai tashi ya zai yi wasa dakai my baby,  duk hankalin su yagama tashi ganin har shabiyu ba wani magana sai likitoci ke fita da shiga masu kaki,  sai kusan karfe daya suka kira Ahmad,  yashiga saida ya dauki lokaci ya fito ta tashi da Sauri ta nufeshi "Lafiya baban Auwal?  "Alhmdulillah kuzo keda mama ku  ganshi basa bari mutane na shiga ciki ko yanzu na rokesu ne da kyar, cikin sauri ta wuce ko hajiya bata jiraba,  saidai tundaga farkon dakin jikinta yayi mugun sanyi ganin sojoji Kala Kala a jere kowane da tashi matsalar wani ba hannu wasu ba kafafu wasu kuma bama Susan inda kansu yakeba,

Wallahi Y'an uwa duk wadda tasan 44 gefen Y'an Ify dole idan har ta taba shiga saita koka sojoji

ne daga meduguri sai ka musu kuka kaga mutum da ranshi ya rasa kafafu ko wani bangare na jikinshi saboda bautawa kasar shi wallahi kutaya sojojin mu da Addu a suna cikin hadari a Rayuwa wata ma mijinta zai mutu shekara guda bazata sani ba Wasu ko gawar su ba agani, Allah yasa mudace,

Kamar wadda kwai yafashe mata takasa karasawa wajen datake tunanin MA dinta ne akwance hannun shi a nannade ga kanshi ma haka duk fuskar shi a kunbure kamar bashiba wani irin jiri yaso yarda ita hajiya ta rikota tamau duk da batada karfi, takarasa da ita cikeda karfin hali, kuka ne ya kufce mata ta rufe bakinta domin akwance yake kamar gawa ko motsi bayayi ga oxygen a hancin shi batasan lokacin da ta sulale a sumeba, da taimakon Ahmed suka fita da ita saida aka bata gado a wani word din suka daura mata drip tareda Allurai kafin ta farfado, ta zabura ta kuma sa kuka "mama ku ciremin ruwan nan zankoma wurin shi inganshi ya farfado!?

Mama ma idanun ta sun ciko sosai don ta bata magun tausayi Aunty maryam kam saida tayi kuka ganin halin da mijin y'ar uwar tata ke ciki, "kiyi hakuri yasmin Kici wani Abu kinga kodan cikin ki likita ma fada yayi yace harda rashin cin Abincin ma ya janyo miki jiri, ki kwantar da hankalin ki da izinin ubangiji zai samu Ify, "mama bakiga halin da Muhammed ke ciki ba tafada tana wani irin kuka, kiyi hakuri kinfi mahaifiyar shi Sonshi ne ki kwantar da hankalin ki KO zata samu kwarin guiwa kina kallon tsohuwar nan akwai tawakkali da karfin imani,

Haka suketa mata Nasiha saida ruwan ya kare suka matsa mata tasha ruwan tea mai kauri saidai tana gama sha tafara kelaya Amai saboda yunwar da ta shigeta, maryam ta kuma hada mata ta sha kadan, ta mike ita dai zata koma wajen shi, sun canja mai daki saboda gudun hayaniya sunason idan ya farfado suga aikin da sukayi mai akai KO anyi nasara, dakin ta koma duk da nurses din sun so hanata ta shige tareda zama kusa dashi ta riko hannun shi mai lafiyar ta dora a saman cikinta tareda fara yimai magana a hankali, "my sugar please katashi babyn ka na son ganinka gashi yafara motsi, ina kewar ka please ka tashi bazan rika complain nagaji ba daga yau KO sau goma zakayi,

KO motsawa baiyi ba haka ta cigba da zuba mai sambatu daga karshe ta dora kanta saman hannun mai Lafiya, kallon kirjinshi fari tayi mai suma luf luf a waje ba Riga a jikinshi sai dogon wandon kaki kawai saboda kana nun ciwon dake kota ina a jikin nashi, duk da yana cikin ciwo muscle dinshi na nan sai Kara kunbura da sukayi , wata nurse ce ta matso tareda cewa "madam please karki dame shi fa bamason ana mai hayaniya,

Itadai kokarin janyo zanin rufarda ke gefen gadon takeyi ta rufemai kirjin shi don wani irin kishi takeji yanda nurse din nan ke kalle mata miji ba Riga, "noo please madam he needs a fresh air so that the wound will heal quick, anki abarshi a buden shegiya wato ta kare Mai kallo, tafada cikeda masifa itadai nurse ba Hausa bataji Ashariyarda ake lafta mata ba ta juya ta fita tana mamakin yanda Yasmin keda mugun taurin kai taki KO bari ta kula da wannan handsome guy din duk dama wai bai da Lafiya baima san me akeyiba,

Sai kusan dare mutane suka watse anyi fama da ita ta tafi KO wanka tayi taki sallah kawai take matsawa tace sai ya farfado zatayi wankan hajiya tace abarta tunda Ahmad na kusa tunda shima bawai an sallame shi bane kawai ganin ciwon ogan nashi yafi nashi dole ya mike , gadon dake gefen nashi ta kwanta wayarta ta kunna da tun zuwanta bata koma kantaba gaba daya ta kasa bacci daga karshe ma dadduma ta haye tafara nafiloli, wajen karfe shabiyu ya bude idon shi, a hankali yakebin dakin da kallo ya hangota a zaune a sallaya, motsawa yayi domin kanshi da bakinshi sunyi mai nauyi sosai,

Saurin tashi tayi ta nufi gadon da sassarfa, idon shi dake cikeda ciwo ya zuba mata domin sunyi mugun ja da Alama yanajin ciwo sosai Amma yakasa cewa komai sai ido, " baban baby kafarka Alhmdulillah tafada cikeda farin ciki ta riko hannun shi sai wani irin hawayen farin ciki ke fita " Alhmdulillah kafarka Sannu my sugar, tafada ganin yana juya kai ta zabura batareda tsoran komai ba tafita, a nan ta samu likitan dake on duty ta kirashi jikinta na rawa,

Yana zuwa ya saramai "tank God oga you are fine girgiza mai kai kawai yayi ya duba shi tareda zare mai oxygen din yace " madam congrats oga is Alright saidai raunin jikinshi da hannun shi da aka dora sai ankula kar aikin ya lalace, godiya tayimai yace zata iya bashi KO ruwan tea ne saboda yasha drugs dinshi, jikinta na rawa ta bude kayan tea da aka ajiye musu manya ta hada mai dama akwai katon plask ta zuba ruwan zafin tareda Ajiye hijabin ta domin likitan ya tafi, ido kawai yake binta dashi kayan baccin jiyane a jikinta,
Masu santsi Riga da wando dogo rigar Mai hannun shimi ce KO bra babu a juk8nta,

Da taimakon ta ta dagomai gadon ya zauna sai ido kawai yake binta dashi saida ta zauna yace "go and lock the door yafada dakyar kalmar tafito domin wani irin kishi yskeji ganin yanda yake hango kayanshi kar wani yashigo ya ganta yasan wani na kallar mai ita zai karasa shurawa for sure,

Kallon shi kawai tayi ta taka ta rufe kofar da key tabarshi a jiki tana murmushin jin dadi wato yana ciwoma halin na nan cikinta ya koma zubawa ido yana hango yanda ya tasa yayi wata

Ajiyar zuciya  ta matso tareda dago cup din ta kai bakinshi,  "spoon yace mata ta gane me yake nufi ta fara bashi a baki a hayana kare mata kallo don jiyake idan ya bude baki kamar kanshi zai cire,

Saida yasha sosai kafin ta bashi maganin ta maida gadon ya kwanta still ido kawai yake binta dashi,  sai a lokacin takejin bazata iya bacci ba wanka ba bathroom din da yake fes tashiga ta kwabe ta sirkq ruwa mai zafi sosai tayi wanka domin akwai komai sabo a ciki dakin special ne saida ta tsane jikin ta da towel kafin ta mayarda kayanta dole ta fito ya zuba mata idanun shi, "wanka yanzu da tsakar dare?  Yafada dakyar,  "um banyi wanka ba yau saboda kai,

Bai kuma cewa komai ba sai ido ta rufe mai jikinshi saboda sanyin garin har bacci ya daukeshi ta zauna tareda zuba mai ido batajin zata iya runtsawa ganin mijinta a cikin wannan hali tasan don yana jarumin namiji ne har yake iya bude baki yana mata magana tasan da Lafiya lau yake da tuni ya makale mata irin kallon da taga yake aika mata dashi,

 Saida aka kira sallar Asuba ta koma bathroom tayo Alwala ta tada nafila kafin tayi sallar Asuba, tana zaune a wurin har gari yayi haske,   bai kuma tashiba domin magun gunan akwai ma bacci da zasu taimaka mai,  karfe bakwai Asibitin ya kuma cika har da su baba yauma  mama ta kawo mata break fast din da takeso taci sosai domin hankalin ta ya kwanta tunda ya farka ta gani a daren jiya,  koda hajiya ta iso taga fuskar ta da walwala tace "Alhmdulillahi Fatima daga ganin fuskar ki babana ya farfado KO, ?  "Eh hajiya Amma kuma tunda ya koma bacci  bai tashiba kuma har yanzu tafada muryar ta na karyewa,

"Ai haka ma mungodewa Allah Fatima wasu ma ran suka rasa baki daya sai muyi mai fatan samun Lafiya kawai,  tace tom Aunty maryam ma ta iso wurin,  ta tanbayeta ya su Maman Amla ?  "Wallahi zaki tausaya mata yasmin rashin miji ba wasa ba saikin zubar mata da hawaye,  ta mugun jin tausayin ta tareda Addu ar Allah ya musu gafara,

Mama ta matsa mata ta je gida ta huta  tunda jikin da sauki kodan cikin ta,  ita kanta bacci takeji sosai don bata runtsa ba Sam jiya,  dakin ta koma ta dauki key din motar ta kafin ta matsa kusa dashi ta shafo gefen fuskar shi wurinda ba kunburi ta duka ta bashi kiss a goshi " Allah yabaka Lafiya Zuma ta,  saida ya dan motsa idonshi kafin ya ci gaba da baccin ta tafi,

Gidan ta ta koma tanayin fakin ta shiga tasamu baba jummai zaune ita Kadai tana kallo a falon, "uwar dakina Sannu da zuwa,  "yauwa baba "ya mai jiki kuma jiya mai gadinki ke fadamin Allah ya Kara tsare su ya kuma bashi Lafiya Amen tace ta wuce dakinta kai tsaye bathroom ta shiga ta yi wanka tareda watsa kayan a dustbin ta dauro towel KO mai bata tsaya shafawa ba ta fada gado,  bacci ne ya dauketa mai Lafiya,

Bata farka ba sai karfe goma sha biyu ta mike bakinta daukeda salati,  ta janyo wayarta  taga time durowa tayi  ta koma watso ruwa,  cikin sauri ta shafa mai da humrar ta mai taushin kamshi kafin  ta bude katon walldrp dinta ta ciro wata doguwar rigar voil orange mai kyalkyali taji aiki ga rigar ta mugun fito da surar kirjinta domin play ce ta kamata daga kirjinta zuwa kuguntа daga kasa ta bude sosai,  ta daura dankwali tareda dakko matching gyale light orange da takalmi ta yafa ba make up a fuskar ta KO kadan sai wet lips da powder,   tayi matukar yin kyau sannan ta dauki wayarta da jaka ta fito,  dakin da baba jummai take ta karasa

Saida ta ciro dubu goma a Jakarta ta bata  "gashi baba zankoma Asibiti don Allah ku dafa duk Abinda kuke bukata ba lallai indawo yauba ma,  "to Allah yasaka da Alkhairi uwardaki na nagode sosai,  ta juya dakinta domin tayi mantuwa brush dinta ta dauka tareda turare ta ciro wata rigar bacci da katon saabon hijab da single zani ta jefa a Jakarta sannan ta fita,  ta matsu bata ga halin da yake ciki yanzu,

Tukinta takeyi cikin natsuwa harta isa 44 bata tafi da komai ba saboda tasan Y'an uwa suna kawo Abinci ga su drink da ruwa katon katon jiya Aunty Halima ta kawo  ba Abinda babu a wurin don haka gab da  word din da yake tayi parking domin akwai gefen motoci ,  ta rufe motar ta nufi dakin cikin natsuwa,  jinmuryar su hajiya dasu yaya Halima yasa ta san cewa ya farfado kenan,  da sallama ta tura kofar ta shiga kanta akasa domin tasan idanun shi biyu karyasa tasha kunya,

Tunda ta shigo ya kafeta da ido ko kiftawa bayayi wata irin wawuyar Ajiyar ya sauke har wani irin karkace wuya yayi baida  muda su hajiya dake dakin ba don su mama tuni suntafi Aunty maryam kuwa na wurin mijinta a dakin da yake,  dagashi sai Y'an Uwan shine a dakin,  gaishe su tayi batareda tayi gigin daga kanta ta kalle shiba,  hajiya tace to Fatima tunda kindawo bari mugudu mubaki wuri Kici gaba da wannan mijin naki,  bude baki yayi yace "bayan ko kallo na ma takiyi hajiya zaku tafi kubarni da ita kuna ganin bata ko damu daniba,  "Amma dai baba na duk kokarin da yarinyar nan tayi jiya nasan bata runtsa ba kodazu saida nasa baki ta tafi gida tadan huta,

"To basai tazo ta rungume niba da tadawo kallifa inda ta wani makale,  "oh ni jikar mutum hudu Kadai kula karka fama aikin hannun ka kaji mai likita yace ko, ?  Barshi kawai hajiya yazai wani hanani yin Abinda naga dama Allah ne ya nufi zanrayu da yanzu nazama gawa don haka ku kyale shirmen likita,  su yaya Halima suka yomai ca "to kar Allah yasa ka kiyaye jikinka  zai fada maka ai shugaban marasa kunya hajiya ni natafi  kutashi mu wuce,

Itadai batace komai ba sai Addu a take karyabata kunya a gaban hajiya,  suka fita gaba

dayansu sukace sai gobe tunda Abin da sauki,  suna fita ta bisu domin rakasu ta karbi yaron hannun salma wato karamarsu saida suka tafi dukansu ta koma dakin cikeda farin ciki,  tarasa me yasa ya mata kwarjini takasa hada ido dashi Sam,  tana tura kofar yace lock it and come closer yafada kai tsaye ta dago kai ta kalleshi for the first time tunda ta shigo yanzu akwai farar singlet a jikinshi,  saidai wandon kakin ne har yanzu hannun shi na rataye da abin rataye hannu bandage din kanshi ma na nan saidai fuskar ta sauka yanzu sai dan kukkujewa da tayi a gefen, kafeta da ido yayi tareda zubawa surar jikinta ido ya kalli cikinta da ya bayyana kadan yayi murmushi,  "come let me see my baby,

